
# Mu Karanta!

## Jagoran Malamai

Aji 1

Zango na Uku

Hausa




USAID
FROM THE AMERICAN PEOPLE

NORTHERN EDUCATION INITIATIVE **PLUS**

# Mu Karanta!

## Jagoran Malamai

Aji 1

Zango na Uku

Hausa

The text and illustrations in this work are licensed under the Creative Commons Attribution 4.0 International License. To view a copy of this license, visit http://creativecommons.org/licenses/by/4.0/.

First edition, 2016

**Rights and permissions**

Under the Creative Commons Attribution license, you are free to copy, distribute, transmit and adapt the work as long as you attribute or credit the original author or illustrator. In the case of this book use the following attribution language: “This work is an adaptation of materials originally developed under the Nigeria Reading Access and Research Activity and licensed under the Creative Commons Attribution 4.0 International License. The material was developed under the USAID funded Northern Education Initiative Plus program and licensed under the Creative Commons Attribution 4.0 International License.”

# Abubuwan da Ke Ciki

**Godiya** .......... **ii**

**Waɗanda Suka Bayar da Gudunmawa** .......... **iii**

**Gabatarwa daga NERDC** .......... **iv**

**Gabatarwa daga Kwamishinonin Ilimi na Jihar Bauchi da Sokoto** .......... **v**

**Jawabi a kan Littafin** .......... **vi**

Mako Na 1 - Darasi Na 1 Zuwa Na 5 .......... 2

Mako Na 2 - Darasi Na 1 Zuwa Na 5 .......... 9

Mako Na 3 - Darasi Na 1 Zuwa Na 5 .......... 16

Mako Na 4 - Darasi Na 1 Zuwa Na 5 .......... 23

Mako Na 5 - Auna Fahimtar Ɗalibai .......... 30

Mako Na 6 - Darasi Na 1 Zuwa Na 5 .......... 32

Mako Na 7 - Darasi Na 1 Zuwa Na 5 .......... 39

Mako Na 8 - Darasi Na 1 Zuwa Na 5 .......... 46

Mako Na 9 - Darasi Na 1 Zuwa Na 5 .......... 53

Mako Na 10 - Auna Fahimtar Ɗalibai .......... 60

Mako Na 11 - Darasi Na 1 Zuwa Na 5 .......... 62

Mako Na 12 - Darasi Na 1Zuwa Na 5 .......... 69

**Jadawin Haruffan Hausa** .......... **76**

# Godiya

Godiya ta musamman ga duk waɗanda suka taimaka wa nasarar wannan aiki. Wannan littafi an rubuta shi ne don inganta karatun yara a matakin farko, kuma ya samu cikakkiyar gudunmawa daga ƙwararru da kuma Masana daban-daban a ƙarƙashin jagorancin hukumar bincike da kuma ci gaban Ilimi ta ƙasa; wato NERDC, wadda ya samu tallafi daga hukumar tallafawa da ci gaban ƙasa-da-ƙasa ta Amurka; wato USAID to hannun wannan shirin da ke da taken 'himmar ci gaban ilimi a arewacin Nijeriya' (NEIplus). Sunayen waɗanda suka ba da gudunmawa wajen tsara wannan aiki yana ƙumshe shafi guda a cikin littafin. Haka kuma, ba za a taɓa mantawa da irin gudunmawar da Farfesa Ismail Junaidu (babban sakatare a hukumar NERDC) ya bayar ba, wajen ganin wannan aiki ya kammala tun daga farkonsa har zuwa ƙarshensa. Haka kuma Hajiya Nafisa Ado ta USAID, ta taimaka wajen ba da shawarwari kan irin al- ƙiblar da ya kamata abi don ganin samun wannan nasarar. Dr. Fathi El Ashry, da Dr. Lynn Evans da kuma Mary Sugrue sun ba da gagarumar gudunmawa ta ilimi kan yadda aikin ya kamata ya kasance. Masana irin su Alison Pflepson da Drake Warrick sun ba da ta su gudummawar musamman kasancewar sun yi aikin RARA a jihohin da ake aiwatar da wannan aikin.

Ba za mu manta ba da Godwin Ondoma da John Mutum, waɗanda su suka tsara dukkan hotuna da zane-zane dake ƙumshe a cikin wannan littafin don cimma wannan buri.

# Waɗanda Suka Ba da Gudunmawa

| Sunaye | Ma'aikata |
|---|---|
| Ahmad Alhaji Umar | Northern Education Initiative Plus, Bauchi |
| Amina Ibraheem Abubakar | Abubakar Tatari Ali Polytechnic, Bauchi |
| Bala Yusuf Waziri | College of Education Azare |
| Bilyaminu Bello Inuwa | Northern Education Initiative Plus, Abuja |
| Dahiru Yalwa Muhammed | College of Education Azare |
| Dr. Balarabe Abudullahi | Ahmadu Bello University, Zaria. |
| Garba D. Gandu | Nigerian Educational Research and Development Council (NERDC) |
| Hadiza Alkasim Sidi | Abubakar Tatari Ali Polytechnic, Bauchi |
| Hadiza Salihu Koko | Shehu Shagari College of Education, Sokoto |
| Lawali Ibrahim | State Universal Basic Education Board, Sokoto |
| Muazu Mustapha | Hausa Writer and Consultant Bakori, Katsina |
| Muhammed Bello Yusuf | Northern Education Initiative Plus, Sokoto |
| Nafisa Ado | USAID/Nigeria |
| Prof. Salisu Ahmed Yakasai | Usman Danfodio University, Sokoto |
| Prof. Lawan Danladi | Bayero University Kano |
| Yahaya Abbas | Yusuf Bala Usman College of Legal and General Studies Daura Katsina State |
| Zahrau Abubakar Maishanu | Northern Education Initiative Plus, Sokoto |
| Zaliha Nasiruddeen Bello | Sokoto State University |

# Gabatarwa

Kwarewa da karatu abu ne mai muhimmanci wajen ilimantar da yara a Nijeriya.  Bisa wannan tafarkin ne Hukumar Bincike da Bunƙasa Ilimi ta Nijeriya (NERDC) bisa ikon da take da shi game da Haɓaka harshe da cigaban ilimi, ta haɗa gwiwa da Shirin Ilimi na NEI Plus domin a samar da Littattafan Karatu a Matakin Farko. An samar da waɗannan littattafan ne bisa tsarin ƙumshiya da daidaituwar dabarun  Karatu a Matakin Farko.

An ƙarfafa tsari da dabarun Karatu a Matakin Farko ta hanyar rubuta littafin 'Mu Karanta' wanda ya haɗa da Littafin Ɗalibai aji 1- 3 da kuma Jagoran Malamai aji 1- 3.  Wannan shi ne abu mafi muhimmanci da ya shafi rayuwar yara a Nijeriya, musamman jihohin da wannan shirin ya shafa, saboda ƙwarewa da karatu yana da matuƙar tasiri ba kawai wajen naƙaltar harshe ba, har ma da bunƙasa ilimi.   Littattafan 'Mu Karanta' na ɗalibai da jagoran malamai an samar da su ne bisa dabarun karatu kamar haka:

- **Sanayyar Sauti**
- **Tsarin sauti/haruffa**
- **Gaɓar kalma/kalma**
- **Kwarewa da naƙaltar karatu**
- **Auna fahimta**
- **Dabarun ɗab'i da Zubin rubutu**

An ba wa ɗalibai damar amfani da darussan da suka koya, da kwatanta aiwatar da dabarun da suka koya.

Haka kuma Littattafan Karatu a Matakin Farko suna bayar da damar bitar darussa a kullum ko a mako-mako.

Littattafan suna ba wa yara damar gwaji da yin karatu matuƙa, wanda wannan yana ƙara ƙarfafashi wajen ƙwarewa da naƙaltar karatu wanda kuma wannan zai sa yara su gina ɗabi'un karatu nagari.

Ina mai matuƙar farin cikin miƙa ɗimbin godiya ga Shirin nan na bunƙasa ilimi a arewacin Najeriya (Northern Education Initiative Plus) saboda kawo wannan sabon yunƙuri tare da gode wa Hukumar USAID wadda ta bayar da taimakon kuɗi da tallafin aiki.

Ina godiya matuƙa ga manyan masana game da aiki tukuru mai inganci.

Bisa kyakkyawan sakamakon da muke fata, Hukumar NERDC ta na mai matuƙar farin cikin gabatar da waɗannan littattafan ga ɗalibai da malamai da sauran jami'ai na Jihohin Bauchi da Sokoto.  Muna da ƙarfin gwiwa cewa ta wannan littattafan za a sami kyakkyawan sauyi wajen bunƙasa ilimin yara.

**Prof. Ismail Junaidu**

Babban Sakataren Gudanarwa

Hukumar Bincike da Bunƙasa Ilimi ta Nijeriya

(NERDC)

# Gabatarwa daga Kwamishinonin Ilimi na Jihar Bauchi da Sokoto


Sanin kowa ne cewa ilimi shi ne ginshiƙin cigaban kowace al'umma. Matuƙar yara ba su iya karatu da rubutu ba, to kuwa babu wata nasara da za a samu ta fuskar ilimi. Shi kuma iya karatu ba daga sama ake samunsa ba, ba kuma tsintarsa ake yi ba. Yara suna koyon karatu ne idan an bi wata tsararriyar hanya da wasu suka sadaukar da kai domin tabbatar da ita, sannan kuma iyaye da sauran jama'ar gida suke bayar da tasu gudunmawar. Binciken da aka gudanar kwana nan a kan iya karatun yara da ke azuzuwa biyu da uku ya tabbatar da cewa, yara ƙalilan ne suka iya karatun Hausa a matakan farko na ilimi. Muna sane da cewa akwai buƙatar jihohinmu su ɗauki matakan inganta ƙwarewar malamanmu cikin gaggawa, yadda za su iya gabatar da darussan koyon karatu a wannan mataki mai muhimmanci a rayuwarsu ta neman ilimi. Saboda haka, muna godiya ga hukumar haɓaka ƙasa da ƙasa ta Amurka (USAID) da Jihohinmu saboda haɗa kai da suka yi da tsarin "NEIPlus" domin samar da waɗannan litattafai masu matuƙar inganci da nufin ƙaddamar da shirin nan na 'Mu karanta!' a dukkan makarantunmu na firamare. Wannan shiri ya zamo tamkar karaya a kan gaɓa, saboda haka yana da cikakken goyon bayanmu. An tsara wannan shiri na 'Mu Karanta!' a kan dabarun koyarwa na zamani da duniya ta aminta da shi. Kuma ya haɗa ƙwararru da muke da su daga jihohi da kuma ƙasa baki ɗaya a fannin ilimi da harshen Turanci da kuma Hausa, sun kuma sanya wa tsarin albarka.

Malami su ne ƙashin bayan nasarar da ake son samu a wannan shirin na 'Mu Karanta!'. Malamai su ne za su koyar da waɗannan darussan, don haka ya zama tilas a kan duk masu ruwa da tsaki a kan sha'anin ilimi, su tabbatar cewa malaman firamare sun sami dukkan goyon bayan da suke buƙata don su taimaki yaranmu yadda za su iya karatu. Malamai su riƙa ba wa yara ayyukan da za su yi idan sun koma gida don ci gaba da koyon karatu. A nan ya kamata iyaye su taimaka wa waɗannan yaran a ko da yaushe, don ganin yaran sun koyi karatu. Haka kuma ya kamata su tabbatar yaran sun je makaranta a kan lokaci kuma kullum yadda son iya karatu zai ƙara shiga ransu.

A matakin jihohi kuma, za mu ga cewa mun tallafa wajen haɓaka ƙwarewar malamanmu a kan sana'arsu ta koyarwa. Za mu tabbatar da samar wa makarantu da kayan aiki, sannan mu gabatar da ayyukan da za su taimaka wajen cim ma nasarar wannan shiri. Ya zamo tilas ga kowane mai ruwa da tsaki a sha'anin ilimi da ya yi duk abin da zai iya wajen dawo da tushen martabar tsarin iliminmu. A nan ana jan hankalin malamai da su tabbatar sun yi amfani da waɗannan litattafai ta hanyar da ta dace, yadda yara za su amfana sosai a makarantanmu. Muna da cikakken ƙwarin gwiwa cewa wannan yunƙuri zai taimaka wa yaranmu da al'ummarmu da jihohinmu da kuma ƙasarmu baki ɗaya.



**Eng. Nuhu Gidado**
Mai Girma Mataimakin Gwamna kuma
Kwamishinan Ilimi Na Jihar Bauchi.



**Dr. Muhammad Jabbi Kilgori**
Mai Girma Kwamishinan Ilimi
Na Jihar Sokoto.

# Jawabi a kan Littafin

Wannan littafin an rubuta shi ne domin ya samar wa yara a ƙananan azuzuwan firamare ingantattun hanyoyin iya karatu da ake bukata a shekaru uku na farkon firamare. Binciken da aka gudanar kwananan a arewacin Nijeriya ya nuna yara a makarantun firamare kadan ne kan iya karatu a harshen da aka haifesu da shi. Masana masu bincike a duniya sun tabbatar da ce wa idan yara suka iya karatu da harshen da ake amfani da shi yau da kullum a azazuwan farko na firamare, za su yi nasara a harkar karatunsu. Matakan koyon karatu da suka sani a Matakin farko na illimi, sukan maida shi zuwa wasu harsuna, a yayin da yaran suke girma kuma, wannan yakan taimaka masu a wasu darussan daban wadda ke nuna muhimmancin karatu.

Shi wannan Littafin karatun Ɗalibai, an gina shi ne a kan jigogi guda uku; Gida da Al'umma, da Makaranta. Wannan zai taimaka wa yara su koyi karatun Hausa da kuma Turunci, tare da sanin bayanin muhimmancin abubuwa na rayuwa da suka saba da shi. Littafin ya ƙumshi darussa hudu a kowace sati, sa'annan akwai darasi ɗaya akan waiwaye da gyara a rana na biyar, haka tsarin yake. Amma a sati na biyar, akan maida hankali ne kan 'yar ƙaramar gwaji wa kowani yaro, wajen ganin cewa ƙwazonsa na tafiya tare da 'yan uwansa, za a yi ƙoƙarin tafiya da duka wadda aka bari a baya. An shirya darussan, ta yin amfani da baƙaƙen Hausa. An fara amfani da baƙaƙen da aka fi amfani da su ne wadda bincike ya tabbatar. Darasi na ɗaya za a maimaita shi a darasi na biyu. Za a koyar da baƙaƙe da sautukansu tare da gaɓoɓinsu. Sannan, za a yi amfani da baƙaƙen wajen gina kalma da kuma jimla. Haka kuma, za a rubuta gajeren labari da wannan baƙaƙe. Kuma za a karanta 'yar labari wa ɗalibai a kowace darasi. Domin cigaba da koyon karatu, baƙaƙen da aka koyar a darasi na ɗaya da na biyu, su za a nanata a darasi na uku da na huɗu. A rana na biyar malami zai yi aikin waiwaye da gyara ta hanyar yin 'yar gwaji wa wasu zaɓaɓɓun ɗalibai kaɗai. Sakamakon wannan gwaji zai ba da dama wa malami ya san wurin da dalibansa suke buƙatar tallafi da kuma damar sanin irin ayyukar da zasu yi domin su ƙware, kafin su wuce zuwa darasin sati na gaba.

Nasarar wannan shiri ya rataya ne a wuyar malami, ta hanyar amfani da ƙwazonsa da juriya, zai sa ɗalibai samun nasarar iya karatu. Har ila yau malami yana buƙatar goyon baya da haɗin kan iyaye da al'umma domin a sami biyan buƙata. Don samun wannan nasara, ya zamo dole a bawa kowane ɗalibi littafin karatunsa, ba wai a kulle su a ajiye ba. Sa'anan dole kowani ɗalibi ya tafi da littafinsa gida bayan an tashi a makaranta. A can gida kuwa, ana sa ran iyaye za su taimaka wa yara da aikin gida; su saurari ya'yansu su masu karatu, kuma su gaya masu labarai da suka koya a makaranta a kowace rana. Haka kuma za su taimaka masu wajen koyon rubutu. Sa'anan akwai wani wuri da aka tanada a cikin littafin ɗalibai, inda iyaye za su sa hannu ko wace rana. Wadda ke nuna cewa sun tallafa wa yaransu a karatun da suke yi a kowani rana.

Wannan littafi an rubuta shi da burin kowa zai ba da na shi/ko nata irin gudumawar wajen tabbatar da yara sun iya karatu a azuzuwan farko. Malamai da shugabannin makarantu su tabbatar kowane yaro da yarinya sun samu littafin karatun **KYAUTA** ba tare da sun biya ko sisi ba.




# Zango Na 3
# Mako Na 1 — 12

## Alamomi

| | |
|---|---|
| M | **Aikin Malami/Malama:**<br>A nan malami/malama zai/za ta yi aiki shi/ita kaɗai yayin da ɗalibai ke koyon aikin ta hanyar kallo da sauraron aikin da malami/malama yake/take yi. |
| MƊ | **Aikin Malami/Malama da Ɗalibai:**<br>A nan malami/malama zai/za ta yi aiki sa'annan ɗalibai su gwada yin aikin da malamin/malamar ya/ta gama aikatawa. |
| Ɗ | **Aikin Ɗalibai:**<br>A nan ɗalibai kaɗai za su gwada yin aiki, yayin da malami/malama ke jagorantarsu. |
| ■ | **Alamar Akwati:**<br>An danganta sashen **'Sunayen Haruffa da Sautukansu'** da wannan alamar ta akwati. A nan malami/malama zai/za ta jagoranci ɗalibai zuwa ga sashen ta hanyar jan hankalinsu zuwa ga alamar akwati da ke cikin Littafin Karatun Ɗalibai. |
| ● | **Alamar Da'ira:**<br>An danganta sashen **'Gano Gaɓar Kalma'** da wannan alamar ta da'ira. A nan malami/malama zai/za ta jagoranci ɗalibai zuwa ga sashen ta hanyar jan hankalinsu zuwa ga alamar da'ira da ke cikin Littafin Karatun Ɗalibai. |
| ♥ | **Alamar Zuciya:**<br>An danganta sashen **'Kalmomin da za a karanta'** da wannan alamar ta dala. A nan malami/malama zai/za ta jagoranci ɗalibai zuwa ga sashen ta hanyar jan hankalinsu zuwa ga alamar dala da ke cikin Littafin Karatun Ɗalibai. |
| ★ | **Alamar Tauraro:**<br>An danganta sashen **'Karatun Jimla'** da wannan alamar ta tauraro. A nan malami/malama zai/za ta jagoranci ɗalibai zuwa ga sashen ta hanyar jan hankalinsu zuwa ga alamar tauraro da ke cikin Littafin Karatun Ɗalibai. |
| ⏰ | **Alamar Agogo:** Wannan alamar na nuna wa malami/malama lokacin da zai/za ta ɗauka domin karantar da sashe. |

## Waƙa ⏰ minti 5

Waƙar da za a gabatar.

**<u>Waƙar `Yan Kwalisa</u>**

**`Yan yara ku bar ƙazanta,**
**Ku yi aski ku yanke farce,**
**Kwaskwas ko ƙwalƙwali ku gyara,**
**Sai ku zamto masu tsafta,**
**Sai ku zamto `yan ƙwalisa X 2**

M 1. Rera waƙar sau biyu, tare da kwaikwayon abin da ake faɗa a cikin waƙar.

MƊ 2. Maimaita mataki na ɗaya (1) tare da ɗalibai.

Ɗ 3. Umurci ɗalibai da su rera waƙar tare da kwaikwayon abin da ake faɗa a cikin waƙar.

## Amon sautin gaɓa ⏰ minti 3

Kalmomin da za a tafa gaɓoɓinsu: **[ƙuruciya, ƙwarai, baƙunci, maƙwabtaka]**

M 1. Ka/ki ce: **[ƙuruciya]**. Idan akwai hoton kalmar ɗalibai su nuna a littafinsu.

2. Maimaita furta kalmar **[ƙuruciya]** tare da tafa amon sautin kowace gaɓa.

3. Nuna yawan gaɓoɓin kalmar da yatsun hannu.

MƊ 4. Maimaita mataki na biyu da na uku (2-3) tare da ɗalibai.

Ɗ 5. Umurci ɗalibai da su furta, su tafa, sannan su nuna yawan gaɓoɓin da ke cikin sauran kalmomin **[ƙwarai, baƙunci, maƙwabtaka]**.

## Bambance Sautukan Gaɓoɓi ⏰ minti 3

Gaɓar da za a bambance: **[ƙa, ƙwa]**

Kalmomin da za a bambance: **[ƙusa, keke, ƙosai, ƙwarya, jirgi]**

M 1. Ka/ki ce: Ina so a ɗaga babban yatsa sama 👍 idan aka ji sautin gaɓar **[ƙa ko ƙwa]** a cikin kalmomin da zan faɗa. Idan kuma ba a ji sautin gaɓar **[ƙa ko ƙwa]** ba sai a yi ƙasa da babban yatsa. 👎

2. Ka/ki ce: Misali **[ƙosai]**. 👍

MƊ 3. Ka/ki ce: **[keke]** 👎

4. Ka/ki ce: To mu fara **[ƙosai]** 👍 (A jagoranci ɗalibai da su ɗaga babban yatsa sama).

5. Ka/ki ce: **[keke]** 👎 (A jagoranci ɗalibai da su yi ƙasa da babban yatsansu).

Ɗ 6. Ɗalibai su ɗaga babban yatsansu sama ko ƙasa yayin da kake/kike furta kalmomin **[girki, makaranta, gida, fulawa, girbi]**.


Mako Na 1 Darasi Na 1 da Na 2

Baba yana tuƙa mota.
Motar Baba ta yi ƙura sosai.
An cika motar Baba da kayan lambu.
Cikin motar Baba akwai ƙwai da yawa.
Kusa ta fasa tayar motar Baba.

2

## Sunayen Haruffa ⏰ minti 5

Haruffan wannan darasi: **[Ƙ ƙ, Kw ƙw]**

M 1. Rubuta harafin **[Ƙ ƙ]** a kan allo.

2. Nuna harafin **[Ƙ ƙ]** ka/ki faɗi sunansa sau uku.

MƊ 3. Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashe mai alamar akwati.

4. Maimaita mataki na biyu (2) tare da umurtar ɗalibai da su nuna harafin a cikin littafinsu.

Ɗ 5. Umurci rukunan ɗalibai daban-daban da su karanta tare da nuna harafin **[Ƙ ƙ]** a cikin littafinsu.

M MƊ Ɗ 6. Maimaita matakin farko zuwa na biyar (1-5) da ɗaya harafin **[Kw ƙw]**.

MƊ 7. Umurci ɗalibai da su nuna harafin da za ka/ki furta a cikin littafinsu. (Yi ta furta haruffan **[Ƙ, Kw]** kana/kina sassauya su).

## Fahimtar Gaɓar Kalma ⏰ minti 5

Gaɓoɓin da za a karanta: **[ƙa, ƙu, ƙwai]**

M 1. Rubuta gaɓar **[ƙa]** a kan allo.

2. Nuna kowane harafi tare da furta sunansa.

3. Aza yatsa a ƙasan gaɓar ka/ki bi ta daga hagu zuwa dama kana/kina karanta ta.

MƊ 4. Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashe mai alamar da'ira.

5. Maimaita mataki na biyu da na uku (2-3) ta hanyar amfani da littafin ɗalibai.

Ɗ 6. Umurci ɗalibai da su karanta tare da nuna gaɓar kalmar **[ƙa]** a cikin littafinsu.

M MƊ Ɗ 7. Maimaita matakin farko zuwa na shida (1-6) da sauran gaɓoɓin kalma **[ƙu, ƙwa]**.

## ♥ Fahimtar Kalmomi ⏰ minti 5

Kalmomin da za a karanta: **[ƙura, tuƙa, ƙwai]**

(M) 1. Rubuta kalmar **[ƙura]** a kan allo.

2. Nuna kowace gaɓa **[ƙu/ra]** cikin kalmar kana/kina karantawa a hankali.

3. Aza yatsa a ƙasan kalma **[ƙura]** ka/ki karanta ta daga hagu zuwa dama da hanzari.

(M'D) 4. Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashe mai alamar zuciya.

5. Maimaita mataki na biyu da na uku (2-3) ta hanyar amfani da littafin ɗalibai.

(D) 6. Umurci ɗalibai da su karanta tare da nuna kalmar **[ƙura]** a cikin littafinsu.

(M) (M'D) (D) 7. Maimaita matakin farko zuwa na shida (1-6) da sauran kalmomin **[tuƙa, ƙwai]**.

## ★ Karatun Jimla ⏰ minti 5

(M) 1. Rubuta jimlar **[Cikin motar Baba <u>akwai</u> ƙwai da yawa.]** a kan allo.

2. Karanta jimlar tare da aza yatsa a ƙasan kowace kalma, yayin karantawa.

3. Koya wa ɗalibai ma'anar kalmar **[<u>akwai</u>]** kamar yadda ta zo a cikin jimlar, ta hanyar amfani da sassan jiki, ko hotuna, ko wata hanya da za su fahimta.

(M'D) 4. Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashe mai alamar tauraro.

5. Maimaita mataki na biyu (2) tare da ɗalibai ta hanyar amfani da littafin ɗalibai.

6. Tambayi ɗalibai ma'anar kalmar **[<u>akwai</u>]**, sannan a sake yi musu bayani idan har ba su ba da amsa ba.

(D) 7. Umurci ɗalibai da su karanta jimlar yayin da suke nuna kalmomin da suke karantawa a littafinsu.

8. Tambayi ɗalibai ma'anar kalmar **[<u>akwai</u>]**.

## Karatun Labari ⏰ minti 15

(M) 1. Jagoranci ɗalibai su gano sunayen abubuwan da ke cikin hoton littafinsu. A tambaye su abin da suke tsammani zai faru dangane da hotunan.

2. Rubuta labarin a kan allo.

**Baba yana tuƙa mota.**

**Motar Baba ta yi ƙura sosai.**


**An cika motar Baba da kayan lambu.**

**Cikin motar Baba <u>akwai</u> ƙwai da yawa.**

**Kusa ta fasa tayar motar Baba.**

3. Karanta labarin, kana/kina bi da yatsa a ƙasan kowace kalma.

4. Koya wa ɗalibai ma'anar kalmomi **[kayan lambu, ƙura, tuƙa]** kamar yadda suka zo a cikin


Mako Na 1 Darasi Na 1 da Na 2

■ K ƙ Kw ƙw

● ƙu ƙa ƙwai

♥ ƙura tuƙa ƙwai

★ Cikin motar Baba akwai ƙwai da yawa.

ƙura ƙura
tuƙa tuƙa
ƙwai ƙwai

ƙura ƙura
tuƙa tuƙa
ƙwai ƙwai

3

labarin, ta hanyar amfani da sassan jiki, ko hotuna, ko wata hanya da za su fahimta.

(M'D) 5. Maimaita mataki na uku (3) tare da umurtar ɗalibai da su nuna kalmomin a cikin littafinsu yayin da suke karantawa.

6. Tambayi ɗalibai ma'anar kalmomin **[kayan lambu, ƙura, tuƙa]**, sannan a sake yi musu bayani idan har ba su ba da amsa ba.

(D) 7. Umurci ɗalibai da su nuna kalmomin a cikin littafinsu yayin da suke karanta labarin a bayyane. A tabbatar suna karatun tare. Zagaya don taimaka wa ɗaliban da ke da buƙata a lokacin da suke karatun.

8. Tambayi ɗalibai ma'anar kalmomin **[kayan lambu, ƙura, tuƙa]**.

(M) 9. Auna fahimtar ɗalibai dangane da labarin, ta hanyar tambayoyi.

Umurci ɗalibai da su yi tunanin labarin da aka karanto kafin su ɗaga hannu.

**Tambayoyi**

1. **Me aka cika a motar Baba?**
2. **Me ya fasa tayar motar Baba?**

## Karatun Labari a Bayyane ⏰ minti 5

(M) 1. Karanta kan labari ***[Zaki Sarkin Dawa (1)]***

2. Nuna hoto idan akwai shi.

3. Tambayi ɗalibai su yi hasashen abin da suke ganin zai faru a labarin.

4. Koyar da ma'anar sabbin kalmomi ***[karaga, bambanci, aminci]*** ta hanyar amfani da sassan jiki, ko hotuna, ko wata hanya da za su fahimta.

5. Umurci ɗalibai su gano kalmomin nan a lokacin da kake/kike karanta labarin, ta hanyar ɗaga babban yatsa sama a duk lokacin da suka ji an faɗi kalmomin.

6. Karanta labarin ta yadda zai jawo hankalin ɗalibai.

*Wata rana dabbobi suka zabi sabon sarki zaki. Yana hawa* ***<u>karagar</u>*** *mulki, ya sa aka tara su . Ya ce, 'mu `yan`uwan juna ne. Babu*

***bambanci*** *tsakaninmu. Daga yau ka da wata dabba ta ƙara kashe `yar uwarta'. Kafin ya ƙare jawabinsa, mafiyawansu hawaye ne a idanunsu. Duniya ta dawo sabuwa a dajin nan. Kare da kura sai su kwana wuri guda, ba matsala. Damisa da barewa su zauna su yi hira. Aka zauna cikin* ***aminci*** *da zaman lafiya. Babu wata dabba da ke taɓa wata dabba `yar`uwarta da mugun nufi. Adalci ya bazu cikin dajin. Suna ta noma abinsu.*

7. Tambayi ɗalibai su koma kan hasashensu.
8. Yi wa ɗalibai tambayoyin da ke ƙasan labarin.

**Tambayoyi**

1. **Su wa sarki ya sa aka tara masa?**
2. **Su wa ke yin noma?**

## Rubutu


minti 19

Kalmomin da za a rubuta: **[ƙura, tuƙa, ƙwai]**

M 1. Rubuta **[ƙura]** a kan allo, a hankali tare da bayanin yadda kake/kike rubutun.

MƊ 2. Umurci ɗalibai da su tusa **[ƙura]** da ke da ɗigo-ɗigo a littafinsu na karatu, yayin da kai/ke ma kake/kike tusawa a kan allo.

Ɗ 3. Umurci ɗalibai da su tusa [ƙura] da ke da ɗigo-ɗigo, sannan su rubuta **[ƙura]** a filin da aka tanada a littafinsu don rubutu a ɓangaren dama.




4. A duba yanayin zamansu, da yanayin riƙon fensiri da inda suke fara rubutun da kuma yadda suke rubutun.

M MƊ Ɗ 5. Maimaita matakin farko zuwa na huɗu (1-4) da sauran kalmomin **[tuƙa, ƙwai]**.

## Aikin Gida

1. Tuna wa ɗalibai su karanta darasin yau tare da iyayensu ko 'yan'uwa ko abokai.
2. Tuna wa ɗalibai su gwada rubutun da aka yi a aji a sashen da aka tanadar don yin hakan a littafansu.

## Matashiya a Kan Darasi Na 2

1. Tuna wa ɗalibai cewa za a maimaita darasin da ya gabata.
2. A sashen rubutu, a umurci ɗalibai daban-daban da su gano abinda ke cikin hoton da ke sashen rubutu a cikin littattafansu. Ka/ki karanta jimlar **[Kusa ta fasa taya.]**, sannan a gabatar da mataki na biyu zuwa na huɗu (2-4) na sashen rubutu da jimlar.
3. A yi amfani da wannan labarin da tambayoyinsa a sashen Karatun Labari a Bayyane:

### *Zaki Sarkin Dawa (2)*

*Wata shekara aka* ***jarabce*** *su da* ***fari****. Duk abin da suka shuka ya ƙone. Sarki ya sa aka buɗe rumbunansa, aka yi ta bayar wa ga talakawa, har sai da abinci ya ƙare. Sarki ya shiga cikin damuwa. Damuwar kuma ta haifar masa da rashin lafiya. Rannan da ya kwanta, kafin gari ya waye ya rasu. Dabbobi suka zauna cikin* ***juyayi****. Ana cikin haka sai ga ruwa ya sauka. Idan aka shuka masara sai ta fito, ta girma har a girbe cikin mako guda. Haka suka ci gaba da rayuwa cikin ni`ima, kodayaushe suna tuna sarkinsu.*

***Tambayoyi***

*1. Wa ya sa aka buɗe rumbunansa?*
*2. Me ya haifar wa sarki da rashin lafiya?*
*3. Me ya sa kodayaushe suke tuna sarkinsu?*

## Waƙa — minti 5

Waƙar da za a gabatar.

**Waƙar Yan Kwalisa**

**`Yan yara ku bar ƙazanta,**
**Ku yi aski ku yanke farce,**
**Kwaskwas ko ƙwalƙwali ku gyara,**
**Sai ku zamto masu tsafta,**
**Sai ku zamto `yan ƙwalisa X 2**

M 1. Rera waƙar sau biyu, tare da kwaikwayon abin da ake faɗa a cikin waƙar.

MƊ 2. Maimaita mataki na ɗaya (1) tare da ɗalibai.

Ɗ 3. Umurci ɗalibai da su rera waƙar tare da kwaikwayon abin da ake faɗa a cikin waƙar.

## Amon sautin gaɓa — minti 3

Kalmomin da za a bambance: **[kura, ƙwai, ƙurji, ƙwarewa]**

M 1. Ka/ki ce: **[kura]**. Idan akwai hoton kalmar ɗalibai su nuna a littafinsu.

2. Maimaita furta kalmar **[kura]** tare da tafa amon sautin kowace gaɓa.

3. Nuna yawan gaɓoɓin kalmar da yatsun hannu.

MƊ 4. Maimaita mataki na biyu da na uku (2-3) tare da ɗalibai.

Ɗ 5. Umurci ɗalibai da su furta, su tafa, sannan su nuna yawan gaɓoɓin da ke cikin sauran kalmomin **[kwai, ƙurji, ƙwarewa**].

## Bambance Sautukan Gaɓoɓi — minti 3

Gaɓoɓin da za a bambance: **[ƙa, ƙwa]**

Kalmomin da za a bambance: **[gona, ƙwai, ƙwari, tuƙa, hanya]**

M 1. Ka/ki ce: Ina so a ɗaga babban yatsa sama 👍 idan aka ji sautin gaɓar **[ƙa ko ƙwa]** a cikin kalmomin da zan faɗa. Idan kuma ba a ji sautin gaɓar **[ƙa ko ƙwa]** ba sai a yi ƙasa da babban yatsa 👎.

2. Ka/ki ce: Misali **[ƙwari]**.👍

3. Ka/ki ce: **[hanya]** 👎

MƊ 4. Ka/ki ce: To mu fara **[ƙwari]** 👍 (A jagoranci ɗalibai da su ɗaga babban yatsa sama).

5. Ka/ki ce: **[hanya]** 👎 (A jagoranci ɗalibai da su yi ƙasa da babban yatsansu).

Ɗ 6. Ɗalibai su ɗaga babban yatsansu sama ko ƙasa yayin da kake/kike furta kalmomin **[gona, ƙwai, ƙwari, tuƙa, hanya.**


Mako Na 1 Darasi Na 3 da Na 4

Sabuwar ƙwarya cike da ƙwai.
Kwarya kuwa ta cika ƙwarai.
Nana na ɗauke da ƙwaryar ƙwai.
Ta haɗu da Amina ɗauke da ƙwaƙwaƙwa.
Za su kai ƙwai da ƙwaƙwaƙwa a maƙwabta.

6

## Sunayen Haruffa — minti 5

Haruffan wannan darasi: **[Ƙ ƙ, Kw ƙw]**

M 1. Rubuta harafin **[Ƙ ƙ]** a kan allo.

2. Nuna harafin **[Ƙ ƙ]** ka/ki faɗi sunansa sau uku.

MƊ 3. Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashe mai alamar akwati.

4. Maimaita mataki na biyu (2) tare da umurtar ɗalibai da su nuna harafin a cikin littafinsu.

Ɗ 5. Umurci rukunan ɗalibai daban-daban da su karanta tare da nuna harafin **[Ƙ ƙ]** a cikin littafinsu.

M MƊ Ɗ 6. Maimaita matakin farko zuwa na biyar (1-5) da ɗaya harafin **[Kw ƙw]**.

MƊ 7. Umurci ɗalibai da su nuna harafin da za ka/ki furta a cikin littafansu. (Yi ta furta haruffan **[Ƙ, Kw]** kana/kina sassauyasu).

## Fahimtar Gaɓar Kalma — minti 5

Gaɓoɓin da za a karanta: **[kwa, ƙwar, ƙi]**

M 1. Rubuta gaɓar **[ƙwa]** a kan allo.

2. Nuna kowane harafi tare da furta sunansa.

3. Aza yatsa a ƙasan gaɓar ka/ki bi ta daga hagu zuwa dama kana/kina karanta ta.

MƊ 4. Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashe mai alamar da'ira.

5. Maimaita mataki na biyu da na uku (2-3) ta hanyar amfani da littafin ɗalibai.

Ɗ 6. Umurci ɗalibai da su karanta tare da nuna gaɓar kalmar **[ƙwa]** a cikin littafinsu.

M MƊ Ɗ 7. Maimaita matakin farko zuwa na shida (1-6) da sauran gaɓoɓin kalma **[ƙwar, ƙi]**.

# Mako Na 1 Darasi Na 3 da Na 4

## ♥ Fahimtar Kalmomi ⏰ minti 5

Kalmomin da za a karanta: **[ƙwarai, ƙusa, ƙwarya]**

(M) 1. Rubuta kalmar **[ƙwarai]** a kan allo.
2. Nuna kowace gaɓa **[ƙwa/rai]** cikin kalmar kana/kina karantawa a hankali.
3. Aza yatsa a ƙasan kalma **[ƙwarai]** ka/ki karanta ta daga hagu zuwa dama da hanzari.

(M'D) 4. Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashe mai alamar zuciya.
5. Maimaita mataki na biyu da na uku (2-3) ta hanyar amfani da littafin ɗalibai.

(D) 6. Umurci ɗalibai da su karanta tare da nuna kalmar **[ƙwarai]** a cikin littafinsu.

(M) (M'D) (D) 7. Maimaita matakin farko zuwa na shida (1-6) da sauran kalmomin **[ƙusa, ƙwarya]**.

## ★ Karatun Jimla ⏰ minti 5

(M) 1. Rubuta jimlar **[Nana na <u>ɗauke</u> da ƙwaryar ƙwai.]** a kan allo.
2. Karanta jimlar tare da aza yatsa a ƙasan kowace kalma, yayin karantawa.
3. Koya wa ɗalibai ma'anar kalmar **[<u>ɗauke</u>]** kamar yadda ta zo a cikin jimlar, ta hanyar amfani da sassan jiki, ko hotuna, ko wata hanya da za su fahimta.

(M'D) 4. Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashe mai alamar tauraro.
5. Maimaita mataki na biyu (2) tare da ɗalibai ta hanyar amfani da littafin ɗalibai.
6. Tambayi ɗalibai ma'anar kalmar **[<u>ɗauke</u>]**, sannan a sake yi musu bayani idan har ba su ba da amsa ba.


(D) 7. Umurci ɗalibai da su karanta jimlar, tare da nuna kalmomin da suke karantawa a littafinsu.
8. Tambayi ɗalibai ma'anar kalmar **[<u>ɗauke</u>]**.

## Karatun Labari ⏰ minti 15

(M) 1. Jagoranci ɗalibai su gano sunayen abubuwan da ke cikin hoton littafinsu. A tambaye su abin da suke tsammani zai faru dangane da hotunan.
2. Rubuta labarin a kan allo.

**Sabuwar ƙwarya cike da ƙwai.**
**Kwarya kuwa ta cika ƙwarai.**
**Nana na ɗauke da ƙwaryar ƙwai.**
**Ta haɗu da Amina ɗauke da ƙwaƙwaƙwa.**
**Za su kai ƙwai da ƙwaƙwaƙwa a maƙwabta.**

3. Karanta labarin, kana/kina bi da yatsa a ƙasan kowace kalma.
4. Koya wa ɗalibai ma'anar kalmomi **[ɗauke, ƙwaƙwaƙwa, maƙwabta]** kamar yadda suka zo


Mako Na 1 Darasi Na 3 da Na 4

■ K ƙ Kw ƙw

● ƙwa ƙwar ƙi

♥ ƙwarai ƙusa ƙwarya

★ Nana na ɗauke da ƙwaryar ƙwai.

ƙusa ƙusa
ƙwarai ƙwarai
ƙwarya ƙwarya

ƙusa ƙusa
ƙwarai ƙwarai
ƙwarya ƙwarya

7

a cikin labarin, ta hanyar amfani da sassan jiki, ko hotuna, ko wata hanya da za su fahimta.

(M'D) 5. Maimaita mataki na uku (3) tare da umurtar ɗalibai da su nuna kalmomin a cikin littafinsu yayin da suke karantawa.
6. Tambayi ɗalibai ma'anar kalmomin **[ɗauke, ƙwaƙwaƙwa, maƙwabta]**, sannan a sake yi musu bayani idan har ba su ba da amsa ba.

(D) 7. Umurci ɗalibai da su nuna kalmomin a cikin littafinsu yayin da suke karanta labarin a bayyane. A tabbatar suna karatun tare. Zagaya don taimaka wa ɗaliban da ke da buƙata a lokacin da suke karatun.
8. Tambayi ɗalibai ma'anar kalmomin **[ɗauke, ƙwaƙwaƙwa, maƙwabta]**.

(M) 9. Auna fahimtar ɗalibai dangane da labarin, ta hanyar tambayoyi.


Umurci ɗalibai da su yi tunanin labarin da aka karanto kafin su ɗaga hannu.

**Tambayoyi**

1. **Me aka cika da ƙwarya?**
2. **Me Nana da Amina za su kai maƙwabta?**

## Karatun Labari a Bayyane ⏰ minti 5

(M) 1. Karanta kan labari **[Kura Da Kurege (1)]**
2. Nuna hoto idan akwai shi.
3. Tambayi ɗalibai su yi hasashen abin da suke ganin zai faru a labarin.
4. Koyar da ma'anar sabbin kalmomi **[kurege, tarko, damƙe]** ta hanyar amfani da sassan jiki, ko hotuna, ko wata hanya da za su fahimta.
5. Umurci ɗalibai su gano kalmomin nan a lokacin da kake/kike karanta labarin, ta hanyar ɗaga babban yatsa sama a duk lokacin da suka ji an faɗi kalmomin.
6. Karanta labarin ta yadda zai jawo hankalin ɗalibai.




*Wata rana yunwa ta kama **kurege**. Yana cikin yawo a daji sai ya ji ana ta kiransa. Ya juya haka, sai ga kura ɗaure a **tarko**. Ta ce, 'taimaka ka kwance ni, tun jiya nake ɗaure'. Kurege ya ce, 'na san halinki ba ki da amana, kar in yi maki rana ki yi mani dare'. Kura ta yi alƙawali ba za ta yi haka ba. Kurege ya ɗan tsaya kamar ba zai yarda ba, ta ba shi tausayi. Ya kwance ta. Yana kwance ta, sai ta **damƙe** shi, ta ce, 'wallahi yunwa nake ji. Jiya ban ci komai ba!'*

7. Tambayi ɗalibai su koma kan hasashensu.
8. Yi wa ɗalibai tambayoyin da ke ƙasan labarin.

**Tambayoyi**

1. **Wa yake jin yunwa?**
2. **Wa kurage ya gani a tarko?**

## Rubutu

minti 19

Kalmomin da za a rubuta: **[ƙusa, ƙwarai, ƙwarya]**

M 1. Rubuta **[ƙusa]** a kan allo, a hankali tare da bayanin yadda kake/kike rubutun.

MƊ 2. Umurci ɗalibai da su tusa **[ƙusa]** da ke da ɗigo-ɗigo a littafinsu na karatu, yayin da kai/ke ma kake/kike tusawa a kan allo.

Ɗ 3. Umurci ɗalibai da su tusa **[ƙusa]** da ke da ɗigo-ɗigo, sannan su rubuta **[ƙusa]** a filin da aka tanada a littafinsu don rubutu a ɓangaren dama.

4. A duba yanayin zamansu, da yanayin riƙon fensiri da inda suke fara rubutun da kuma yadda suke rubutun.

M MƊ Ɗ 5. Maimaita matakin farko zuwa na huɗu (1-4) da sauran kalmomin **[ƙwarai, ƙwarya]**.

## Aikin Gida

1. Tuna wa ɗalibai su karanta darasin yau tare da iyayensu ko 'yan'uwa ko abokai.
2. Tuna wa ɗalibai su gwada rubutun da aka yi a aji a sashen da aka tanadar don yin hakan a littafinsu.

## Matashiya a Kan Darasi Na Huɗu (4)

1. Tuna wa ɗalibai cewa za a maimaita darasin da ya gabata.
2. A sashen rubutu, a umurci ɗalibai daban-daban da su gano abinda ke cikin hoton da ke sashen rubutu a cikin littattafansu. Ka/ki karanta jimlar ***[Amina na ɗauke da kwakwakwa.]***, sannan a gabatar da mataki na biyu zuwa na huɗu (2-4) na sashen rubutu da jimlar.
3. A yi amfani da wannan labarin da tambayoyinsa a sashen Karatun Labari a Bayyane:

### Labarin Babangida Kurma (2)

*Ana cikin haka sai ga dila. Ya tambaye su abin da ke faruwa. Kurege ya yi masa bayani. Dila ya ce, 'ke kura fa?'. Ta ce, 'haka ne, ni fa yunwa nake ji'. Dila ya ce, 'yaushe rabonki da abinci?'. Ta ce, 'tun jiya war haka'. Ta nuna inda rana take jiya da bakinta. Ya ce, 'ya za ki nuna da baki'. Ta **nuna** da hannu ɗaya. Ya ce, 'ba mu gane ba'. Ta saki kurege ta nuna da hannu biyu. Kurege ya yi wuf! Ya **zura** da gudu, dila ma ya bi shi, suka bar kura **sororo** ba abinci.*

***Tambayoyi***

*1. Wa kurege ya yi wa bayani?*

*2. Me kurege ya yi da kura ta sake shi?*

*3. Me ya sa dila ya ce wa kura ta nuna masu da hannu biyu?*

# Mako Na 1 Darasi Na 5

Haruffan da za a yi amfani da su: **[Ƙ ƙ, Kw ƙw]**
Gaɓoɓin kalmar da za a yi amfani da su: **[ƙu, ƙa, ƙwai, ƙwa, ƙwar, ƙi]**
Kalmomin da za a yi amfani da su: **[ƙura, tuƙa, ƙwai, ƙwarai, ƙusa, ƙwarya]**
Labarin da za a a yi amfani da shi:

**Baba yana tuƙa mota.**
**Motar Baba ta yi ƙura sosai.**
**An cika motar Baba da kayan lambu.**
**Cikin motar Baba akwai ƙwai da yawa.**
**Kusa ta fasa tayar motar Baba.**

Tambayoyin da za a yi wa ɗalibai:

1. **Me aka cika a motar Baba?**
2. **Me ya fasa tayar motar Baba?**

Gaɓoɓin da za a yi amfani da su a shifta: **[ƙura, tuƙa, ƙwai, ƙwarai, ƙusa, ƙwarya]**

1. Rubuta **[Kƙ, Kw ƙw]** a kan allo.
2. Zaɓi ɗalibai maza da mata, a ƙalla biyar, don su karanta haruffan da aka rubuta a kan allon.
3. Rubuta **[ƙu, ƙa, ƙwai, ƙwa, ƙwar, ƙi]** a kan allo.
4. Zaɓi ɗalibai maza da mata, a ƙalla biyar, don su karanta gaɓoɓin kalmar da aka rubuta a kan allon.
5. Rubuta **[ƙura, tuƙa, ƙwai, ƙwarai, ƙusa, ƙwarya]** a kan allo.
6. Zaɓi ɗalibai maza da mata, a ƙalla biyar, don su karanta kalmomin da aka rubuta a kan allon.
7. Rubuta a kan allo.

   **Baba yana tuƙa mota.**
   **Motar Baba ta yi ƙura sosai.**
   **An cika motar Baba da kayan lambu.**
   **Cikin motar Baba akwai ƙwai da yawa.**
   **Kusa ta fasa tayar motar Baba.**

8. Zaɓi ɗalibai maza da mata, a ƙalla biyar, don su karanta labarin da aka rubuta a kan allon.
9. A yi wa kowane daga cikin ɗaliban da aka zaɓa tambayoyin auna fahimtar labarin da suka karanta kafin umurtar ɗalibi/ɗaliba na/ta gaba da ya/ta karanta labarin.
   1. **Me aka cika a motar Baba?**
   2. **Me ya fasa tayar motar Baba?**
10. Zaɓi ɗalibai maza da mata, a ƙalla biyar, don su rubuta gaɓoɓin da za ka/ki karanto musu.
11. Kalmomin da za a karanto su ne **[ƙura, tuƙa, ƙwai, ƙwarai, ƙusa, ƙwarya]**.
12. A auna sashen da ɗaliban suka fi rauni daga gwajin da aka gabatar.
13. Yayin da aka gano wuraren da yara suke da matsala, sai a yi ɗayan waɗanna:

- Idan ma fi yawan ɗaliban ba su zo makaranta a kwanakin dasussan ba, ko kuma ba su fahimci darussan ba, to a koyar da cikakken darasi ɗaya na wannan makon.
- Idan kuma ma fi yawan yara suna da rauni ne a wani sashi na darasi, sai a zaɓi sashen ƙarin ƙwarewa da yake da alaƙa da wannan sashen a koyar.

## Waƙa
minti 5

Waƙar da za a gabatar.

**<u>Waƙar Harafin Gw</u>**

**Gwanda da daɗi, gwanda X 2**
**Gwaiba da zaƙi, gwaiba X 2**
**Gwando da garɗi, gwando X 2**
**Kwano da zaƙi babu!**

M 1. Rera waƙar sau biyu, tare da kwaikwayon abin da ake faɗa a cikin waƙar.

MD 2. Maimaita mataki na ɗaya (1) tare da ɗalibai.

D 3. Umurci ɗalibai da su rera waƙar tare da kwaikwayon abin da ake faɗa a cikin waƙar.

## Amon sautin gaɓa
minti 3

Kalmomin da za a bambance: **[akwati, gwanda, gwauruwa, kwanciya]**

M 1. Ka/ki ce: **[akwati]**. Idan akwai hoton kalmar ɗalibai su nuna a littafinsu.
2. Maimaita furta kalmar **[akwati]** tare da tafa amon sautin kowace gaɓa.
3. Nuna yawan gaɓoɓin kalmar da yatsun hannu.

MD 4. Maimaita mataki na biyu da na uku (2-3) tare da ɗalibai.

D 5. Umurci ɗalibai da su furta, su tafa, sannan su nuna yawan gaɓoɓin da ke cikin sauran kalmomin **[gwanda, gwauruwa, kwanciya]**.

## Bambance Sautukan Gaɓoɓi
minti 3

Gaɓoɓin da za a bambance: **[Kwa, Gwa]**

Kalmomin da za a bambance: **[gwalo, gwari, tsalle, rigima, kwalba]**

M 1. Ka/ki ce: Ina so a ɗaga babban yatsa sama idan aka ji sautin gaɓar **[Kwa ko Gwa]** a cikin kalmomin da zan faɗa. Idan kuma ba a ji sautin gaɓar **[Kwa ko Gwa]** ba sai a yi ƙasa da babban yatsa.
2. Ka/ki ce: Misali **[gwari]**.
3. Ka/ki ce: **[tsalle]**

MD 4. Ka/ki ce: To mu fara **[gwari]** (A jagoranci ɗalibai da su ɗaga babban yatsa sama).
5. Ka/ki ce: **[tsalle]** (A jagoranci ɗalibai da su yi ƙasa da babban yatsansu).

D 6. Umurci ɗalibai da su ɗaga babban yatsansu sama ko ƙasa yayin da kake/kike furta kalmomin **[gwalo, gwari, tsalle, rigima, kwalba].**


Mako Na 2 Darasi Na 1 da Na 2

Nana na kwalliya za ta kasuwa.
Amina na kwaikwayon kwalliyar Nana.
Za su sayo agwagwa da gwaiba.
Amina ta ɗauko agwagi biyu.
Nana ta ɗauko kwandon gwaiba.
Gwaibar Nana na da kyau ƙwarai.

10

## Sunayen Haruffa
minti 5

Haruffan wannan darasi: **[Kw kw, Gw gw]**

M 1. Rubuta harafin **[Kw kw]** a kan allo.
2. Nuna harafin **[Kw kw]** ka/ki faɗi sunansa sau uku.

MD 3. Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashe mai alamar akwati.
4. Maimaita mataki na biyu (2) tare da umurtar ɗalibai da su nuna harafin a cikin littafinsu.

D 5. Umurci rukunan ɗalibai daban-daban da su karanta tare da nuna harafin **[Kw kw]** a cikin littafinsu.

M MD D 6. Maimaita matakin farko zuwa na biyar (1-5) da ɗaya harafin **[Gw gw]**.

MD 7. Umurci ɗalibai da su nuna harafin da za ka/ki furta a cikin littafinsu. (Yi ta furta haruffan **[Kw, Gw]** kana/kina sassauya su).

## Fahimtar Gaɓar Kalma
minti 5

Gaɓoɓin da za a karanta: **[gwa, gwai, kwai]**

M 1. Rubuta gaɓar **[gwa]** a kan allo.
2. Nuna kowane harafi tare da furta sunansa.
3. Aza yatsa a ƙasan gaɓar ka/ki bi ta daga hagu zuwa dama kana/kina karanta ta.

MD 4. Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashe mai alamar da'ira.
5. Maimaita mataki na biyu da na uku (2-3) ta hanyar amfani da littafin ɗalibai.

D 6. Umurci ɗalibai da su karanta tare da nuna gaɓar kalmar **[gwa]** a cikin littafinsu.

M MD D 7. Maimaita matakin farko zuwa na shida (1-6) da sauran gaɓoɓin kalma **[gwai, kwai]**.

# Mako Na 2 Darasi Na 1 da Na 2

## ♥ Fahimtar Kalmomi ⏰ minti 5

Kalmomin da za a karanta: **[agwagwa, gwaiba, kwaikwayo, akwai]**

(M) 1. Rubuta kalmar **[agwagwa]** a kan allo.
2. Nuna kowace gaɓa **[a/gwa/gwa]** cikin kalmar kana/kina karantawa a hankali.
3. Aza yatsa a ƙasan kalma **[agwagwa]** ka/ki karanta ta daga hagu zuwa dama da hanzari.

(M'D) 4. Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashe mai alamar zuciya.
5. Maimaita mataki na biyu da na uku (2-3) ta hanyar amfani da littafin ɗalibai.

(D) 6. Umurci ɗalibai da su karanta tare da nuna kalmar **[agwagwa]** a cikin littafinsu.

(M) (M'D) (D) 7. Maimaita matakin farko zuwa na shida (1-6) da sauran kalmomin [**gwaiba, kwaikwayo, akwai**].

## ★ Karatun Jimla ⏰ minti 5

(M) 1. Rubuta jimlar **[Nana ta ɗauko kwandon gwaiba.]** a kan allo.
2. Karanta jimlar tare da aza yatsa a ƙasan kowace kalma, yayin karantawa.
3. Koya wa ɗalibai ma'anar kalmar **[kwando]** kamar yadda ta zo a cikin jimlar, ta hanyar amfani da sassan jiki, ko hotuna, ko wata hanya da za su fahimta.

(M'D) 4. Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashe mai alamar tauraro.
5. Maimaita mataki na biyu (2) tare da ɗalibai ta hanyar amfani da littafin ɗalibai.
6. Tambayi ɗalibai ma'anar kalmar **[kwando]**, sannan a sake yi musu bayani idan har ba su ba da amsa ba.

(D) 7. Umurci ɗalibai da su karanta jimlar, tare da nuna kalmomin da suke karantawa a littafinsu.
8. Tambayi ɗalibai ma'anar kalmar **[kwando]**.

## Karatun Labari ⏰ minti 15

(M) 1. Jagoranci ɗalibai su gano sunayen abubuwan da ke cikin hoton littafinsu. A tambaye su abin da suke tsammani zai faru dangane da hotunan.
2. Rubuta labarin a kan allo.

**Nana na kwalliya za ta kasuwa.**

**Amina na kwaikwayon kwalliyar Nana.**


**Za su sayo agwagwa da gwaiba.**

**Amina ta ɗauko agwagi biyu.**

**Nana ta ɗauko kwandon gwaiba.**

**Gwaibar Nana na da kyau ƙwarai.**

3. Karanta labarin, kana/kina bi da yatsa a ƙasan kowace kalma.


Mako Na 2 Darasi Na 1 da Na 2
■ Kw kw Gw gw
● gwa gwai kwai
♥ agwagwa gwaiba kwaikwayo akwai
★ Nana ta ɗauko kwandon gwaiba.
akwai akwai
gwaiba gwaiba
agwagwa agwagwa
akwai akwai
gwaiba gwaiba
agwagwa agwagwa
11

4. Koya wa ɗalibai ma'anar kalmomi **[kwalliya, kwaikwayo, agwagwa]** kamar yadda suka zo a cikin labarin, ta hanyar amfani da sassan jiki, ko hotuna, ko wata hanya da za su fahimta.

(M'D) 5. Maimaita mataki na uku (3) tare da umurtar ɗalibai da su nuna kalmomin a cikin littafinsu yayin da suke karantawa.
6. Tambayi ɗalibai ma'anar kalmomin **[kwalliya, kwaikwayo, agwagwa]**, sannan a sake yi musu bayani idan har ba su ba da amsa ba.

(D) 7. Umurci ɗalibai da su nuna kalmomin a cikin littafinsu yayin da suke karanta labarin a bayyane. A tabbatar suna karatun tare. Zagaya don taimaka wa ɗaliban da ke da buƙata a lokacin da suke karatun.
8. Tambayi ɗalibai ma'anar kalmomin **[kwalliya, kwaikwayo, agwagwa]**.

(M) 9. Auna fahimtar ɗalibai dangane da labarin, ta hanyar tambayoyi.

Umurci ɗalibai da su yi tunanin labarin da aka karanto kafin su ɗaga hannu.

**Tambayoyi**

1. **Me Amina ke kwaikwayo?**
2. **Me Nana da Amina za su sayo?**

## Karatun Labari a Bayyane ⏰ minti 5

(M) 1. Karanta kan labari **[Altine da Kawayenta (1)]**
2. Nuna hoto idan akwai shi.
3. Tambayi ɗalibai su yi hasashen abin da suke ganin zai faru a labarin.
4. Koyar da ma'anar sabbin kalmomi **[birge, tuffa, yazawa]** ta hanyar amfani da sassan jiki, ko hotuna, ko wata hanya da za su fahimta.
5. Umurci ɗalibai su gano kalmomin nan a lokacin da kake/kike karanta labarin, ta hanyar ɗaga babban yatsa sama a duk lokacin da suka ji an faɗi kalmomin.
6. Karanta labarin ta yadda zai jawo hankalin ɗalibai.

*Altine yarinya ce `yar kimanin shekara goma. Mahaifiyarta na sana`ar sayar da kayan marmari. Altine na taimaka wa mahaifiyarta sosai. Wata rana Altine ta shirya ta tafi lambu sayen kayan marmari. A hanya ta haɗu da ƙawarta Laraba. Suka haɗu suka tafi lambu. Abin da ya fara* ***birge*** *su, shi ne irin tsarin da mai lambun ya yi. Layin mangwaro daban, layin lemo daban, layin gwaiba daban, layin yazawa daban, layin tuffa ma daban. Altine ta sayo kwandon* ***tuffa*** *da na gwaiba da na* ***yazawa****. Kawarta ta sayo guda biyu. Mai baro ya aza kaya ya turo masu zuwa gida.*

7. Tambayi ɗalibai su koma kan hasashensu.
8. Yi wa ɗalibai tambayoyin da ke ƙasan labarin.

**Tambayoyi**

1. **Altine yarinya ce `yar shekara nawa?**
2. **Wace ce Altine ta haɗu da ita a hanya?**

## Rubutu


minti 19

Kalmomin da za a rubuta: **[akwai, gwaiba, agwagwa]**

M 1. Rubuta **[akwai]** a kan allo, a hankali tare da bayanin yadda kake/kike rubutun.

M'Ɗ 2. Umurci ɗalibai da su tusa **[akwai]** da ke da ɗigo-ɗigo a littafinsu na karatu, yayin da kai/ke ma kake/kike tusawa a kan allo.

3. Umurci ɗalibai da su tusa **[akwai]** da ke da ɗigo-ɗigo, sannan su rubuta **[akwai]** a filin da aka tanada a littafinsu don rubutu a ɓangaren dama.




Ɗ 4. A duba yanayin zamansu, da yanayin riƙon fensiri da inda suke fara rubutun da kuma yadda suke rubutun.

M M'Ɗ Ɗ 5. Maimaita matakin farko zuwa na huɗu (1-4) da sauran kalmomin **[gwaiba, agwagwa]**.

## Aikin Gida

1. Tuna wa ɗalibai su karanta darasin yau tare da iyayensu ko'yan'uwa ko abokai.
2. Tuna wa ɗalibai su gwada rubutun da aka yi a aji a sashen da aka tanadar don yin hakan a littafansu.

## Matashiya a Kan Darasi Na Biyu (2)

1. Tuna wa ɗalibai cewa za a maimaita darasin da ya gabata.
2. A sashen rubutu, a umurci ɗalibai daban-daban da su gano abinda ke cikin hoton da ke sashen rubutu a cikin littattafansu. Ka/ki karanta jimlar **[Nana na ɗauke da kwandon gwaiba.]**, sannan a gabatar da mataki na biyu zuwa na huɗu (2-4) na sashen rubutu da jimlar.
3. A yi amfani da wannan labarin da tambayoyinsa a sashen Karatun Labari a Bayyane:

### *Altine da Kawayenta (2)*

*A hanyarsu ta dawowa, Altine ta ce, ta fahimci yadda ake cin* ***zarafin*** *mata, saboda haka babban burinta a rayuwa shi ne ta zama* ***lauya****, domin ƙwato wa mata haƙƙinsu. Lami ta ce, tana so ta zama likita. Da isar Altine gida, ta fitar da kaya, sai ta ga kwando huɗu. Ta je ta tambayi ƙawarta, ko ta bar* ***kwandonta*** *a cikin kayanta. Ta ce a`a. Altine ta tabbatar da cewa mai baro ne ya yi kuskure wajen ɗauko kayan. Ta yi sauri ta koma ta yi wa mai lambu bayani, ya ji daɗi, ya bar mata kwandon kyauta.*

***Tambayoyi***

*1. Me Altine take so ta zama a rayuwarta?*
*2. Me Lami take so ta zama a rayuwarta?*
*3 Me ya sa mai lambu ya bar mata kwando kyauta?*

## Waƙa ⏰ minti 5

Waƙar da za a gabatar.

**<u>Waƙar Harafin Gw</u>**

**Gwanda da daɗi, gwanda X 2**
**Gwaiba da zaƙi, gwaiba X 2**
**Gwando da garɗi, gwando X 2**
**Kwano da zaƙi babu!**

M 1. Rera waƙar sau biyu, tare da kwaikwayon abin da ake faɗa a cikin waƙar.

MD 2. Maimaita mataki na ɗaya (1) tare da ɗalibai.

D 3. Umurci ɗalibai da su rera waƙar tare da kwaikwayon abin da ake faɗa a cikin waƙar.

## Amon sautin gaba ⏰ minti 3

Kalmomin da za a bambance: **[kwanaki, gwamna, gwaninta, kwatance]**

M 1. Ka/ki ce: **[kwanaki]**. Idan akwai hoton kalmar ɗalibai su nuna a littafinsu.
2. Maimaita furta kalmar [kwanaki] tare da tafa amon sautin kowace gaba.
3. Nuna yawan gaɓoɓin kalmar da yatsun hannu.

MD 4. Maimaita mataki na biyu da na uku (2-3) tare da ɗalibai.

D 5. Umurci ɗalibai da su furta, su tafa, sannan su nuna yawan gaɓoɓin da ke cikin sauran kalmomin **[gwamna, gwaninta, kwatance]**.

## Bambance Sautukan Gaɓoɓi ⏰ minti 3

Gaɓoɓin da za a bambance: **[kwa, gwa]**

Kalmomin da za a bambance: **[gwauro, faɗuwa, kwaɗo, anini, kwabbai]**

M 1. Ka/ki ce: Ina so a ɗaga babban yatsa sama 👍 idan aka ji sautin gaɓar **[kwa ko gwa]** a cikin kalmomin da zan faɗa. Idan kuma ba a ji sautin gaɓar **[kwa ko gwa]** ba sai a yi ƙasa da babban yatsa 👎.
2. Ka/ki ce: Misali **[kwabbai]**.
3. Ka/ki ce: **[faɗuwa]** 👎

MD 4. Ka/ki ce: To mu fara **[kwabbai]** 👍 (A jagoranci ɗalibai da su ɗaga babban yatsa sama).
5. Ka/ki ce: **[faɗuwa]** 👎 (A jagoranci ɗalibai da su yi ƙasa da babban yatsansu).

D 6. Umurci ɗalibai da su ɗaga babban yatsansu sama ko ƙasa yayin da kake/kike furta kalmomin **[gwauro, faɗuwa, kwaɗo, anini, kwabbai]**.

Mako Na 2 Darasi Na 3 da Na 4



Abba da Nana a kan jaki.
Kaka ya sayo kwandon gwaza.
Za su kai gwazar gida a dafa.
Sun haɗu da gwarzo a hanya.
Kaka ta wanke gwazar a ƙwarya.
Gwazar za ta yi daɗi.

14

## ■ Sunayen Haruffa ⏰ minti 5

Haruffan wannan darasi: **[Kw kw, Gw gw]**

M 1. Rubuta harafin **[Kw kw]** a kan allo.
2. Nuna harafin **[Kw kw]** ka/ki faɗi sunansa sau uku.

MD 3. Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashe mai alamar akwati.
4. Maimaita mataki na biyu (2) tare da umurtar ɗalibai da su nuna harafin a cikin littafinsu.

D 5. Umurci rukunan ɗalibai daban-daban da su karanta tare da nuna harafin **[Kw kw]** a cikin littafinsu.

M MD D 6. Maimaita matakin farko zuwa na biyar (1-5) da ɗaya harafin **[Gw gw]**.

MD 7. Umurci ɗalibai da su nuna harafin da za ka/ki furta a cikin littafansu. (Yi ta furta haruffan **[Kw, Gw]** kana/kina sassauyasu).

## ● Fahimtar Gaɓar Kalma ⏰ minti 5

Gaɓoɓin da za a karanta: **[gwar, kwan, kwa]**

M 1. Rubuta gaɓar **[gwar]** a kan allo.
2. Nuna kowane harafi tare da furta sunansa.
3. Aza yatsa a ƙasan gaɓar ka/ki bi ta daga hagu zuwa dama kana/kina karanta ta.

MD 4. Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashe mai alamar da'ira.
5. Maimaita mataki na biyu da na uku (2-3) ta hanyar amfani da littafin ɗalibai.

D 6. Umurci ɗalibai da su karanta tare da nuna gaɓar kalmar **[gwar]** a cikin littafinsu.

M MD D 7. Maimaita matakin farko zuwa na shida (1-6) da sauran gaɓoɓin kalma **[kwan, kwa]**.


Mako Na 2 Darasi Na 3 da Na 4

■ Kw kw Gw gw

● gwar kwan kwa

♥ gwarzo gwaza kwakwa kwando

★ Za su kai gwazar gida a dafa.

gwaza gwaza
gwarzo gwarzo
kwakwa kwakwa

gwaza gwaza
gwarzo gwarzo
kwakwa kwakwa

15

## ♥ Fahimtar Kalmomi ⏰ minti 5

Kalmomin da za a karanta: **[gwarzo, gwaza, kwakwa, kwando]**

M 1. Rubuta kalmar **[gwarzo]** a kan allo.
2. Nuna kowace gaɓa **[gwar/zo]** cikin kalmar kana/kina karantawa a hankali.
3. Aza yatsa a ƙasan kalma **[gwarzo]** ka/ki karanta ta daga hagu zuwa dama da hanzari.

M'D 4. Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashe mai alamar zuciya.
5. Maimaita mataki na biyu da na uku (2-3) ta hanyar amfani da littafin ɗalibai.

D 6. Umurci ɗalibai da su karanta tare da nuna kalmar **[gwarzo]** a cikin littafinsu.

M M'D D 7. Maimaita matakin farko zuwa na shida (1-6) da sauran kalmomin **[gwaza, kwakwa, kwando]**.

## ★ Karatun Jimla ⏰ minti 5

M 1. Rubuta jimlar **[Za su kai gwazar gida a dafa.]** a kan allo.
2. Karanta jimlar tare da aza yatsa a ƙasan kowace kalma, yayin karantawa.
3. Koya wa ɗalibai ma'anar kalmar **[gwaza]** kamar yadda ta zo a cikin jimlar, ta hanyar amfani da sassan jiki, ko hotuna, ko wata hanya da za su fahimta.
4. Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashe mai alamar tauraro.

M'D 5. Maimaita mataki na biyu (2) tare da ɗalibai ta hanyar amfani da littafin ɗalibai.
6. Tambayi ɗalibai ma'anar kalmar **[gwaza]**, sannan a sake yi musu bayani idan har ba su ba da amsa ba.

D 7. Umurci ɗalibai da su karanta jimlar, tare da nuna kalmomin da suke karantawa a littafinsu.
8. Tambayi ɗalibai ma'anar kalmar **[gwaza]**.

## Karatun Labari ⏰ 15 minti

M 1. Jagoranci ɗalibai su gano sunayen abubuwan da ke cikin hoton littafinsu. A tambaye su abin da suke tsammani zai faru dangane da hotunan.
2. Rubuta labarin a kan allo.

**Abba da Nana a kan jaki.**
**Kaka ya sayo kwandon gwaza.**
**Za su kai gwazar gida a dafa.**
**Sun haɗu da gwarzo a hanya.**
**Kaka ta wanke gwazar a ƙwarya.**
**Gwazar za ta yi daɗi.**

3. Karanta labarin, kana/kina bi da yatsa a ƙasan kowace kalma.
4. Koya wa ɗalibai ma'anar kalmomi **[kwando, gwaza, gwarzo]** kamar yadda suka zo a cikin labarin, ta hanyar amfani da sassan jiki, ko hotuna, ko wata hanya da za su fahimta.

M'D 5. Maimaita mataki na uku (3) tare da umurtar ɗalibai da su nuna kalmomin a cikin littafinsu yayin da suke karantawa.
6. Tambayi ɗalibai ma'anar kalmomin **[kwando, gwaza, gwarzo]**, sannan a sake yi musu bayani idan har ba su ba da amsa ba.

D 7. Umurci ɗalibai da su nuna kalmomin a cikin littafinsu yayin da suke karanta labarin a bayyane. A tabbatar suna karatun tare. Zagaya don taimaka wa ɗaliban da ke da buƙata a lokacin da suke karatun.
8. Tambayi ɗalibai ma'anar kalmomin **[kwando, gwaza, gwarzo]**.

M 9. Auna fahimtar ɗalibai dangane da labarin, ta hanyar tambayoyi.

Umurci ɗalibai da su yi tunanin labarin da aka karanto kafin su ɗaga hannu.

**Tambayoyi**

1. **Me Kaka da Abba suka sayo?**
2. **Da wa Kaka da Abba suka haɗu?**

## Karatun Labari a Bayyane ⏰ minti 5

M 1. Karanta kan labari **[Kurege Mai Wayo (1)]**
2. Nuna hoto idan akwai shi.
3. Tambayi ɗalibai su yi hasashen abin da suke ganin zai faru a labarin.
4. Koyar da ma'anar sabbin kalmomi **[alade, sassabe, huɗa]** ta hanyar amfani da sassan jiki, ko hotuna, ko wata hanya da za su fahimta.
5. Umurci ɗalibai su gano kalmomin nan a lokacin da kake/kike karanta labarin, ta hanyar ɗaga babban yatsa sama a duk lokacin da suka ji an faɗi kalmomin.
6. Karanta labarin ta yadda zai jawo hankalin ɗalibai.


*Wata rana kura da kurege da maciji da* ***alade*** *suna jin tsananin yunwa. Suka haɗa kai domin su yi noma tare. Suka zaɓi wani fili a daji,*

*suka gyara ya zama gonarsu. Maciji ya ce, 'zai sassabe ya gyara gona'. **Alade** ya ce, 'ni zan yi **huɗa**. Kura ta ce, 'za ta nome gonar'. Kurege ya ce, 'zan nemo irin shukawa'. Maciji ya yi sassabe. Alade ya yi huɗa. Kura ta nome gona. Kurege kuma ya tafi neman irin shuka a kasuwa. A kasuwa, kurege ya ga wata mata da dawa, da masara da wake.*

7. Tambayi ɗalibai su koma kan hasashensu.
8. Yi wa ɗalibai tambayoyin da ke ƙasan labarin.

**Tambayoyi**

1. **Su wa suka haɗa kai domin su yi noma tare?**
2. **Wa kurege ya gani a kasuwa?**




## Rubutu

minti 19

Kalmomin da za a rubuta: **[gwaza, gwarzo, kwakwa]**

M 1. Rubuta **[gwaza]** a kan allo, a hankali tare da bayanin yadda kake/kike rubutun.

MƊ 2. Umurci ɗalibai da su tusa **[gwaza]** da ke da ɗigo-ɗigo a littafinsu na karatu, yayin da kai/ke ma kake/kike tusawa a kan allo.

Ɗ 3. Umurci ɗalibai da su tusa [gwaza] da ke da ɗigo-ɗigo, sannan su rubuta [gwaza] a filin da aka tanada a littafinsu don rubutu a ɓangaren dama.

4. A duba yanayin zamansu, da yanayin riƙon fensiri da inda suke fara rubutun da kuma yadda suke rubutun.

M MƊ Ɗ 5. Maimaita matakin farko zuwa na huɗu (1-4) da sauran kalmomin **[gwarzo, kwakwa]**.

## Aikin Gida

1. Tuna wa ɗalibai su karanta darasin yau tare da iyayensu ko 'yan'uwa ko abokai.
2. Tuna wa ɗalibai su gwada rubutun da aka yi a aji a sashen da aka tanadar don yin hakan a littafinsu.

## Matashiya A Kan Darasi Na Hudu (4)

1. Tuna wa ɗalibai cewa za a maimaita darasin da ya gabata.
2. A sashen rubutu, a umurci ɗalibai daban-daban da su gano abinda ke cikin hoton da ke sashen rubutu a cikin littattafansu. Ka/ki karanta jimlar **[Ga jaki ɗauke da kwandon gwaza.]**, sannan a gabatar da mataki na biyu zuwa na huɗu (2-4) na sashen rubutu da jimlar.
3. A yi amfani da wannan labarin da tambayoyinsa a sashen Karatun Labari a Bayyane:

### Kurege Mai Wayo (2)

*Da lokacin tafiyar matar nan ya yi sai kurege ya ruga gaba ya faɗi kamar ya mutu, sai matar ta ce wai! Ga nama na samu. Amma idan na ɗauka zai cinye mani dawa. Da kurege ya ji ba ta **ɗauke** shi ba, sai ya sake shan gabanta ya kwanta. Sai ta ce wannan karon kam sai na ɗauka. Ta ɗauki kurege ta sa cikin ƙwaryarta. Ta shiga daji neman **ɓawon kalgo** ta ɗaure kurege. Sai kurege ya ɗauke ƙwaryar. Ko da ta dawo sai ta tarar babu ƙwarya, babu kurege. Kurege ya kai iri suka shuka da abokansa.*

***Tamabayoyi***

1. *A ina matar nan ta sa kurege?*
2. *Me kurege ya ɗauke wa matar nan?*
3. *Me ya sa kurege ya yi tunanin ya je ya kwanta kamar ya mutu?*

# Mako Na 2 Darasi Na 5

Haruffan da za a yi amfani da su: **[Kw kw, Gw gw]**

Gaɓoɓin kalmar da za a yi amfani da su: **[gwa, gwai, kwai, gwar, kwan, kwa]**

Kalmomin da za a yi amfani da su: **[agwagwa, gwaiba, kwaikwayo, akwai, gwarzo, gwaza, kwakwa, kwando]**

Labarin da za a a yi amfani da shi:

**Nana na kwalliya za ta kasuwa.**
**Amina na kwaikwayon kwalliyar Nana.**
**Za su sayo agwagwa da gwaiba.**
**Amina ta ɗauko agwagi biyu.**
**Nana ta ɗauko kwandon gwaiba.**
**Gwaibar Nana na da kyau ƙwarai.**

Tambayoyin da za a yi wa ɗalibai:

1. **Me Amina ke kwaikwayo?**
2. **Me Nana da Amina za su sayo?**

Gaɓoɓin da za a yi amfani da su a shifta: **[ƙura, tuƙa, ƙwai, ƙwarai, ƙusa, ƙwarya]**

1. Rubuta **[Kw kw, Gw gw]** a kan allo.
2. Zaɓi ɗalibai maza da mata, a ƙalla biyar, don su karanta haruffan da aka rubuta a kan allon.
3. Rubuta **[gwa, gwai, kwai, gwar, kwan, kwa]** a kan allo.
4. Zaɓi ɗalibai maza da mata, a ƙalla biyar, don su karanta gaɓoɓin kalmar da aka rubuta a kan allon.
5. Rubuta **[agwagwa, gwaiba, kwaikwayo, akwai, gwarzo, gwaza, kwakwa, kwando]** a kan allo.
6. Zaɓi ɗalibai maza da mata, a ƙalla biyar, don su karanta kalmomin da aka rubuta a kan allon.
7. Rubuta a kan allo.

   **Nana na kwalliya za ta kasuwa.**
   **Amina na kwaikwayon kwalliyar Nana.**
   **Za su sayo agwagwa da gwaiba.**
   **Amina ta ɗauko agwagi biyu.**
   **Nana ta ɗauko kwandon gwaiba.**
   **Gwaibar Nana na da kyau ƙwarai.**
8. Zaɓi ɗalibai maza da mata, a ƙalla biyar, don su karanta labarin da aka rubuta a kan allon.
9. A yi wa kowane daga cikin ɗaliban da aka zaɓa tambayoyin auna fahimtar labarin da suka karanta kafin umurtar dalibi/ɗaliba na/ta gaba da ya/ta karanta labarin.
   1. **Me Amina ke kwaikwayo?**
   2. **Me Nana da Amina za su sayo?**
10. Zaɓi ɗalibai maza da mata, a ƙalla biyar, don su rubuta gaɓoɓin da za ka/ki karanto musu.
11. Kalmomin da za a karanto su ne **[agwagwa, gwaiba, kwaikwayo, akwai, gwarzo, gwaza, kwakwa, kwando]**.
12. A auna sashen da ɗaliban suka fi rauni daga gwajin da aka gabatar.
13. Yayin da aka gano wuraren da yara suke da matsala, sai a yi ɗayan waɗannan:
    - Idan ma fi yawan ɗaliban ba su zo makaranta a kwanakin dasussan ba, ko kuma ba su fahimci darussan ba, to a koyar da cikakken darasi ɗaya na wannan makon.
    - Idan kuma ma fi yawan yara suna da rauni ne a wani sashi na darasi, sai a zaɓi sashen ƙarin ƙwarewa da yake da alaƙa da wannan sashen a koyar.

# Mako Na 3 Darasi Na 1 da Na 2

## Waƙa

minti 5

Waƙar da za a gabatar.

**<u>Waƙar Barin Ɓarna Da Kazanta</u>**

**`Yan yara ban da ɓarna X 2**
**Ɓera ne ad da ɓarna X 2**
**Bari fyace majina nan X 2**
**fyacewa har ga riga X 2**
**In kun fyace ga riga X 2**
**Ai ko dai kun ƙazanta X 2**

M 1. Rera waƙar sau biyu, tare da kwaikwayon abin da ake faɗa a cikin waƙar.

MD 2. Maimaita mataki na ɗaya (1) tare da ɗalibai.

D 3. Umurci ɗalibai da su rera waƙar tare da kwaikwayon abin da ake faɗa a cikin waƙar.

## Amon sautin gaɓa

minti 3

Kalmomin da za a bambance: **[ɓarna, ɓaure, fyace, ɓawo]**

M 1. Ka/ki ce: **[ɓarna]**. Idan akwai hoton kalmar ɗalibai su nuna a littafinsu.

2. Maimaita furta kalmar **[ɓarna]** tare da tafa amon sautin kowace gaɓa.

3. Nuna yawan gaɓoɓin kalmar da yatsun hannu.

MD 4. Maimaita mataki na biyu da na uku (2-3) tare da ɗalibai.

D 5. Umurci ɗalibai da su furta, su tafa, sannan su nuna yawan gaɓoɓin da ke cikin sauran kalmomin **[ɓaure, fyace, ɓawo]**.

## Bambance Sautukan Gaɓoɓi

minti 3

Gaɓar da za a bambance: **[ɓa, fya]**

Kalmomin da za a bambance: **[ɓangare, ɓace, fyace, ɗaki, kogi]**

M 1. Ka/ki ce: Ina so a ɗaga babban yatsa sama idan aka ji sautin gaɓar **[ɓa ko fya]** a cikin kalmomin da zan faɗa. Idan kuma ba a ji sautin gaɓar **[ɓa ko fya]** ba sai a yi ƙasa da babban yatsa .

2. Ka/ki ce: Misali **[fyace]**.

3. Ka/ki ce: **[kogi]**

MD 4. Ka/ki ce: To mu fara **[fyace]** (A jagoranci ɗalibai da su ɗaga babban yatsa sama).

5. Ka/ki ce: **[kogi]** (A jagoranci ɗalibai da su yi ƙasa da babban yatsansu).

D 6. Umurci ɗalibai da su ɗaga babban yatsansu sama ko ƙasa yayin da kake/kike furta kalmomin: **[ɓangare, ɓace, fyace, ɗaki, kogi]**.


Mako Na 3 Darasi Na 1 da Na 2

Taɓaryar Kaka ta ɓata tun jiya.
Su Nana sun fita neman taɓaryar saƙo-saƙo.
A hanya Nana ta fyace hancinta.
Ta karce hancinta da ɓawon kalgo.
Nana ta gano taɓaryar Kaka a hanyar gona.

18

## Sunayen Haruffa

minti 5

Haruffan wannan darasi: **[Ɓ ɓ, Fy fy]**

M 1. Rubuta harafin **[Ɓ ɓ]** a kan allo.

2. Nuna harafin **[Ɓ ɓ]** ka/ki faɗi sunansa sau uku.

MD 3. Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashe mai alamar akwati.

4. Maimaita mataki na biyu (2) tare da umurtar ɗalibai da su nuna harafin a cikin littafinsu.

D 5. Umurci rukunan ɗalibai daban-daban da su karanta tare da nuna harafin **[Ɓ ɓ]** a cikin littafinsu.

M MD D 6. Maimaita matakin farko zuwa na biyar (1-5) da ɗaya harafin **[Fy fy]**.

MD 7. Umurci ɗalibai da su nuna harafin da za ka/ki furta a cikin littafinsu. (Yi ta furta haruffan **[Ɓ, Fy]** kana/kina sassauya su).

## Fahimtar Gaɓar Kalma

minti 5

Gaɓoɓin da za a karanta: **[ɓa, ɓar, fya]**

M 1. Rubuta gaɓar **[ɓa]** a kan allo.

2. Nuna kowane harafi tare da furta sunansa.

3. Aza yatsa a ƙasan gaɓar ka/ki bi ta daga hagu zuwa dama kana/kina karanta ta.

MD 4. Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashe mai alamar da'ira.

5. Maimaita mataki na biyu da na uku (2-3) ta hanyar amfani da littafin ɗalibai.

D 6. Umurci ɗalibai da su karanta tare da nuna gaɓar kalmar **[ɓa]** a cikin littafinsu.

M MD D 7. Maimaita matakin farko zuwa na shida (1-6) da sauran gaɓoɓin kalma **[ɓar, fya]**.

## ♥ Fahimtar Kalmomi ⏰ minti 5

Kalmomin da za a karanta: **[ɓawo, fyace, ɓata, taɓarya]**

M 1. Rubuta kalmar **[ɓawo]** a kan allo.
2. Nuna kowace gaɓa **[ɓa/wo]** cikin kalmar kana/kina karantawa a hankali.
3. Aza yatsa a ƙasan kalma **[ɓawo]** ka/ki karanta ta daga hagu zuwa dama da hanzari.

M'D 4. Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashe mai alamar zuciya.
5. Maimaita mataki na biyu da na uku (2-3) ta hanyar amfani da littafin ɗalibai.

D 6. Umurci ɗalibai da su karanta tare da nuna kalmar **[ɓawo]** a cikin littafinsu.

M M'D D 7. Maimaita matakin farko zuwa na shida (1-6) da sauran kalmomin **[fyace, ɓata, taɓarya]**.

## ★ Karatun Jimla ⏰ minti 5

M 1. Rubuta jimlar **[Nana ta fyace hancinta da ɓawon kalgo.]** a kan allo.
2. Karanta jimlar tare da aza yatsa a ƙasan kowace kalma, yayin karantawa.
3. Koya wa ɗalibai ma'anar kalmar **[kalgo]** kamar yadda ta zo a cikin jimlar, ta hanyar amfani da sassan jiki, ko hotuna, ko wata hanya da za su fahimta.

M'D 4. Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashe mai alamar tauraro.
5. Maimaita mataki na biyu (2) tare da ɗalibai ta hanyar amfani da littafin ɗalibai.
6. Tambayi ɗalibai ma'anar kalmar **[kalgo]**, sannan a sake yi musu bayani idan har ba su ba da amsa ba.

D 7. Umurci ɗalibai da su karanta jimlar, tare da nuna kalmomin da suke karantawa a littafinsu.
8. Tambayi ɗalibai ma'anar kalmar **[kalgo]**.

## Karatun Labari ⏰ minti 15

M 1. Jagoranci ɗalibai su gano sunayen abubuwan da ke cikin hoton littafinsu. A tambaye su abin da suke tsammani zai faru dangane da hotunan.
2. Rubuta labarin a kan allo.

**Taɓaryar Kaka ta ɓata tun jiya.**


**Su Nana sun fita neman taɓaryar saƙo-saƙo.**

**A hanya Nana ta fyace hancinta.**

**Ta karce hancinta da ɓawon kalgo.**

**Nana ta gano taɓaryar Kaka a hanyar gona.**

3. Karanta labarin, kana/kina bi da yatsa a ƙasan kowace kalma.



Mako Na 3 Darasi Na 1 da Na 2

■ Ɓ ɓ Fy fy

● ɓa ɓar fya

♥ ɓawo fyace ɓata taɓarya

★ Nana ta fyace hancinta da ɓawon kalgo.

ɓawo ɓawo
fyace fyace
ɓata ɓata

ɓawo ɓawo
fyace fyace
ɓata ɓata

19

4. Koya wa ɗalibai ma'anar kalmomi **[kalgo, ɓawo, saƙo-saƙo]** kamar yadda suka zo a cikin labarin, ta hanyar amfani da sassan jiki, ko hotuna, ko wata hanya da za su fahimta.

M'D 5. Maimaita mataki na uku (3) tare da umurtar ɗalibai da su nuna kalmomin a cikin littafinsu yayin da suke karantawa.
6. Tambayi ɗalibai ma'anar kalmomin **[kalgo, ɓawo, saƙo-saƙo]**, sannan a sake yi musu bayani idan har ba su ba da amsa ba.

D 7. Umurci ɗalibai da su nuna kalmomin a cikin littafinsu yayin da suke karanta labarin a bayyane. A tabbatar suna karatun tare. Zagaya don taimaka wa ɗaliban da ke da buƙata a lokacin da suke karatun.
8. Tambayi ɗalibai ma'anar kalmomin **[kalgo, ɓawo, saƙo-saƙo]**.

M 9. Auna fahimtar ɗalibai dangane da labarin, ta hanyar tambayoyi.

Umurci ɗalibai da su yi tunanin labarin da aka karanto kafin su ɗaga hannu.

**Tambayoyi**

1. **Me Nana da Amina ke nema?**
2. **A ina aka ga taɓaryar Kaka?**

## Karatun Labari a Bayyane ⏰ minti 5

M 1. Karanta kan labari **[Labarin Damon Sarki (1)]**
2. Nuna hoto idan akwai shi.
3. Tambayi ɗalibai su yi hasashen abin da suke ganin zai faru a labarin.
4. Koyar da ma'anar sabbin kalmomi [**damo, kiyaye, soya]** ta hanyar amfani da sassan jiki, ko hotuna, ko wata hanya da za su fahimta.

5. Umurci ɗalibai su gano kalmomin nan a lokacin da kake/kike karanta labarin, ta hanyar ɗaga babban yatsa sama a duk lokacin da suka ji an faɗi kalmomin.
6. Karanta labarin ta yadda zai jawo hankalin ɗalibai.

   *A wani gari an yi wani sarki mai ƙatuwar gona. Sai ya sayo **damo** masu yawan gaske don su yi masa gadin gona. Sarki ya sa aka yi shela a gari cewa, kar wanda ya ci damonsa, duk wanda ya ci zai mutu. Kowa ya **kiyaye** a garin. Rannan kwaɗayin nama ya kama gizo. Ya yi ta neman naman da zai ci bai samu ba. Sai kawai ya tafi gonar sarki. Ya ɗauko damo ɗaya, ya yanka, ya kawo gida aka **soya** masa ya cinye. Bayan wani lokaci gizo ya ƙara komawa. Haka ya yi ta yi har suka ƙare.*
7. Tambayi ɗalibai su koma kan hasashensu.
8. Yi wa ɗalibai tambayoyin da ke ƙasan labarin.

**Tambayoyi**

1. **Me sarki ya sayo domin su yi masa gadi?**
2. **A ina gizo ya ɗauko damo?**

## Rubutu

minti 19

Kalmomin da za a rubuta: **[ɓawo, fyace, ɓata]**

M 1. Rubuta **[ɓawo]** a kan allo, a hankali tare da bayanin yadda kake/kike rubutun.

MƊ 2. Umurci ɗalibai da su tusa **[ɓawo]** da ke da ɗigo-ɗigo a littafinsu na karatu, yayin da kai/ke ma kake/kike tusawa a kan allo.




Ɗ 3. Umurci ɗalibai da su tusa **[ɓawo]** da ke da ɗigo-ɗigo, sannan su rubuta **[ɓawo]** a filin da aka tanada a littafinsu don rubutu a bangaren dama.

4. A duba yanayin zamansu, da yanayin riƙon fensiri da inda suke fara rubutun da kuma yadda suke rubutun.

M MƊ Ɗ 5. Maimaita matakin farko zuwa na huɗu (1-4) da sauran kalmomin **[fyace, ɓata]**.

## Aikin Gida

1. Tuna wa ɗalibai su karanta darasin yau tare da iyayensu ko 'yan'uwa ko abokai.
2. Tuna wa ɗalibai su gwada rubutun da aka yi a aji a sashen da aka tanadar don yin hakan a littafinsu.

## Matashiya A Kan Darasi Na Biyu (2)

1. Tuna wa ɗalibai cewa za a maimaita darasin da ya gabata.
2. A sashen rubutu, a umurci ɗalibai daban-daban da su gano abinda ke cikin hoton da ke sashen rubutu a cikin littattafansu. Ka/ki karanta jimlar **[Nana na riƙe da taɓarya.]**, sannan a gabatar da mataki na biyu zuwa na huɗu (2-4) na sashen rubutu da jimlar.
3. A yi amfani da wannan labarin da tambayoyinsa a sashen Karatun Labari a Bayyane:

### Labarin Damon Sarki (2)

*Bayan gizo ya gama cinye damon sarki gabaɗayansu. Sai ciwon ciki ya kama shi. **Ciwo** ya yi tsanani, har ba ya iya tashi tsaye. Matarsa ta goya shi, domin ta kai shi wurin maimagani. A hanya, kura da zaki suka tambaye ta, 'ina za ki'. Ta ce, 'zan kai gizo wurin magani'. Suka ce, 'ba wani magani sai mutuwa, gizo damon sarki ya ci'. Ta rusa ihu, ta ce, 'gizo! Kwaɗayinka ya ja maka **halaka**'. Ka zauna nan bayan gari, kar ka mutu ka dame mu da **wari**'. Ta tafi ta bar shi nan ya mutu shi kaɗai.*

***Tambayoyi***

1. *Wace ce ta goya gizo?*
2. *A ina gizo ya mutu?*
3. *Me ya sa kowa ya ƙi cin damon sarki sai gizo?*

## Waƙa
minti 5

Waƙar da za a gabatar.

**Waƙar Barin Ɓarna Da Kazanta**

**`Yan yara ban da ɓarna X 2**
**Ɓera ne ad da ɓarna X 2**
**Bari fyace majina nan X 2**
**fyacewa har ga riga X 2**
**In kun fyace ga riga X 2**
**Ai ko dai kun ƙazanta X 2**

M 1. Rera waƙar sau biyu, tare da kwaikwayon abin da ake faɗa a cikin waƙar.

MƊ 2. Maimaita mataki na ɗaya (1) tare da ɗalibai.

Ɗ 3. Umurci ɗalibai da su rera waƙar tare da kwaikwayon abin da ake faɗa a cikin waƙar.

## Amon sautin gaɓa
minti 3

Kalmomin da za a bambance: **[ɓarewa, fyacewa, fyaɗewa, ɓace]**

M 1. Ka/ki ce: **[ɓarewa]**. Idan akwai hoton kalmar ɗalibai su nuna a littafinsu.

2. Maimaita furta kalmar **[ɓarewa]** tare da tafa amon sautin kowace gaɓa.

3. Nuna yawan gaɓoɓin kalmar da yatsun hannu.

MƊ 4. Maimaita mataki na biyu da na uku (2-3) tare da ɗalibai.

Ɗ 5. Umurci ɗalibai da su furta, su tafa, sannan su nuna yawan gaɓoɓin da ke cikin sauran kalmomin **[fyacewa, fyaɗewa, ɓace]**.

## Bambance Sautukan Gaɓoɓi
minti 3

Gaɓar da za a bambance: **[ɓa, fya]**

Kalmomin da za a bambance: **[fyacewa, ɓangaranci, fyaɗewa, teku, fadama]**

M 1. Ka/ki ce: Ina so a ɗaga babban yatsa sama idan aka ji sautin gaɓar **[ɓa ko fya]** a cikin kalmomin da zan faɗa. Idan kuma ba a ji sautin gaɓar **[ɓa ko fya]** ba sai a yi ƙasa da babban yatsa.

2. Ka/ki ce: Misali **[fyaɗewa]**.

3. Ka/ki ce: **[teku]**

MƊ 4. Ka/ki ce: To mu fara **[fyaɗewa]** (A jagoranci ɗalibai da su ɗaga babban yatsa sama).

5. Ka/ki ce: **[teku]** (A jagoranci ɗalibai da su yi ƙasa da babban yatsansu).

Ɗ 6. Umurci ɗalibai da su ɗaga babban yatsansu sama ko ƙasa yayin da kake/kike furta kalmomin: **[fyacewa, ɓangaranci, fyaɗewa, teku, fadama]**.

Mako Na 3 Darasi Na 3 da Na 4



Katon ɓera a ɗakin Mama.
Abba ya sa sandarsa ya fyaɗe ɓera.
Ɓera ya fyaɗu sosai ya mutu.
Mama ta ji ɗaɗin fyaɗe ɓeran.
Abba ya jefar da ɓera a cikin shara.

22

## Sunayen Haruffa
minti 5

Haruffan wannan darasi: **[Ɓ ɓ, Fy fy]**

M 1. Rubuta harafin **[Ɓ ɓ]** a kan allo.

2. Nuna harafin **[Ɓ ɓ]** ka/ki faɗi sunansa sau uku.

MƊ 3. Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashe mai alamar akwati.

4. Maimaita mataki na biyu (2) tare da umurtar ɗalibai da su nuna harafin a cikin littafinsu.

Ɗ 5. Umurci rukunan ɗalibai daban-daban da su karanta tare da nuna harafin [Ɓ ɓ] a cikin littafinsu.

M MƊ Ɗ 6. Maimaita matakin farko zuwa na biyar (1-5) da ɗaya harafin **[Fy fy]**.

MƊ 7. Umurci ɗalibai da su nuna harafin da za ka/ki furta a cikin littafinsu. (Yi ta furta haruffan **[Ɓ, Fy]** kana/kina sassauya su).

## Fahimtar Gaɓar Kalma
minti 5

Gaɓoɓin da za a karanta: **[ɓal, ɓe, fya]**

M 1. Rubuta gaɓar **[ɓal]** a kan allo.

2. Nuna kowane harafi tare da furta sunansa.

3. Aza yatsa a ƙasan gaɓar ka/ki bi ta daga hagu zuwa dama kana/kina karanta ta.

MƊ 4. Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashe mai alamar da'ira.

5. Maimaita mataki na biyu da na uku (2-3) ta hanyar amfani da littafin ɗalibai.

Ɗ 6. Umurci ɗalibai da su karanta tare da nuna gaɓar kalmar **[ɓal]** a cikin littafinsu.

M MƊ Ɗ 7. Maimaita matakin farko zuwa na shida (1-6) da sauran gaɓoɓin kalma **[ɓe, fya]**.

# Mako Na 3 Darasi Na 3 da Na 4

## ♥ Fahimtar Kalmomi

⏰ minti 5

Kalmomin da za a karanta: **[ɓalli, fyaɗe, ɓera, fyaɗu]**

M
1. Rubuta kalmar **[ɓalli]** a kan allo.
2. Nuna kowace gaɓa **[ɓal/li]** cikin kalmar kana/kina karantawa a hankali.
3. Aza yatsa a ƙasan kalma **[ɓalli]** ka/ki karanta ta daga hagu zuwa dama da hanzari.

M'D 4. Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashe mai alamar zuciya.

5. Maimaita mataki na biyu da na uku (2-3) ta hanyar amfani da littafin ɗalibai.

D 6. Umurci ɗalibai da su karanta tare da nuna kalmar **[ɓalli]** a cikin littafinsu.

M M'D D 7. Maimaita matakin farko zuwa na shida (1-6) da sauran kalmomin **[fyaɗe, ɓera, fyaɗu]**.

## ★ Karatun Jimla

⏰ minti 5

M 1. Rubuta jimlar **[Mama ta ji ɗaɗin fyaɗe ɓeran.]** a kan allo.

2. Karanta jimlar tare da aza yatsa a ƙasan kowace kalma, yayin karantawa.
3. Koya wa ɗalibai ma'anar kalmar **[fyaɗe]** kamar yadda ta zo a cikin jimlar, ta hanyar amfani da sassan jiki, ko hotuna, ko wata hanya da za su fahimta.

M'D 4. Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashe mai alamar tauraro.

5. Maimaita mataki na biyu (2) tare da ɗalibai ta hanyar amfani da littafin ɗalibai.
6. Tambayi ɗalibai ma'anar kalmar **[fyaɗe]**, sannan a sake yi musu bayani idan har ba su ba da amsa ba.

D 7. Umurci ɗalibai da su karanta jimlar, tare da nuna kalmomin da suke karantawa a littafinsu.

8. Tambayi ɗalibai ma'anar kalmar **[fyaɗe]**.

## Karatun Labari

⏰ minti 15

M 1. Jagoranci ɗalibai su gano sunayen abubuwan da ke cikin hoton littafinsu. A tambaye su abin da suke tsammani zai faru dangane da hotunan.

2. Rubuta labarin a kan allo.

   **Katon ɓera a ɗakin Mama.**

   **Abba ya sa sandarsa ya fyaɗe ɓera.**

   **Ɓera ya fyaɗu sosai ya mutu.**

   **Mama ta ji ɗaɗin fyaɗe ɓeran.**

   **Abba ya jefar da ɓera a cikin shara.**

3. Karanta labarin, kana/kina bi da yatsa a ƙasan kowace kalma.



Mako Na 3 Darasi Na 3 da Na 4

■ Ɓ ɓ Fy fy

● ɓal ɓe fya

♥ ɓalli fyaɗe ɓera fyaɗu

★ Mama ta ji ɗaɗin fyaɗe ɓeran.

ɓalli ɓalli

fyaɗe fyaɗe

ɓera ɓera

ɓalli ɓalli

fyaɗe fyaɗe

ɓera ɓera

23

4. Koya wa ɗalibai ma'anar kalmomi **[fyaɗe, ɓera]** kamar yadda suka zo a cikin labarin, ta hanyar amfani da sassan jiki, ko hotuna, ko wata hanya da za su fahimta.

M'D 5. Maimaita mataki na uku (3) tare da umurtar ɗalibai da su nuna kalmomin a cikin littafinsu yayin da suke karantawa.

6. Tambayi ɗalibai ma'anar kalmomin **[fyaɗe, ɓera]**, sannan a sake yi musu bayani idan har ba su ba da amsa ba.

D 7. Umurci ɗalibai da su nuna kalmomin a cikin littafinsu yayin da suke karanta labarin a bayyane. A tabbatar suna karatun tare. Zagaya don taimaka wa ɗaliban da ke da buƙata a lokacin da suke karatun.

8. Tambayi ɗalibai ma'anar kalmomin **[fyaɗe, ɓera]**.

M 9. Auna fahimtar ɗalibai dangane da labarin, ta hanyar tambayoyi.

   Umurci ɗalibai da su yi tunanin labarin da aka karanto kafin su ɗaga hannu.

**Tambayoyi**

1. **Me Abba ya yi wa ɓera?**
2. **Daɗin me Mama ta ji?**

## Karatun Labari a Bayyane

⏰ minti 5

M 1. Karanta kan labari **[Yarinya Mai Neman Ganyen Miya (1)]**

2. Nuna hoto idan akwai shi.
3. Tambayi ɗalibai su yi hasashen abin da suke ganin zai faru a labarin.
4. Koyar da ma'anar sabbin kalmomi **[kauye, ƙanenta, gagara]** ta hanyar amfani da sassan jiki, ko hotuna, ko wata hanya da za su fahimta.
5. Umurci ɗalibai su gano kalmomin nan a lokacin da kake/kike karanta labarin, ta hanyar ɗaga babban yatsa sama a duk lokacin da suka ji an faɗi kalmomin.

6. Karanta labarin ta yadda zai jawo hankalin ɗalibai.

   *A wani **ƙauye**, akwai wata yarinya mai suna Cindo. Rannan an aike ta sayo ganyen miya ita da **ƙanenta**. A hanyarsu ta dawowa suka gamu da wata tsohuwa. Ta ce masu, 'sannunku, ku taimaka mani da ganye ɗaya mana'. Cindo ta ce, 'ba za a bayar ba'. Suka ci gaba da tafiya abinsu. Har sun kai wani dutse suka zauna domin su huta. Bayan sun huta, za su tafi gida, Cindo ta **gagara** tashi. Suka yi suka yi, abu ya gagara. Suka tafi gida suka faɗa wa iyayensu. Su ma suka zo suka yi ta ƙokari amma abun ya gagara.*

7. Tambayi ɗalibai su koma kan hasashensu.
8. Yi wa ɗalibai tambayoyin da ke ƙasan labarin.

**Tambayoyi**

1. **Me aka aiki Cindo ta sayo ita da ƙanenta?**
2. **Wace ce su Cindo suka gamu da ita a hanya?**


## Rubutu

minti 19

Kalmomin da za a rubuta: **[ɓalli, fyaɗe, ɓera]**

(M) 1. Rubuta **[ɓalli]** a kan allo, a hankali tare da bayanin yadda kake/kike rubutun.

(MƊ) 2. Umurci ɗalibai da su tusa **[ɓalli]** da ke da ɗigo-ɗigo a littafinsu na karatu, yayin da kai/ke ma kake/kike tusawa a kan allo.




(Ɗ) 3. Umurci ɗalibai da su tusa **[ɓalli]** da ke da ɗigo-ɗigo, sannan su rubuta **[ɓalli]** a filin da aka tanada a littafinsu don rubutu a ɓangaren dama.

4. A duba yanayin zamansu, da yanayin riƙon fensiri da inda suke fara rubutun da kuma yadda suke rubutun.

(M) (MƊ) (Ɗ) 5. Maimaita matakin farko zuwa na huɗu (1-4) da sauran kalmomin **[fyaɗe, ɓera]**.

## Aikin Gida

1. Tuna wa ɗalibai su karanta darasin yau tare da iyayensu ko 'yan'uwa ko abokai.
2. Tuna wa ɗalibai su gwada rubutun da aka yi a aji a sashen da aka tanadar don yin hakan a littafansu.

## Matashiya A Kan Darasi Na Huɗu (4)

1. Tuna wa ɗalibai cewa za a maimaita darasin da ya gabata.
2. A sashen rubutu, a umurci ɗalibai daban-daban da su gano abinda ke cikin hoton da ke sashen rubutu a cikin littattafansu. Ka/ki karanta jimlar **[Abba ya bi ɓera da sandarsa.]**, sannan a gabatar da mataki na biyu zuwa na huɗu (2-4) na sashen rubutu da jimlar.
3. A yi amfani da wannan labarin da tambayoyinsa a sashen Karatun Labari a Bayyane:

### Yarinya Mai Neman Ganyen Miya (2)

*Bayan iyayen yarinyar nan sun kasa **tayar** da ita. Sai aka yi shawarar gina mata **bukka** a wurin. Ashe kura na lura da lokacin da mahaifiyarta ke kawo mata abinci. Rannan kura ta zo ta yi muryar mahaifiyar yarinyar. Yarinya ta gane ba mahaifiyar ta ce ba. Ta ki **buɗewa**. Ta gaya wa mahaifiyarta. Mahaifiyar ta ce, 'dole in kula kar kura ta cinye mani `yata'. Kullum tana a bakin bukkar. Ashe tsohuwar nan aljana ce. Ta ji tausayin mahaifiyar Cindo. Sai ta ce, '`yarki ta yi mani rashin kunya, amma yanzu na haƙura, ki kama hannunta, ku tafi gida'.*

***Tambayoyi***

1. *Me aka yi shawarar a gina wa yarinyar nan?*
2. *Wa ke kawo wa yarinya abinci?*
3. *Me ya sa aljanar nan ta ji tausayin mahaifiyar Cindo?*

# Mako Na 3 Darasi Na 5

Haruffan da za a yi amfani da su: **[Ɓ ɓ, Fy fy]**
Gaɓoɓin kalmar da za a yi amfani da su: **[ɓa, ɓar, fya, ɓal, ɓe, fya]**
Kalmomin da za a yi amfani da su: **[ɓawo, fyace, ɓata, taɓarya, ɓalli, fyaɗe, ɓera, fyaɗu]**

Labarin da za a a yi amfani da shi:

**Katon ɓera a ɗakin Mama.**
**Abba ya sa sandarsa ya fyaɗe ɓera.**
**Ɓera ya fyaɗu sosai ya mutu.**
**Mama ta ji ɗaɗin fyaɗe ɓeran.**
**Abba ya jefar da ɓera a cikin shara.**

Tambayoyin da za a yi wa ɗalibai:

1. **Me Abba ya yi wa ɓera?**
2. **Daɗin me Mama ta ji?**

Gaɓoɓin da za a yi amfani da su a shifta: **[ƙura, tuƙa, ƙwai, ƙwarai, ƙusa, ƙwarya]**

1. Rubuta **[Ɓɓ, Fy fy]** a kan allo.
2. Zaɓi ɗalibai maza da mata, a ƙalla biyar, don su karanta haruffan da aka rubuta a kan allon.
3. Rubuta **[ɓa, ɓar, fya, ɓal, ɓe, fya]** a kan allo.
4. Zaɓi ɗalibai maza da mata, a ƙalla biyar, don su karanta gaɓoɓin kalmar da aka rubuta a kan allon.
5. Rubuta **[ɓawo, fyace, ɓata, taɓarya, ɓalli, fyaɗe, ɓera, fyaɗu]** a kan allo.
6. Zaɓi ɗalibai maza da mata, a ƙalla biyar, don su karanta kalmomin da aka rubuta a kan allon.
7. Rubuta a kan allo.

   **Katon ɓera a ɗakin Mama.**
   **Abba ya sa sandarsa ya fyaɗe ɓera.**
   **Ɓera ya fyaɗu sosai ya mutu.**
   **Mama ta ji ɗaɗin fyaɗe ɓeran.**
   **Abba ya jefar da ɓera a cikin shara.**

8. Zaɓi ɗalibai maza da mata, a ƙalla biyar, don su karanta labarin da aka rubuta a kan allon.
9. A yi wa kowane daga cikin ɗaliban da aka zaɓa tambayoyin auna fahimtar labarin da suka karanta kafin umurtar ɗalibi/ɗaliba na/ta gaba da ya/ta karanta labarin.
   1. **Me Abba ya yi wa ɓera?**
   2. **Daɗin me Mama ta ji?**
10. Zaɓi ɗalibai maza da mata, a ƙalla biyar, don su rubuta gaɓoɓin da za ka/ki karanto musu.
11. Kalmomin da za a karanto su ne **[ɓawo, fyace, ɓata, taɓarya, ɓalli, fyaɗe, ɓera, fyaɗu]**.
12. A auna sashen da ɗaliban suka fi rauni daga gwajin da aka gabatar.
13. Yayin da aka gano wuraren da yara suke da matsala, sai a yi ɗayan waɗannan:
    - Idan ma fi yawan ɗaliban ba su zo makaranta a kwanakin dasussan ba, ko kuma ba su fahimci darussan ba, to a koyar da cikakken darasi ɗaya na wannan makon.
    - Idan kuma ma fi yawan yara suna da rauni ne a wani sashi na darasi, sai a zaɓi sashen ƙarin ƙwarewa da yake da alaƙa da wannan sashen a koyar.

## Waƙa — minti 5

Waƙar da za a gabatar.

<u>Waƙar Gyara</u>

**'Yara mu gyara, muna ta gyarawa X 2**
**Karatu,**
**Muna ta gyarawa,**
**Rubutu,**
**Muna ta gyarawa,**
**Lissafi,**
**Muna ta gyarawa,**
**'Yara mu gyara, muna ta gyarawa x2**

M 1. Rera waƙar sau biyu, tare da kwaikwayon abin da ake faɗa a cikin waƙar.

MƊ 2. Maimaita mataki na ɗaya (1) tare da ɗalibai.

Ɗ 3. Umurci ɗalibai da su rera waƙar tare da kwaikwayon abin da ake faɗa a cikin waƙar.

## Amon sautin gaɓa — minti 3

Kalmomin da za a bambance: **[gyara, ƙyalli, kyale]**

M 1. Ka/ki ce: **[gyara]**. Idan akwai hoton kalmar ɗalibai su nuna a littafinsu.

2. Maimaita furta kalmar **[gyara]** tare da tafa amon sautin kowace gaɓa.

3. Nuna yawan gaɓoɓin kalmar da yatsun hannu.

MƊ 4. Maimaita mataki na biyu da na uku (2-3) tare da ɗalibai.

Ɗ 5. Umurci ɗalibai da su furta, su tafa, sannan su nuna yawan gaɓoɓin da ke cikin sauran kalmomin **[ƙyalli, kyale, gyale]**.

## Bambance Sautukan Gaɓoɓi — minti 3

Gaɓar da za a bambance: **[gya, kya]**

Kalmomin da za a bambance: **[damisa, gyatuma, gyarawa, ƙyanƙyami, samaniya]**

M 1. Ka/ki ce: Ina so a ɗaga babban yatsa sama idan aka ji sautin gaɓar **[gya ko kya]** a cikin kalmomin da zan faɗa. Idan kuma ba a ji sautin gaɓar **[gya ko kya]** ba sai a yi ƙasa da babban yatsa.

2. Ka/ki ce: Misali **[gyatuma]**.

3. Ka/ki ce: **[samaniya]**

MƊ 4. Ka/ki ce: To mu fara **[gyatuma]** (A jagoranci ɗalibai da su ɗaga babban yatsa sama).

5. Ka/ki ce: **[samaniya]** (A jagoranci ɗalibai da su yi ƙasa da babban yatsansu).

Ɗ 6. Umurci ɗalibai da su ɗaga babban yatsansu sama ko ƙasa yayin da kake/kike furta kalmomin: **[damisa, gyatuma, gyarawa, ƙyanƙyami, samaniya]**.

Mako Na 4 Darasi Na 1 da Na 2



Nana na kallon ƙyallin madubinta.
Nana ta goge madubinta da ƙyalle.
Kaka na gyara gyaɗar miya.
Kaka ta yi miyar gyaɗa da rama.
Nana da Kaka za su ci tuwo da miyar gyaɗa.

26

## Sunayen Haruffa — minti 5

Haruffan wannan darasi: **[Gy gy, Ky ƙy]**

M 1. Rubuta harafin **[Gy gy]** a kan allo.

2. Nuna harafin **[Gy gy]** ka/ki faɗi sunansa sau uku.

MƊ 3. Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashe mai alamar akwati.

4. Maimaita mataki na biyu (2) tare da umurtar ɗalibai da su nuna harafin a cikin littafinsu.

Ɗ 5. Umurci rukunan ɗalibai daban-daban da su karanta tare da nuna harafin **[Gy gy]** a cikin littafinsu.

M MƊ Ɗ 6. Maimaita matakin farko zuwa na biyar (1-5) da ɗaya harafin **[Ky ƙy]**.

MƊ 7. Umurci ɗalibai da su nuna harafin da za ka/ki furta a cikin littafinsu. (Yi ta furta haruffan **[Gy, Ky]** kana/kina sassauya su).

## Fahimtar Gaɓar Kalma — minti 5

Gaɓoɓin da za a karanta: **[gya, ƙya, ƙyal]**

M 1. Rubuta gaɓar **[gya]** a kan allo.

2. Nuna kowane harafi tare da furta sunansa.

3. Aza yatsa a ƙasan gaɓar ka/ki bi ta daga hagu zuwa dama kana/kina karanta ta.

MƊ 4. Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashe mai alamar da'ira.

5. Maimaita mataki na biyu da na uku (2-3) ta hanyar amfani da littafin ɗalibai.

Ɗ 6. Umurci ɗalibai da su karanta tare da nuna gaɓar kalmar **[gya]** a cikin littafinsu.

M MƊ Ɗ 7. Maimaita matakin farko zuwa na shida (1-6) da sauran gaɓoɓin kalma **[ƙya, ƙyal]**.

# Mako Na 4 Darasi Na 1 da Na 2

## ♥ Fahimtar Kalmomi ⏰ minti 5

Kalmomin da za a karanta: **[gyara, gyaɗa, ƙyalli, ƙyalle]**

M 1. Rubuta kalmar **[gyara]** a kan allo.
2. Nuna kowace gaɓa **[gya/ra]** cikin kalmar kana/kina karantawa a hankali.
3. Aza yatsa a ƙasan kalma **[gyara]** ka/ki karanta ta daga hagu zuwa dama da hanzari.

MƊ 4. Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashe mai alamar zuciya.
5. Maimaita mataki na biyu da na uku (2-3) ta hanyar amfani da littafin ɗalibai.

Ɗ 6. Umurci ɗalibai da su karanta tare da nuna kalmar [gyara] a cikin littafinsu.

M MƊ Ɗ 7. Maimaita matakin farko zuwa na shida (1-6) da sauran kalmomin **[gyaɗa, ƙyalli, ƙyalle]**.

## ★ Karatun Jimla ⏰ minti 5

M 1. Rubuta jimlar **[Kaka na gyara gyaɗar miya.]** a kan allo.
2. Karanta jimlar tare da aza yatsa a ƙasan kowace kalma, yayin karantawa.
3. Koya wa ɗalibai ma'anar kalmar **[gyara]** kamar yadda ta zo a cikin jimlar, ta hanyar amfani da sassan jiki, ko hotuna, ko wata hanya da za su fahimta.

MƊ 4. Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashe mai alamar tauraro.
5. Maimaita mataki na biyu (2) tare da ɗalibai ta hanyar amfani da littafin ɗalibai.
6. Tambayi ɗalibai ma'anar kalmar **[gyara]**, san-nan a sake yi musu bayani idan har ba su ba da amsa ba.


Ɗ 7. Umurci ɗalibai da su karanta jimlar, tare da nuna kalmomin da suke karantawa a littafinsu.
8. Tambayi ɗalibai ma'anar kalmar **[gyara]**.

## Karatun Labari ⏰ minti 15

M 1. Jagoranci ɗalibai su gano sunayen abubuwan da ke cikin hoton littafinsu. A tambaye su abin da suke tsammani zai faru dangane da hotunan.
2. Rubuta labarin a kan allo.

**Nana na kallon ƙyallin madubinta.**
**Nana ta goge madubinta da ƙyalle.**
**Kaka na gyara gyadar miya.**
**Kaka ta yi miyar gyaɗa da rama.**
**Nana da Kaka za su ci tuwo da miyar gyaɗa.**

3. Karanta labarin, kana/kina bi da yatsa a ƙasan kowace kalma.


Mako Na 4 Darasi Na 1 da Na 2

| | |
|---|---|
| ■ | Gy gy Ky ƙy |
| ● | gya ƙya ƙyal |
| ♥ | gyara gyaɗa ƙyalli ƙyalle |
| ★ | Kaka na gyara gyaɗar miya. |

gyara gyara
gyaɗa gyaɗa
ƙyalli ƙyalli

gyara gyara
gyaɗa gyaɗa
ƙyalli ƙyalli

27

4. Koya wa ɗalibai ma'anar kalmomi **[ƙyalli, goge, gyara]** kamar yadda suka zo a cikin labarin, ta hanyar amfani da sassan jiki, ko hotuna, ko wata hanya da za su fahimta.

MƊ 5. Maimaita mataki na uku (3) tare da umurtar ɗalibai da su nuna kalmomin a cikin littafinsu yayin da suke karantawa.
6. Tambayi ɗalibai ma'anar kalmomin **[ƙyalli, goge, gyara]**, sannan a sake yi musu bayani idan har ba su ba da amsa ba.

Ɗ 7. Umurci ɗalibai da su nuna kalmomin a cikin littafinsu yayin da suke karanta labarin a bayyane. A tabbatar suna karatun tare. Zagaya don taimaka wa ɗaliban da ke da buƙata a lokacin da suke karatun.
8. Tambayi ɗalibai ma'anar kalmomin **[ƙyalli, goge, gyara]**.

M 9. Auna fahimtar ɗalibai dangane da labarin, ta hanyar tambayoyi.
Umurci ɗalibai da su yi tunanin labarin da aka karanto kafin su ɗaga hannu.

**Tambayoyi**

1. **Me Nana ke yi?**
2. **Me Kaka ta yi?**

## Karatun Labari a Bayyane ⏰ minti 5

M 1. Karanta kan labari **[Labarin Kwaɗo Da Kunama (1)]**
2. Nuna hoto idan akwai shi.
3. Tambayi ɗalibai su yi hasashen abin da suke ganin zai faru a labarin.
4. Koyar da ma'anar sabbin kalmomi **[gaɓa, amince]** ta hanyar amfani da sassan jiki, ko hotuna, ko wata hanya da za su fahimta.
5. Umurci ɗalibai su gano kalmomin nan a lokacin da kake/kike karanta labarin, ta hanyar ɗaga babban yatsa sama a duk lokacin da suka ji an faɗi kalmomin.

6. Karanta labarin ta yadda zai jawo hankalin ɗalibai.

   *Wata rana, kunama na so ta tsallaka rafi, amma ba hanyar tsallakawa. Tana cikin tunanin yadda za ta yi, sai ga kwaɗo, sai ta tambaye shi ko zai tsallakar da ita. Kwaɗo ya ce, 'ina tsoron in ɗauke ki, ki harbi ni. Ta ce, 'haba mutumina! Kai da ka taimake ni. Idan na harbe ka ai tare za mu mutu'. Kwaɗo ya ce, 'ai kina iya bari sai mun tsallake, sannan ki harbe ni'. Ta ce haba abokina, 'idan na harbe ka a **gaɓa**, ka mutu, wa zai mayar da ni? Kwaɗo ya **amince**, ya daka tsalle da ita, sai cikin ruwa.*

7. Tambayi ɗalibai su koma kan hasashensu.
8. Yi wa ɗalibai tambayoyin da ke ƙasan labarin.

**Tambayoyi**

1. **Me kunama ke so kwaɗo ya yi mata?**
2. **Me kwaɗo ke jin tsoron kunama ta yi masa?**




## Rubutu

minti 19

Kalmomin da za a rubuta: **[gyara, gyaɗa, ƙyalli]**

M 1. Rubuta **[gyara]** a kan allo, a hankali tare da bayanin yadda kake/kike rubutun.

MƊ 2. Umurci ɗalibai da su tusa **[gyara]** da ke da ɗigo-ɗigo a littafinsu na karatu, yayin da kai/ke ma kake/kike tusawa a kan allo.

Ɗ 3. Umurci ɗalibai da su tusa **[gyara]** da ke da ɗigo-ɗigo, sannan su rubuta **[gyara]** a filin da aka tanada a littafinsu don rubutu a ɓangaren dama.

4. A duba yanayin zamansu, da yanayin riƙon fensiri da inda suke fara rubutun da kuma yadda suke rubutun.

M MƊ Ɗ 5. Maimaita matakin farko zuwa na huɗu (1-4) da sauran kalmomin **[gyaɗa, ƙyalli]**.

## Aikin Gida

1. Tuna wa ɗalibai su karanta darasin yau tare da iyayensu ko 'yan'uwa ko abokai.
2. Tuna wa ɗalibai su gwada rubutun da aka yi a aji a sashen da aka tanadar don yin hakan a littafinsu.

## Matashiya A Kan Darasi Na Biyu (2)

1. Tuna wa ɗalibai cewa za a maimaita darasin da ya gabata.
2. A sashen rubutu, a umurci ɗalibai daban-daban da su gano abinda ke cikin hoton da ke sashen rubutu a cikin littattafansu. Ka/ki karanta jimlar **[Kaka na gyara gyaɗa.]**, sannan a gabatar da mataki na biyu zuwa na huɗu (2-4) na sashen rubutu da jimlar.
3. A yi amfani da wannan labarin da tambayoyinsa a sashen Karatun Labari a Bayyane:

### Labarin Kwaɗo Da Kunama (2)

*Bayan kwaɗo ya shiga ruwa, sai kunama ta taɓa bayansa ta ji shi duk tsoka. Cikin ranta ta ce, 'ka ga ja`irin nan ya ƙoshi, bari in ɗan harbe shi in gani. Tana harbinshi, zafin ƙarinta ya ratsa ƙwaƙwalwarsa, take ya kayar da ita cikin ruwa. Shi kuwa ya daka tsalle sai bakin gaba. Ya yi sa'a ya hango **yakuwa**, da sauri ya isa ya ciri ganyen ya murza a bayansa. Nan take **radaɗin** zafin ya tafi. Ita kunama na can cikin ruwa tana ƙoƙarin fita, amma ta riga ta nutse. Shi kuwa kwaɗo ya ci gaba da harkokinsa.*

***Tambayoyi***

1. *Me kunama ta ce bayan ta taɓa bayan kwaɗo?*
2. *Me kwaɗo ya yi da kunama ta harbe shi?*
3. *Me ya sa kunama ke ƙoƙarin fita daga ruwa?*

# Mako Na 4 Darasi Na 3 da Na 4

## Waƙa

minti 5

Waƙar da za a gabatar.

**<u>Waƙar Gyara</u>**

**'Yara mu gyara, muna ta gyarawa X 2**
**Karatu,**
**Muna ta gyarawa,**
**Rubutu,**
**Muna ta gyarawa,**
**Lissafi,**
**Muna ta gyarawa,**
**'Yan yara mu gyara, muna ta gyarawa x2**

M 1. Rera waƙar sau biyu, tare da kwaikwayon abin da ake faɗa a cikin waƙar.

M'D 2. Maimaita mataki na ɗaya (1) tare da ɗalibai.

D 3. Umurci ɗalibai da su rera waƙar tare da kwaikwayon abin da ake faɗa a cikin waƙar.

## Amon sautin gaba

minti 3

Kalmomin da za a bambance: **[gyaɗa, gyangyaɗi, ƙyalle, ƙyaure]**

M 1. Ka/ki ce: **[gyaɗa]**. Idan akwai hoton kalmar ɗalibai su nuna a littafinsu.

2. Maimaita furta kalmar **[gyaɗa]** tare da tafa amon sautin kowace gaɓa.

3. Nuna yawan gaɓoɓin kalmar da yatsun hannu.

M'D 4. Maimaita mataki na biyu da na uku (2-3) tare da ɗalibai.

D 5. Umurci ɗalibai da su furta, su tafa, sannan su nuna yawan gaɓoɓin da ke cikin sauran kalmomin **[gyangyaɗi, ƙyalle, ƙyaure]**.

## Bambance Sautukan Gaɓobi

minti 3

Gaɓar da za a bambance: **[gya, ƙya]**

Kalmomin da za a bambance: **[gyara, ƙyafta, allo, ƙyashi, mota]**

M 1. Ka/ki ce: Ina so a ɗaga babban yatsa sama idan aka ji sautin gaɓar **[gya ko ƙya]** a cikin kalmomin da zan faɗa. Idan kuma ba a ji sautin gaɓar **[gya ko ƙya]** ba sai a yi ƙasa da babban yatsa.

2. Ka/ki ce: Misali **[ƙyafta]**.

3. Ka/ki ce: **[mota]**.

M'D 4. Ka/ki ce: To mu fara **[ƙyafta]** (A jagoranci ɗalibai da su ɗaga babban yatsa sama).

5. Ka/ki ce: **[mota]** (A jagoranci ɗalibai da su yi ƙasa da babban yatsansu).

D 6. Umurci ɗalibai da su ɗaga babban yatsansu sama ko ƙasa yayin da kake/kike furta kalmomin: **[gyara, kyafta, allo, ƙyashi, mota]**.

Mako Na 4 Darasi Na 3 da Na 4



Kaka da Abba sun hau jakin Kaka.
Za su gonar Kaka su shuka gyaɗa da wake.
Kaka na gyara gyaɗa da wake.
Sun ƙyale Nana a gida.
Nana na wanke gyale da ɗankwali.

30

## Sunayen Haruffa

minti 5

Haruffan wannan darasi: **[Gy gy, Ky ƙy]**

M 1. Rubuta harafin **[Gy gy]** a kan allo.

2. Nuna harafin **[Gy gy]** ka/ki faɗi sunansa sau uku.

M'D 3. Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashe mai alamar akwati.

4. Maimaita mataki na biyu (2) tare da umurtar ɗalibai da su nuna harafin a cikin littafinsu.

D 5. Umurci rukunan ɗalibai daban-daban da su karanta tare da nuna harafin **[Gy gy]** a cikin littafinsu.

M M'D D 6. Maimaita matakin farko zuwa na biyar (1-5) da ɗaya harafin **[Ky ƙy]**.

M'D 7. Umurci ɗalibai da su nuna harafin da za ka/ki furta a cikin littafansu. (Yi ta furta haruffan **[Gy, Ky]** kana/kina sassauyasu).

## Fahimtar Gaɓar Kalma

minti 5

Gaɓoɓin da za a karanta: **[gya, ƙyaf, gyar]**

M 1. Rubuta gaɓar **[gya]** a kan allo.

2. Nuna kowane harafi tare da furta sunansa.

3. Aza yatsa a ƙasan gaɓar ka/ki bi ta daga hagu zuwa dama kana/kina karanta ta.

M'D 4. Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashe mai alamar da'ira.

5. Maimaita mataki na biyu da na uku (2-3) ta hanyar amfani da littafin ɗalibai.

D 6. Umurci ɗalibai da su karanta tare da nuna gaɓar kalmar **[gya]** a cikin littafinsu.

M M'D D 7. Maimaita matakin farko zuwa na shida (1-6) da sauran gaɓoɓin kalma **[ƙyaf, gyar]**.

# Mako Na 4 Darasi Na 3 da Na 4

## ♥ Fahimtar Kalmomi ⏰ minti 5

Kalmomin da za a karanta: **[ƙyale, gyale, ƙyaftawa, gyartai]**

**M** 1. Rubuta kalmar **[ƙyale]** a kan allo.

2. Nuna kowace gaɓa **[ƙya/le]** cikin kalmar kana/kina karantawa a hankali.

3. Aza yatsa a ƙasan kalma **[ƙyale]** ka/ki karanta ta daga hagu zuwa dama da hanzari.

**M'D** 4. Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashe mai alamar zuciya.

5. Maimaita mataki na biyu da na uku (2-3) ta hanyar amfani da littafin ɗalibai.

**D** 6. Umurci ɗalibai da su karanta tare da nuna kalmar **[ƙyale]** a cikin littafinsu.

**M** **M'D** **D** 7. Maimaita matakin farko zuwa na shida (1-6) da sauran kalmomin **[gyale, ƙyaftawa, gyartai]**.

## ★ Karatun Jimla ⏰ minti 5

**M** 1. Rubuta jimlar **[Sun ƙyale Nana a gida.]** a kan allo.

2. Karanta jimlar tare da aza yatsa a ƙasan kowace kalma, yayin karantawa.

3. Koya wa ɗalibai ma'anar kalmar **[ƙyale]** kamar yadda ta zo a cikin jimlar, ta hanyar amfani da sassan jiki, ko hotuna, ko wata hanya da za su fahimta.

**M'D** 4. Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashe mai alamar tauraro.

5. Maimaita mataki na biyu (2) tare da ɗalibai ta hanyar amfani da littafin ɗalibai.

6. Tambayi ɗalibai ma'anar kalmar **[ƙyale]**, sannan a sake yi musu bayani idan har ba su ba da amsa ba.

**D** 7. Umurci ɗalibai da su karanta jimlar, tare da nuna kalmomin da suke karantawa a littafinsu.

8. Tambayi ɗalibai ma'anar kalmar **[ƙyale]**.

## Karatun Labari ⏰ minti 15


**M** 1. Jagoranci ɗalibai su gano sunayen abubuwan da ke cikin hoton littafinsu. A tambaye su abin da suke tsammani zai faru dangane da hotunan.

2. Rubuta labarin a kan allo.

**Kaka da Abba sun hau jakin Kaka.**
**Za su gonar Kaka su shuka gyaɗa da wake.**
**Kaka na gyara gyaɗa da wake.**
**Sun ƙyale Nana a gida.**
**Nana na wanke gyale da ɗankwali.**

3. Karanta labarin, kana/kina bi da yatsa a ƙasan kowace kalma.

4. Koya wa ɗalibai ma'anar kalmomi **[shuka, gyale]** kamar yadda suka zo a cikin labarin, ta


Mako Na 4 Darasi Na 3 da Na 4

| | |
|---|---|
| ■ | Gy gy Ky ƙy |
| ● | gya ƙyaf gyar |
| ♥ | ƙyale gyale ƙyaftawa gyartai |
| ★ | Sun ƙyale Nana a gida. |

ƙyale ƙyale
gyale gyale
ƙyaftawa ƙyaftawa

ƙyale ƙyale
gyale gyale
ƙyaftawa ƙyaftawa

31

hanyar amfani da sassan jiki, ko hotuna, ko wata hanya da za su fahimta.

**M'D** 5. Maimaita mataki na uku (3) tare da umurtar ɗalibai da su nuna kalmomin a cikin littafinsu yayin da suke karantawa.

6. Tambayi ɗalibai ma'anar kalmomin **[shuka, gyale]**, sannan a sake yi musu bayani idan har ba su ba da amsa ba.

**D** 7. Umurci ɗalibai da su nuna kalmomin a cikin littafinsu yayin da suke karanta labarin a bayyane. A tabbatar suna karatun tare. Zagaya don taimaka wa ɗaliban da ke da buƙata a lokacin da suke karatun.

8. Tambayi ɗalibai ma'anar kalmomin **[shuka, gyale]**.

**M** 9. Auna fahimtar ɗalibai dangane da labarin, ta hanyar tambayoyi.

Umurci ɗalibai da su yi tunanin labarin da aka karanto kafin su ɗaga hannu.

**Tambayoyi**

1. **Me Kaka da Abba za su shuka?**
2. **Me Nana ke yi?**

## Karatun Labari a Bayyane ⏰ minti 5

**M** 1. Karanta kan labari **[Labarin Wani Maciji Da Kwan Kaza (1)]**

2. Nuna hoto idan akwai shi.

3. Tambayi ɗalibai su yi hasashen abin da suke ganin zai faru a labarin.

4. Koyar da ma'anar sabbin kalmomi **[kiwo, haɗiye]** ta hanyar amfani da sassan jiki, ko hotuna, ko wata hanya da za su fahimta.

5. Umurci ɗalibai su gano kalmomin nan a lokacin da kake/kike karanta labarin, ta hanyar ɗaga babban yatsa sama a duk lokacin da suka ji an faɗi kalmomin.

6. Karanta labarin ta yadda zai jawo hankalin ɗalibai.

   *Wata rana kaza ta dawo daga* ***kiwo****, ta tarar an ɗaukar mata ƙwanta biyu. Nan take ta tafi kiran zakara. Kafin su dawo, maciji ya sake* ***haɗiye*** *ƙwai biyu. Zakara ya tambaye ta,"kwan guda nawa ne?" Ta ce goma ne, amma yanzu saura takwas. Zakara ya lissafa ƙwai shida. "Kin ko iya lissafi?" ya tambaye ta. Kaza ta ji haushin tambayar. Cikin fushi ta fara kirga ƙwanta; ɗaya, biyu, uku, huɗu, biyar, shida. "Tabbas ƙwaina guda takwas na bari kafin in kira ka". Kaza ta ƙwalla ihu, "zakara ka taimake ni, an sace mani ƙwai har guda huɗu!"*

7. Tambayi ɗalibai su koma kan hasashensu.
8. Yi wa ɗalibai tambayoyin da ke ƙasan labarin.

**Tambayoyi**

1. **Wa aka sace wa ƙwai?**
2. **Kwai nawa zakara ya ƙirga?**

## Rubutu

minti 19

Kalmomin da za a rubuta: **[ƙyale, gyale, ƙyaftawa]**

M 1. Rubuta **[ƙyale]** a kan allo, a hankali tare da bayanin yadda kake/kike rubutun.

MƊ 2. Umurci ɗalibai da su tusa **[ƙyale]** da ke da ɗigo-ɗigo a littafinsu na karatu, yayin da kai/ke ma kake/kike tusawa a kan allo.

Ɗ 3. Umurci ɗalibai da su tusa **[ƙyale]** da ke da ɗigo-ɗigo, sannan su rubuta **[ƙyale]** a filin da aka tanada a littafinsu don rubutu a ɓangaren dama.




4. A duba yanayin zamansu, da yanayin riƙon fensiri da inda suke fara rubutun da kuma yadda suke rubutun.

M MƊ Ɗ 5. Maimaita matakin farko zuwa na huɗu (1-4) da sauran kalmomin **[gyale, ƙyaftawa]**.

## Aikin Gida

1. Tuna wa ɗalibai su karanta darasin yau tare da iyayensu ko 'yan'uwa ko abokai.
2. Tuna wa ɗalibai su gwada rubutun da aka yi a aji a sashen da aka tanadar don yin hakan a littafinsu.

## Matashiya A Kan Darasi Na Huɗu (4)

1. Tuna wa ɗalibai cewa za a maimaita darasin da ya gabata.
2. A sashen rubutu, a umurci ɗalibai daban-daban da su gano abinda ke cikin hoton da ke sashen rubutu a cikin littattafansu. Ka/ki karanta jimlar **[Nana na wasa da gyare.]**, sannan a gabatar da mataki na biyu zuwa na huɗu (2-4) na sashen rubutu da jimlar.

3. A yi amfani da wannan labarin da tambayoyinsa a sashen Karatun Labari a Bayyane:

### *Labarin Wani Maciji Da Kwan Kaza (2)*

*Da kaza ta nemi taimakon zakara sai ya ce, "Mu rika sa ido". Maciji na nan na kula, da kaza ta fita sai ya zagaya ya haɗiyi ƙwai. Rannan da kaza ta dawo, sai ta iske saura ɗaya. Zakara ya shirya wata* ***dabara****. Da maciji ya sake dawowa, sai ya haɗiye kwan. Ya yi, ya yi, kwan ya fashe a cikinsa ya kasa. Kwan ya tare wa maciji hanyar numfashi. Saboda haka ya faɗi ya mutu. Kaza da zakara suka tarar da shi* ***matacce****, sai suka ce, 'Ai da ya san dafaffen ƙwai muka aje masa da bai haɗiye ba!"*

***Tambayoyi***

1. *Me zakara ya ce bayan kaza ta nemi taimakonsa?*
2. *Wane irin ƙwai kaza da zakara suka aje wa maciji?*
3. *Me ya sa ƙwan ya ki fashewa a cikin maciji?*

# Mako Na 4 Darasi Na 5

Haruffan da za a yi amfani da su: **[Gy gy, Ƙy ƙy]**
Gaɓoɓin kalmar da za a yi amfani da su: **[gya, ƙya, ƙyal, gya, ƙyaf, gyar]**
Kalmomin da za a yi amfani da su: **[gyara, gyaɗa, ƙyalli, ƙyalle, ƙyale, gyale, ƙyaftawa, gyartai]**
Labarin da za a a yi amfani da shi:

**Kaka da Abba sun hau jakin Kaka.**

**Za su gonar Kaka su shuka gyaɗa da wake.**

**Kaka na gyara gyaɗa da wake.**

**Sun ƙyale Nana a gida.**

**Nana na wanke gyale da ɗankwali.**

Tambayoyin da za a yi wa ɗalibai:

1. **Me Kaka da Abba za su shuka?**
2. **Me Nana ke yi?**

Kalmomin da za a yi amfani da su a shifta: **[ƙura, tuƙa, ƙwai, ƙwarai, ƙusa, ƙwarya]**

1. Rubuta **[Gy gy, Ƙy ƙy]** a kan allo.
2. Zaɓi ɗalibai maza da mata, a ƙalla biyar, don su karanta haruffan da aka rubuta a kan allon.
3. Rubuta **[gya, ƙya, ƙyal, gya, ƙyaf, gyar]** a kan allo.
4. Zaɓi ɗalibai maza da mata, a ƙalla biyar, don su karanta gaɓoɓin kalmar da aka rubuta a kan allon.
5. Rubuta **[gyara, gyaɗa, ƙyalli, ƙyalle, ƙyale, gyale, ƙyaftawa, gyartai]** a kan allo.
6. Zaɓi ɗalibai maza da mata, a ƙalla biyar, don su karanta kalmomin da aka rubuta a kan allon.
7. Rubuta a kan allo.

   **Kaka da Abba sun hau jakin Kaka.**
   **Za su gonar Kaka su shuka gyaɗa da wake.**
   **Kaka na gyara gyaɗa da wake.**
   **Sun ƙyale Nana a gida.**
   **Nana na wanke gyale da ɗankwali.**

8. Zaɓi ɗalibai maza da mata, a ƙalla biyar, don su karanta labarin da aka rubuta a kan allon.
9. A yi wa kowane daga cikin ɗaliban da aka zaɓa tambayoyin auna fahimtar labarin da suka karanta kafin umurtar ɗalibi/ɗaliba na/ta gaba da ya/ta karanta labarin.
   1. **Me Kaka da Abba za su shuka?**
   2. **Me Nana ke yi?**
10. Zaɓi ɗalibai maza da mata, a ƙalla biyar, don su rubuta gaɓoɓin da za ka/ki karanto musu.
11. Kalmomin da za a karanto su ne **[gyara, gyaɗa, ƙyalli, ƙyalle, ƙyale, gyale, ƙyaftawa, gyartai]**.
12. A auna sashen da ɗaliban suka fi rauni daga gwajin da aka gabatar.
13. Yayin da aka gano wuraren da yara suke da matsala, sai a yi ɗayan waɗannan:
    - Idan ma fi yawan ɗaliban ba su zo makaranta a kwanakin dasussan ba, ko kuma ba su fahimci darussan ba, to a koyar da cikakken darasi ɗaya na wannan makon.
    - Idan kuma ma fi yawan yara suna da rauni ne a wani sashi na darasi, sai a zaɓi sashen ƙarin ƙwarewa da yake da alaƙa da wannan sashen a koyar.

# Mako Na 5

1. Za a yi wa dukkanin ɗaliban ajin gwaji.
2. Za ka/ki zauna da ɗaliban ɗaya bayan ɗaya don yin gwajin.
3. Ka/ki fara gwajin ta hanyar ba ɗalibi/ɗaliba "Takardar Gwada Ɗalibai".
4. Umurci ɗalibin/ɗalibar da ya/ta fara karantu daga "Takardar Gwada Ɗalibai" yayin da kake/kike maka abinda yake/take karantawar a "Takardar Auna Fahimtar Ɗalibai" (Za a ga kwafin wannan takardar a shafi na 33 na wannan Jagoran Malamai).
    - Idan ɗalibi/ɗaliba ya/ta faɗa daidai, sai a maka (√) harafin ko gaɓar ko kalmar.
    - Idan kuma bai faɗa daidai ba sai a jawa harafin ko gaɓar ko kalmar layi (—).
    - A zagaye harafin ko gaɓar ko kalmar da aka ja wa layi idan har ɗalibin/ɗalibar ya/ta yi wa kansa/kanta gyara ya/ta faɗa daidai.
5. Idan ɗalibi/ɗaliba bai karanta inda ya ke ba bayan daƙiƙa 3, to sai a umurce shi/ta da ya/ta wuce zuwa ga abu na gaba a "Takardar Gwada Ɗalibai".
6. A ba ɗalibai bayan "Takardar Auna Fahimtar Ɗalibai" don rubuta haruffan da za a karanto musu.
7. Maimaita mataki na biyu zuwa na huɗu (2-4) da dukkanin ɗaliban ajin.
8. A duba sashen da ɗaliban suka fi rauni daga "Takardar Auna Fahimtar Ɗalibai" na gwajin da aka gabatar.

13. Yayin da aka gano wuraren da ɗalibai suke da matsala, sai a yi ɗayan waɗannan:
    - Idan ma fi yawan ɗaliban ba su zo makaranta a makwannin da suka gabata ba, ko kuma ba su fahimci darussan ba, to a maimaita koyar da wasu daga cikin darussan makwannin da suka gabata.
    - Idan kuma ma fi yawan ɗaliban suna da rauni ne a wani sashi na darasi, sai a zaɓi sashen ƙarin ƙwarewa da yake da alaƙa da wannan sashen a koyar.

# Zango Na 3 Mako Na 5

## Takardar Auna Fahimtar Ɗalibai

Adadin amsoshin da aka amsa daidai

**SunanƊalibi/Ɗaliba:**________________________

Sashe na 1. Haruffa

**ƙy ɓ Gw Kw gy K Kw fy**

---

Sashe na 2. Gaɓar Kalma

**ƙwa Fya kwai gwau ɓa**

---

Sashe na 3. Karatun Kalmomi

**gyaɗa gwaiba ɓera ƙura fyace**

---

Sashe na 4. Karatun Labari

**Katon ɓera a ɗakin Mama.**
**Abba ya sa sandarsa ya fyaɗe ɓera.**
**Ɓera ya fyaɗu sosai ya mutu.**
**Mama ta ji daɗin fyaɗe ɓeran.**
**Abba ya jefar da ɓera a cikin shara.**

---

Sashe na 5. Auna Fahimta

1. **Me Abba ya yi wa ɓera?**
2. **Daɗin me Mama ta ji?**

---

Sashe na 6. Shifta

**ƙwai kwando gyara ƙyale fyace**

---

**Sharhin Malami/Malama:**

# Mako Na 6 Darasi Na 1 da Na 2

## Waƙa (minti 5)

Waƙar da za a gabatar.

**<u>Waƙar Yara</u>**

**Yara yara, to,**
**'Yan makaranta, to,**
**Ku tafa, ku tafa, muna tafawa,**
**Gidan duniya, gidan ƙarya,**
**Gidan lahira, gidan gaskiya,**
**Yara yara, to,**
**'Yan makaranta, to,**
**Ku tafa, ku tafa, muna tafawa.**

M 1. Rera waƙar sau biyu, tare da kwaikwayon abin da ake faɗa a cikin waƙar.

MD 2. Maimaita mataki na ɗaya (1) tare da ɗalibai.

D 3. Umurci ɗalibai da su rera waƙar tare da kwaikwayon abin da ake faɗa a cikin waƙar.

## Amon sautin gaɓa (minti 3)

Kalmomin da za a bambance: **['ya'ya, 'yan'uwa, kyanwa, kyakkyawa]**

M 1. Ka/ki ce: **['ya'ya]**. Idan akwai hoton kalmar ɗalibai su nuna a littafinsu.
2. Maimaita furta kalmar **['ya'ya]** tare da tafa amon sautin kowace gaɓa.
3. Nuna yawan gaɓoɓin kalmar da yatsun hannu.

MD 4. Maimaita mataki na biyu da na uku (2-3) tare da ɗalibai.

D 5. Umurci ɗalibai da su furta, su tafa, sannan su nuna yawan gaɓoɓin da ke cikin sauran kalmomin **['yan'uwa, kyanwa, kyakkyawa]**.

## Bambance Sautukan Gaɓoɓi (minti 3)

Gaɓar da za a bambance: **[kya, 'ya]**

Kalmomin da za a bambance: **['yanci, ƙyaure, kyau, takalmi, 'yartsana]**

M 1. Ka/ki ce: Ina so a ɗaga babban yatsa sama idan aka ji sautin gaɓar **[kya ko 'ya]** a cikin kalmomin da zan faɗa. Idan kuma ba a ji sautin gaɓar **[kya ko 'ya]** ba sai a yi ƙasa da babban yatsa.
2. Ka/ki ce: Misali **['yartsana]**.
3. Ka/ki ce: **[ƙyaure]**

MD 4. Ka/ki ce: To mu fara **['yartsan]** (A jagoranci ɗalibai da su ɗaga babban yatsa sama).
5. Ka/ki ce: **[ƙyaure]** (A jagoranci ɗalibai da su yi ƙasa da babban yatsansu).

D 6. Umurci ɗalibai da su ɗaga babban yatsansu sama ko ƙasa yayin da kake/kike furta kalmomin **['yanci, ƙyaure, kyau, takalmi, 'yartsana]**.

Mako Na 6 Darasi Na 1 da Na 2



Nana na kiwon akuya da kaji.
Akuyar Nana ta haifi 'ya'ya guda biyu.
'Ya'yan akuyar Nana na da kyau.
'Ya'yan akuyar Nana mace da namiji ne.
Kowa ya ga kyan 'ya'yan akuyar Nana.

36

## Sunayen Haruffa (minti 5)

Haruffan wannan darasi: **[Ky ky 'Y 'y]**

M 1. Rubuta harafin **[Ky ky]** a kan allo.
2. Nuna harafin **[Ky ky]** ka/ki faɗi sunansa sau uku.

MD 3. Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashe mai alamar akwati.
4. Maimaita mataki na biyu (2) tare da umurtar ɗalibai da su nuna harafin a cikin littafinsu.

D 5. Umurci rukunan ɗalibai daban-daban da su karanta tare da nuna harafin **[Ky ky]** a cikin littafinsu.

M MD D 6. Maimaita matakin farko zuwa na biyar (1-5) da ɗaya harafin **['Y 'y]**.

MD 7. Umurci ɗalibai da su nuna harafin da za ka/ki furta a cikin littafinsu. (Yi ta furta haruffan **[Ky, 'Y]** kana/kina sassauya su).

## Fahimtar Gaɓar Kalma (minti 5)

Gaɓoɓin da za a karanta: **['ya, kyau, kya]**


M 1. Rubuta gaɓar **['ya]** a kan allo.
2. Nuna kowane harafi tare da furta sunansa.
3. Aza yatsa a ƙasan gaɓar ka/ki bi ta daga hagu zuwa dama kana/kina karanta ta.

MD 4. Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashe mai alamar da'ira.
5. Maimaita mataki na biyu da na uku (2-3) ta hanyar amfani da littafin ɗalibai.

D 6. Umurci ɗalibai da su karanta tare da nuna gaɓar kalmar **['ya]** a cikin littafinsu.

M MD D 7. Maimaita matakin farko zuwa na shida (1-6) da sauran gaɓoɓin kalma **[kyau, kya]**.

# Mako Na 6 Darasi Na 1 da Na 2


Mako Na 6 Darasi Na 1 da Na 2

■ Ky ky 'Y 'y

● 'ya kyau kya

♥ 'ya'ya kyau kyakkyawa 'yarsa

★ 'Ya'yan akuyar Nana na da kyau.

'ya'ya 'ya'ya
kyau kyau
kyakkyawa kyakkyawa

'ya'ya 'ya'ya
kyau kyau
kyakkyawa kyakkyawa

37

## ♥ Fahimtar Kalmomi ⏰ minti 5

Kalmomin da za a karanta: **[‘ya’ya, kyau, kyakkyawa, ‘yarsa]**

M 1. Rubuta kalmar **[‘ya’ya]** a kan allo.
2. Nuna kowace gaɓa **[‘ya/’ya]** cikin kalmar kana/kina karantawa a hankali.
3. Aza yatsa a ƙasan kalma **[‘ya’ya]** ka/ki karanta ta daga hagu zuwa dama da hanzari.

M'D 4. Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashe mai alamar zuciya.
5. Maimaita mataki na biyu da na uku (2-3) ta hanyar amfani da littafin ɗalibai.

D 6. Umurci ɗalibai da su karanta tare da nuna kalmar [**‘ya’ya]** a cikin littafinsu.

M M'D D 7. Maimaita matakin farko zuwa na shida (1-6) da sauran kalmomin **[kyau, kyakkyawa, ‘yarsa]**.

## ★ Karatun Jimla ⏰ minti 5

M 1. Rubuta jimlar **[‘Ya’yan akuyar Nana na da kyau.]** a kan allo.
2. Karanta jimlar tare da aza yatsa a ƙasan kowace kalma, yayin karantawa.
3. Koya wa ɗalibai ma’anar kalmar **[‘Ya’ya]** kamar yadda ta zo a cikin jimlar, ta hanyar amfani da sassan jiki, ko hotuna, ko wata hanya da za su fahimta.

M'D 4. Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashe mai alamar tauraro.
5. Maimaita mataki na biyu (2) tare da ɗalibai ta hanyar amfani da littafin ɗalibai.
6. Tambayi ɗalibai ma’anar kalmar **[‘Ya’ya]**, sannan a sake yi musu bayani idan har ba su ba da amsa ba.

D 7. Umurci ɗalibai da su karanta jimlar, tare da nuna kalmomin da suke karantawa a littafinsu.
8. Tambayi ɗalibai ma’anar kalmar **[‘Ya’ya]**.

## Karatun Labari ⏰ minti 15

M 1. Jagoranci ɗalibai su gano sunayen abubuwan da ke cikin hoton littafinsu. A tambaye su abin da suke tsammani zai faru dangane da hotunan.
2. Rubuta labarin a kan allo.

**Nana na kiwon akuya da kaji.**
**Akuyar Nana ta haifi ‘ya’ya guda biyu.**
**‘Ya’yan akuyar Nana na da kyau.**
**‘Ya’yan akuyar Nana mace da namiji ne.**
**Kowa ya ga kyan ‘ya’yan akuyar Nana.**

3. Karanta labarin, kana/kina bi da yatsa a ƙasan kowace kalma.
4. Koya wa ɗalibai ma’anar kalmomi **[kiwo, ‘ya’ya]** kamar yadda suka zo a cikin labarin, ta hanyar amfani da sassan jiki, ko hotuna, ko wata hanya da za su fahimta.

M'D 5. Maimaita mataki na uku (3) tare da umurtar ɗalibai da su nuna kalmomin a cikin littafinsu yayin da suke karantawa.
6. Tambayi ɗalibai ma’anar kalmomin **[kiwo, ‘ya’ya]**, sannan a sake yi musu bayani idan har ba su ba da amsa ba.

D 7. Umurci ɗalibai da su nuna kalmomin a cikin littafinsu yayin da suke karanta labarin a bayyane. A tabbatar suna karatun tare. Zagaya don taimaka wa ɗaliban da ke da buƙata a lokacin da suke karatun.
8. Tambayi ɗalibai ma’anar kalmomin **[kiwo, ‘ya’ya]**.

M 9. Auna fahimtar ɗalibai dangane da labarin, ta hanyar tambayoyi.

Umurci ɗalibai da su yi tunanin labarin, da aka karanto kafin su ɗaga hannu.

**Tambayoyi**

1. **‘Ya’ya nawa akuyar Nana ta haifa?**
2. **Da me da me akuyar Nana ta haifa?**

## Karatun Labari a Bayyane ⏰ minti 5

M 1. Karanta kan labari **[Attajiri da Waziri (1)]**
2. Nuna hoto idan akwai shi.
3. Tambayi ɗalibai su yi hasashen abin da suke ganin zai faru a labarin.
4. Koyar da ma’anar sabbin kalmomi **<u>[attajiri, waziri]</u>** ta hanyar amfani da sassan jiki, ko hotuna, ko wata hanya da za su fahimta.
5. Umurci ɗalibai su gano kalmomin nan a lokacin da kake/kike karanta labarin, ta hanyar ɗaga babban yatsa sama a duk lokacin da suka ji an faɗi kalmomin.

6. Karanta labarin ta yadda zai jawo hankalin ɗalibai.

   *A garin Barwa, an yi wani* ***__attajiri__****, mai taimakon mutane.* ***__Wazirin__*** *garin na jin haushinsa, har ma yana neman hanyar da zai wulaƙanta shi. Ga shi kuma, sarki na yarda da maganarsa. Rannan ya ce wa sarki a haɗa buhun gero da dawa da masara, a umurci attajirin ya raba su kafin wayewar gari. Ashe waziri bai sani ba, akwai wata bishiya a gidan attajirin. Cikin bishiyar akwai ramin tururuwa da maciji ciki. Kullum sai ya gaisa da su, ya ba su abinci. Sun nemi su rika yi masa hidima, amma ya ƙi, ya ce su ma halittu ne kamarsa.*

7. Tambayi ɗalibai su koma kan hasashensu.

8. Yi wa ɗalibai tambayoyin da ke ƙasan labarin.

**Tambayoyi**

1. **Wa ke jin haushin attajiri?**
2. **Me ke cikin kogon bishiya?**


## Rubutu

minti 19

Kalmomin da za a rubuta: **['ya'ya, kyau, kyakkyawa]**

(M) 1. Rubuta **['ya'ya]** a kan allo, a hankali tare da bayanin yadda kake/kike rubutun.

(M'D) 2. Umurci ɗalibai da su tusa **['ya'ya]** da ke da ɗigo-ɗigo a littafinsu na karatu, yayin da kai/ke ma kake/kike tusawa a kan allo.




('D) 3. Umurci ɗalibai da su tusa **['ya'ya]** da ke da ɗigo-ɗigo, sannan su rubuta **['ya'ya]** a filin da aka tanada a littafinsu don rubutu a ɓangaren dama.

4. A duba yanayin zamansu, da yanayin riƙon fensiri da inda suke fara rubutun da kuma yadda suke rubutun.

(M) (M'D) ('D) 5. Maimaita matakin farko zuwa na huɗu (1-4) da sauran kalmomin **[kyau, kyakkyawa]**.

## Aikin Gida

1. Tuna wa ɗalibai su karanta darasin yau tare da iyayensu ko 'yan'uwa ko abokai.
2. Tuna wa ɗalibai su gwada rubutun da aka yi a aji a sashen da aka tanadar don yin hakan a littafansu.

# Matashiya A Kan Darasi Na Biyu 2

1. Tuna wa ɗalibai cewa za a maimaita darasin da ya gabata.
2. A sashen rubutu, a umurci ɗalibai daban-daban da su gano abinda ke cikin hoton da ke sashen rubutu a cikin littattafansu. Ka/ki karanta jimlar **[Akuyar Nana na da 'ya'ya biyu.]**, sannan a gabatar da mataki na biyu zuwa na huɗu (2-4) na sashen rubutu da jimlar.
3. A yi amfani da wannan labarin da tambayoyinsa a sashen Karatun Labari a Bayyane:

## Attajiri da Waziri (2)

*Bayan sarki ya umurci* ***__dogarawa__*** *su aiwatar da abin da waziri ya faɗa. Attajiri ya zauna yana tunanin yadda zai yi. Sai ga tururuwa ta fito. Ganin attajiri cikin damuwa, ta tambaye shi, ya gaya mata. Da jin haka sai* ***__tururuwa__*** *ta gayyato `yan`uwanta suka taimaka wa attajiri. Waziri ya ji haushi, sai ya zuba guba a abincin sarki, ya kamu da rashin lafiya. Maciji ya taimaka wa attajiri da magani. Attajiri ya kai wa sarki magani, ya sha ya warke. Sarki ya gane attajiri mutumin kirki ne, sai ya daina yarda da maganar waziri.*

***Tambayoyi***

*1. Me waziri ya sa wa sarki a abinci?*
*2. Wa ya taimaka wa attajiri?*
*3. Me ya sa sarki ya dai na yarda da waziri?*

# Mako Na 6 Darasi Na 3 da Na 4

## Waƙa
minti 5

Waƙar da za a gabatar.

**<u>Waƙar Yara</u>**

**Yara yara, to,**
**'Yan makaranta, to,**
**Ku tafa, ku tafa, muna tafawa,**
**Gidan duniya, gidan ƙarya,**
**Gidan lahira, gidan gaskiya,**
**Yara yara, to,**
**'Yan makaranta, to,**
**Ku tafa, ku tafa, muna tafawa.**

M 1. Rera waƙar sau biyu, tare da kwaikwayon abin da ake faɗa a cikin waƙar.

MƊ 2. Maimaita mataki na ɗaya (1) tare da ɗalibai.

Ɗ 3. Umurci ɗalibai da su rera waƙar tare da kwaikwayon abin da ake faɗa a cikin waƙar.

## Amon sautin gaba
minti 3

Kalmomin da za a bambance: **[kyauta, kyawawa, 'yanci, 'yantarwa]**

M 1. Ka/ki ce: **[kyauta]**. Idan akwai hoton kalmar ɗalibai su nuna a littafinsu.
2. Maimaita furta kalmar **[kyauta]** tare da tafa amon sautin kowace gaɓa.
3. Nuna yawan gaɓoɓin kalmar da yatsun hannu.

MƊ 4. Maimaita mataki na biyu da na uku (2-3) tare da ɗalibai.

Ɗ 5. Umurci ɗalibai da su furta, su tafa, sannan su nuna yawan gaɓoɓin da ke cikin sauran kalmomin **[kyawawa, 'yanci, 'yantarwa]**.

## Bambance Sautukan Gaɓoɓi
minti 3

Gaɓar da za a bambance: **[kya, 'ya]**

Kalmomin da za a bambance: **[kyauta, kyau, 'ya, doki, gida]**

M 1. Ka/ki ce: Ina so a ɗaga babban yatsa sama idan aka ji sautin gaɓar **[kya ko 'ya]** a cikin kalmomin da zan faɗa. Idan kuma ba a ji sautin gaɓar **[kya ko 'ya]** ba sai a yi ƙasa da babban yatsa.
2. Ka/ki ce: Misali **[kyau]**.
3. Ka/ki ce: **[gida]**.

MƊ 4. Ka/ki ce: To mu fara **[kyau]** (A jagoranci ɗalibai da su ɗaga babban yatsa sama).
5. Ka/ki ce: **[gida]** (A jagoranci ɗalibai da su yi ƙasa da babban yatsansu).

Ɗ 6. Umurci ɗalibai da su ɗaga babban yatsansu sama ko ƙasa yayin da kake/kike furta kalmomin: **[kyauta, kyau, 'ya, doki, gida]**.


Mako Na 6 Darasi Na 3 da Na 4

Abba na da kyanwa fara tas.
Kyanwar Abba na da 'ya'ya da yawa.
Kyanwar Abba na fita yawo nemo abinci.
Amma 'ya'yanta ba su fita yawo.
Abba na son kyanwarsa sosai.

40

## Sunayen Haruffa
minti 5

Haruffan wannan darasi: **[Ky ky 'Y 'y]**

M 1. Rubuta harafin **[Ky ky]** a kan allo.
2. Nuna harafin **[Ky ky]** ka/ki faɗi sunansa sau uku.

MƊ 3. Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashe mai alamar akwati.
4. Maimaita mataki na biyu (2) tare da umurtar ɗalibai da su nuna harafin a cikin littafinsu.

Ɗ 5. Umurci rukunan ɗalibai daban-daban da su karanta tare da nuna harafin **[Ky ky]** a cikin littafinsu.

M MƊ Ɗ 6. Maimaita matakin farko zuwa na biyar (1-5) da ɗaya harafin **['Y 'y]**.

MƊ 7. Umurci ɗalibai da su nuna harafin da za ka/ki furta a cikin littafinsu. (Yi ta furta haruffan **[Ky, 'Y]** kana/kina sassauya su).

## Fahimtar Gaɓar Kalma
minti 5

Gaɓoɓin da za a karanta: **['yan, kyan, kyau]**

M 1. Rubuta gaɓar **['yan]** a kan allo.
2. Nuna kowane harafi tare da furta sunansa.
3. Aza yatsa a ƙasan gaɓar ka/ki bi ta daga hagu zuwa dama kana/kina karanta ta.

MƊ 4. Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashe mai alamar da'ira.
5. Maimaita mataki na biyu da na uku (2-3) ta hanyar amfani da littafin ɗalibai.

Ɗ 6. Umurci ɗalibai da su karanta tare da nuna gaɓar kalmar **['yan]** a cikin littafinsu.

M MƊ Ɗ 7. Maimaita matakin farko zuwa na shida (1-6) da sauran gaɓoɓin kalma **[kyan, kyau]**.

# Mako Na 6 Darasi Na 3 da Na 4

## Fahimtar Kalmomi

minti 5

Kalmomin da za a karanta: [**‘yan’uwa, kyanwa, ‘yanci, kyauta]**

(M) 1. Rubuta kalmar **[‘yan’uwa]** a kan allo.

2. Nuna kowace gaɓa **[‘yan/’uwa]** cikin kalmar kana/kina karantawa a hankali.

3. Aza yatsa a ƙasan kalma **[‘yan’uwa]** ka/ki karanta ta daga hagu zuwa dama da hanzari.

(MD) 4. Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashe mai alamar zuciya.

5. Maimaita mataki na biyu da na uku (2-3) ta hanyar amfani da littafin ɗalibai.

(D) 6. Umurci ɗalibai da su karanta tare da nuna kalmar **[‘yan’uwa]** a cikin littafinsu.

(M) (MD) (D) 7. Maimaita matakin farko zuwa na shida (1-6) da sauran kalmomin **[kyanwa, ‘yanci, kyauta]**.

## Karatun Jimla

minti 5

(M) 1. Rubuta jimlar **[Kyanwar Abba na da ‘ya’ya da yawa.]** a kan allo.

2. Karanta jimlar tare da aza yatsa a ƙasan kowace kalma, yayin karantawa.

3. Koya wa ɗalibai ma’anar kalmar **[kyanwar]** kamar yadda ta zo a cikin jimlar, ta hanyar amfani da sassan jiki, ko hotuna, ko wata hanya da za su fahimta.

(MD) 4. Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashe mai alamar tauraro.

5. Maimaita mataki na biyu (2) tare da ɗalibai ta hanyar amfani da littafin ɗalibai.

6. Tambayi ɗalibai ma’anar kalmar **[kyanwar]**, sannan a sake yi musu bayani idan har ba su ba da amsa ba.

(D) 7. Umurci ɗalibai da su karanta jimlar, tare da nuna kalmomin da suke karantawa a littafinsu.

8. Tambayi ɗalibai ma’anar kalmar **[kyanwar]**.

## Karatun Labari

minti 15

(M) 1. Jagoranci ɗalibai su gano sunayen abubuwan da ke cikin hoton littafinsu. A tambaye su abin da suke tsammani zai faru dangane da hotunan.

2. Rubuta labarin a kan allo.


**Abba na da kyanwa fara tas.**

**Kyanwar Abba na da ‘ya’ya da yawa.**

**Kyanwar Abba na fita yawo nemo abinci.**

**Amma ‘ya’yanta ba su fita yawo.**

**Abba na son kyanwarsa sosai.**



Mako Na 6 Darasi Na 3 da Na 4

Ky ky ‘Y ‘y

‘yan kyan kyau

‘yan’uwa kyanwa ‘yanci kyauta

kyanwar Abba na da ‘ya’ya da yawa.

yanci yanci

kyanwa kyanwa

yan’uwa ‘yan’uwa

yanci yanci

kyanwa kyanwa

yan’uwa ‘yan’uwa

41

3. Karanta labarin, kana/kina bi da yatsa a ƙasan kowace kalma.

4. Koya wa ɗalibai ma’anar kalmomi **[tas, kyanwa, nemo]** kamar yadda suka zo a cikin labarin, ta hanyar amfani da sassan jiki, ko hotuna, ko wata hanya da za su fahimta.

(MD) 5. Maimaita mataki na uku (3) tare da umurtar ɗalibai da su nuna kalmomin a cikin littafinsu yayin da suke karantawa.

6. Tambayi ɗalibai ma’anar kalmomin **[tas, kyanwa, nemo]**, sannan a sake yi musu bayani idan har ba su ba da amsa ba.

(D) 7. Umurci ɗalibai da su nuna kalmomin a cikin littafinsu yayin da suke karanta labarin a bayyane. A tabbatar suna karatun tare. Zagaya don taimaka wa ɗaliban da ke da buƙata a lokacin da suke karatun.

8. Tambayi ɗalibai ma’anar kalmomin **[tas, kyanwa, nemo]**.

(M) 9. Auna fahimtar ɗalibai dangane da labarin, ta hanyar tambayoyi.

Umurci ɗalibai da su yi tunanin labarin da aka karanto kafin su ɗaga hannu.

**Tambayoyi**

1. **Kyanwar Abba wace kala ce?**
2. **Me Abba ya ke so sosai?**

## Karatun Labari a Bayyane

minti 5

(M) 1. Karanta kan labari **[Gizo Mai Dubara (1)]**

2. Nuna hoto idan akwai shi.

3. Tambayi ɗalibai su yi hasashen abin da suke ganin zai faru a labarin.

4. Koyar da ma’anar sabbin kalmomi **[kwaɗayi, gayyaci]** ta hanyar amfani da sassan jiki, ko hotuna, ko wata hanya da za su fahimta.

5. Umurci ɗalibai su gano kalmomin nan a lokacin da kake/kike karanta labarin, ta hanyar ɗaga babban yatsa sama a duk lokacin da suka ji an faɗi kalmomin.

6. Karanta labarin ta yadda zai jawo hankalin ɗalibai.

   *Wata rana gizo ya ji **kwaɗayin** cin nama, kuma ba shi da shi. Ya zauna yana tunani, sai wata dabara ta zo masa. Ya **gayyaci** namun daji da tsuntsaye zuwa gidansa wasa. Kaza ce ta fara zuwa gidan gizo, ya nuna mata wani ɗaki ya ce ta shiga. Sai ga muzuru, shi ma ya shiga ɗakin, da shigarsa, ya cinye kaza.Ana haka sai ga kare ya shiga, shi ma ya gama da muzuru. Bayan kare ya gama da muzuru sai ga kura.*

7. Tambayi ɗalibai su koma kan hasashensu.

8. Yi wa ɗalibai tambayoyin da ke ƙasan labarin.

**Tambayoyi**

1. **Wa ya gayyaci namun daji da tsuntsaye zuwa gidansa?**
2. **Wa ya cinye kaza?**


## Rubutu

minti 19

Kalmomin da za a rubuta: **[ʻyanci, kyanwa, ʻyan'uwa]**

M 1. Rubuta **[ʻyanci]** a kan allo, a hankali tare da bayanin yadda kake/kike rubutun.

MƊ 2. Umurci ɗalibai da su tusa **[ʻyanci]** da ke da ɗigo-ɗigo a littafinsu na karatu, yayin da kai/ke ma kake/kike tusawa a kan allo.




Ɗ 3. Umurci ɗalibai da su tusa **[ʻyanci]** da ke da ɗigo-ɗigo, sannan su rubuta **[ʻyanci]** a filin da aka tanada a littafinsu don rubutu a ɓangaren dama.

4. A duba yanayin zamansu, da yanayin riƙon fensiri da inda suke fara rubutun da kuma yadda suke rubutun.

M MƊ Ɗ 5. Maimaita matakin farko zuwa na huɗu (1-4) da sauran kalmomin **[kyanwa, ʻyan'uwa]**.

## Aikin Gida

1. Tuna wa ɗalibai su karanta darasin yau tare da iyayensu ko ʻyan'uwa ko abokai.
2. Tuna wa ɗalibai su gwada rubutun da aka yi a aji a sashen da aka tanadar don yin hakan a littafansu.

## Matashiya A Kan Darasi Na Huɗu (4)

1. Tuna wa ɗalibai cewa za a maimaita darasin da ya gabata.
2. A sashen rubutu, a umurci ɗalibai daban-daban da su gano abinda ke cikin hoton da ke sashen rubutu a cikin littattafansu. Ka/ki karanta jimlar **[Kyanwa na da ʻya'ya da yawa.]**, sannan a gabatar da mataki na biyu zuwa na huɗu (2-4) na sashen rubutu da jimlar.
3. A yi amfani da wannan labarin da tambayoyinsa a sashen Karatun Labari a Bayyane:

### Gizo Mai Dubara (2)

*Bayan kura ta shiga, ta tarar da kare shi ma ta cinye shi. Kura na cikin cin ƙashi sai kwatsam ga zaki, ya shiga ya cinye kura. Sai ga giwa da damisa, su ma ya nuna masu ɗakin nan, suna shiga suka hau faɗa. Giwa na ganin haka, sai ta fito ta yi tafiyarta. Gizo na ganin faɗa ya **rincabe** tsakanin damisa da zaki, sai ya ɗebo **barkono** ya watsa masu a ido. Faɗa ya ƙi ƙarewa, daga ƙarshe suka karkarshe junansu. Gizo ya kwashi nama ya kai gida, aka soya masa ya ci, ya ƙoshi har ya ajiye saura.*

***Tambayoyi***

*1. Su wa gizo ya hango?*
*2. Wa ya kwashe nama?*
*3. Me ya sa zaki ya cinye kura?*

# Mako Na 6 Darasi Na 5

Haruffan da za a yi amfani da su: **[Ky ky ‘Y ‘y]**
Gaɓoɓin kalmar da za a yi amfani da su: **[‘ya, kyau, kya, ‘yan, kyan, kyau]**
Kalmomin da za a yi amfani da su: **[‘ya’ya, kyau, kyakkyawa, ‘yarsa, ‘yan’uwa, kyanwa, ‘yanci, kyauta]**
Labarin da za a a yi amfani da shi:

**Nana na kiwon akuya da kaji.**

**Akuyar Nana ta haifi ‘ya’ya guda biyu.**

**‘Ya’yan akuyar Nana na da kyau.**

**‘Ya’yan akuyar Nana mace da namiji ne.**

**Kowa ya ga kyan ‘ya’yan akuyar Nana.**

Tambayoyin da za a yi wa ɗalibai:

1. **‘Ya’ya nawa akuyar Nana ta haifa?**
2. **Da me da me akuyar Nana ta haifa?**

Gaɓoɓin da za a yi amfani da su a shifta: **[ƙura, tuƙa, ƙwai, ƙwarai, ƙusa, ƙwarya]**

1. Rubuta **[Ky ky ‘Y ‘y]** a kan allo.
2. Zaɓi ɗalibai maza da mata, a ƙalla biyar, don su karanta haruffan da aka rubuta a kan allon.
3. Rubuta **[‘ya, kyau, kya, ‘yan, kyan, kyau]** a kan allo.
4. Zaɓi ɗalibai maza da mata, a ƙalla biyar, don su karanta gaɓoɓin kalmar da aka rubuta a kan allon.
5. Rubuta **[‘ya’ya, kyau, kyakkyawa, ‘yarsa, ‘yan’uwa, kyanwa, ‘yanci, kyauta]** a kan allo.
6. Zaɓi ɗalibai maza da mata, a ƙalla biyar, don su karanta kalmomin da aka rubuta a kan allon.
7. Rubuta a kan allo.

    **Abba da Ali suna hutawa.**
    **Abba ya sa sabuwar hula.**
    **Ali na son hular Abba.**
    **Ali zai cire hular Abba.**
    **Abba ya ture hannun Ali.**

8. Zaɓi ɗalibai maza da mata, a ƙalla biyar, don su karanta labarin da aka rubuta a kan allon.
9. A yi wa kowane daga cikin ɗaliban da aka zaɓa tambayoyin auna fahimtar labarin da suka karanta kafin umurtar ɗalibi/ɗaliba na/ta gaba da ya/ta karanta labarin.

    1. **‘Ya’ya nawa akuyar Nana ta haifa?**
    2. **Da me da me akuyar Nana ta haifa?**

10. Zaɓi ɗalibai maza da mata, a ƙalla biyar, don su rubuta gaɓoɓin da za ka/ki karanto musu.
11. Kalmomin da za a karanto su ne **[‘ya’ya, kyau, kyakkyawa, ‘yarsa, ‘yan’uwa, kyanwa, ‘yanci, kyauta]**.
12. A auna sashen da ɗaliban suka fi rauni daga gwajin da aka gabatar.
13. Yayin da aka gano wuraren da yara suke da matsala, sai a yi ɗayan waɗannan:

    - Idan ma fi yawan ɗaliban ba su zo makaranta a kwanakin dasussan ba, ko kuma ba su fahimci darussan ba, to a koyar da cikakken darasi ɗaya na wannan makon.
    - Idan kuma ma fi yawan yara suna da rauni ne a wani sashi na darasi, sai a zaɓi sashen ƙarin ƙwarewa da yake da alaƙa da wannan sashen a koyar.

# Mako Na 7 Darasi Na 1 da Na 2

## Waƙa

⏰ minti 5

Waƙar da za a gabatar.

**Waƙar Kirge 1**

**Ɗaya, mafarin ƙirge,**
**Biyu, idanun dabba,**
**Uku, duwatsun murhu,**
**Huɗu, ƙafafun tebur,**
**Biyar, na yatsun hannu.**

Ⓜ 1. Rera waƙar sau biyu, tare da kwaikwayon abin da ake faɗa a cikin waƙar.

ⓂⒹ 2. Maimaita mataki na ɗaya (1) tare da ɗalibai.

Ⓓ 3. Umurci ɗalibai da su rera waƙar tare da kwaikwayon abin da ake faɗa a cikin waƙar.

## Karatun Labari

⏰ minti 15

Ⓜ 1. Jagoranci ɗalibai su gano sunayen abubuwan da ke cikin hoton littafinsu. A tambaye su abin da suke tsammani zai faru dangane da hotunan.

2. Rubuta labarin a kan allo.

**Ga Kaka da jakinsa a hanyar kasuwa.**
**Ya jera damin dawa a bayan jakinsa.**
**Zai je kasuwa ya sayar da dawa.**
**Jaki ya kama hanya a guje.**
**Kaka yana bin jaki a baya.**
**Kaka ya kamo jakinsa**.

3. Karanta labarin, kana/kina bi da yatsa a ƙasan kowace kalma.

4. Koya wa ɗalibai ma'anar kalmomi **[dami, kamo]** kamar yadda suka zo a cikin labarin, ta hanyar amfani da sassan jiki, ko hotuna, ko wata hanya da za su fahimta.

ⓂⒹ 5. Maimaita mataki na uku (3) tare da umurtar ɗalibai da su nuna kalmomin a cikin littafinsu yayin da suke karantawa.

6. Tambayi ɗalibai ma'anar kalmomin **[dami, kamo]**, sannan a sake yi musu bayani idan har ba su ba da amsa ba.

Ⓓ 7. Umurci ɗalibai da su nuna kalmomin a cikin littafinsu yayin da suke karanta labarin a bayyane. A tabbatar suna karatun tare. Zagaya don taimaka wa ɗaliban da ke da buƙata a lokacin da suke karatun.

8. Tambayi ɗalibai ma'anar kalmomin **[dami, kamo]**.

Ⓜ 9. Auna fahimtar ɗalibai dangane da labarin, ta hanyar tambayoyi.

Umurci ɗalibai da su yi tunanin labarin da aka karanto kafin su ɗaga hannu.


Mako Na 7 Darasi Na 1 da Na 2

Ga Kaka da jakinsa a hanyar kasuwa.
Ya jera damin dawa a bayan jakinsa.
Zai je kasuwa ya sayar da dawa.
Jaki ya kama hanya a guje.
Kaka yana bin jaki a baya.
Kaka ya kamo jakinsa.

44

**Tambayoyi**

1. **Me Kaka ya ɗora a bayan jakinsa?**
2. **Wa ke bin jaki a baya?**

## Karatun Labari a Bayyane

⏰ minti 5

Ⓜ 1. Karanta kan labari **[Labarin Namadi da Tururuwa (1)]**

2. Nuna hoto idan akwai shi.

3. Tambayi ɗalibai su yi hasashen abin da suke ganin zai faru a labarin.

4. Koyar da ma'anar sabbin kalmomi **[raggo, zama]** ta hanyar amfani da sassan jiki, ko hotuna, ko wata hanya da za su fahimta.

5. Umurci ɗalibai su gano kalmomin nan a lokacin da kake/kike karanta labarin, ta hanyar ɗaga babban yatsa sama a duk lokacin da suka ji an faɗi kalmomin.

6. Karanta labarin ta yadda zai jawo hankalin ɗalibai.

*A garin Murwi, an yi wani yaro mai suna Namadi, yaro ne* ***raggo****. Wata rana mahaifinsa ya kwanta rashin lafiya. Mahaifin ya ce, 'rashin lafiyar nan ba mai warkewa ce ba. Idan na bar duniya, ka je wajen tururuwa ta koya maka* ***zaman*** *duniya'. Bayan kwana biyu mahaifinsa ya rasu. Ya tuna da maganar mahaifinsa. Ya fita bayan gari. Ya ga tururuwa, ya tsaya yana kallonta tana aiki. Ya nemi ganin babba daga cikinsu, bayan wani lokaci, sai ga wata tururuwa ta fito, da alama tsohuwa ce a cikinsu. Namadi ya gaya mata labarinsa da abin da mahaifinsa ya gaya masa.*

7. Tambayi ɗalibai su koma kan hasashensu.

8. Yi wa ɗalibai tambayoyin da ke ƙasan labarin.

**Tambayoyi**

1. **Wane sako mahaifin Namadi ya bar masa?**
2. **Wa Namadi ya gaya wa labarinsa**?

# Mako Na 7 Darasi Na 1 da Na 2

## Rubutu

⏰ minti 19


Jimlar da za a rubuta: **[Ga jaki ɗauke da dawa a bayansa.]**

Ⓜ 1. Umurci ɗalibai daban-daban da su gano abinda ke cikin hoton da ke sashen rubutu a cikin littattafansu.

2. Ka/ki karanta jimlar **[Ga jaki ɗauke da dawa a bayansa.]**

Ⓓ 3. Umurci ɗalibai da su tusa **[Ga jaki ɗauke da dawa a bayansa.]** da ke da ɗigo-ɗigo, sannan su rubuta [**Ga jaki ɗauke da dawa a bayansa.]** a filin da aka tanada a littafinsu don rubutu.

5. A duba yanayin zamansu, da yanayin riƙon fensiri da inda suke fara rubutun da kuma yadda suke rubutun.




## Aikin Gida

1. Tuna wa ɗalibai su karanta darasin yau tare da iyayensu ko 'yan'uwa ko abokai.
2. Tuna wa ɗalibai su gwada rubutun da aka yi a aji a sashen da aka tanadar don yin hakan a littafansu.

## Matashiya A Kan Darasi Na Biyu (2)

1. Tuna wa ɗalibai cewa za a maimaita darasin da ya gabata.
2. A darasi na 2, a maimaita dukkan darasin amma a yi amfani da wannan labarin da tambayoyinsa a sashen Karatun Labari a Bayyane:

### Labarin Namadi da Tururuwa (2)

*Tururuwa ta ce, 'karatu na **bukatar** abubuwa guda shida: kaifin tunani, da kwaɗayin samun karatun, da hakurin neman karatun, da **guzurin** neman karatun, da daɗewa ana karatun, da malami'. Ya zauna wajensu tsawon shekara biyu. Da zai koma ta ce masa, 'waɗanne abubuwa ne ka koya?'. Ya ce, 'na koyi abubuwa biyar. Duk abin da za ka yi, ka yi shi da gaske. Komai na da lokacinsa, tsari na da amfani a rayuwa, ka kyautata wa tsaofaffi da kananan yara. Ka yi tanadi domin gobe'. Namadi ya canza tunaninsa, ya zama mai himma da kwazo da kuma taimakon mutane.*

***Tambayoyi***

*1. Abubuwa nawa karatu ke bukata?*

*2. Abubuwa nawa Namadi ya koya?*

*3. Me ya sa Namadi ya canza tunaninsa?*

## Waƙa

minti 5

Waƙar da za a gabatar.

**<u>Waƙar Kirge 1</u>**

**Ɗaya, mafarin ƙirge,**
**Biyu, idanun dabba,**
**Uku, duwatsun murhu,**
**Huɗu, ƙafafun tebur,**
**Biyar, na yatsun hannu.**

(M) 1. Rera waƙar sau biyu, tare da kwaikwayon abin da ake faɗa a cikin waƙar.

(MƊ) 2. Maimaita mataki na ɗaya (1) tare da ɗalibai.

(Ɗ) 3. Umurci ɗalibai da su rera waƙar tare da kwaikwayon abin da ake faɗa a cikin waƙar.

## Karatun Labari

minti 15

(M) 1. Jagoranci ɗalibai su gano sunayen abubuwan da ke cikin hoton littafinsu. A tambaye su abin da suke tsammani zai faru dangane da hotunan.

2. Rubuta labarin a kan allo.

**Nana ta je garin Ringimi a mota.**
**Baba ya wanke motarsa da ruwa.**
**Saboda motar ta yi ƙura sosai.**
**Mama da Nana za su je kasuwa.**
**Za su je kasuwa a motar Baba.**
**Za su sayo kaji da doya.**

3. Karanta labarin, kana/kina bi da yatsa a ƙasan kowace kalma.

4. Koya wa ɗalibai ma'anar kalmomi **[ƙura, sayo]** kamar yadda suka zo a cikin labarin, ta hanyar amfani da sassan jiki, ko hotuna, ko wata hanya da za su fahimta.

(MƊ) 5. Maimaita mataki na uku (3) tare da umurtar ɗalibai da su nuna kalmomin a cikin littafinsu yayin da suke karantawa.

6. Tambayi ɗalibai ma'anar kalmomin **[ƙura, sayo]**, sannan a sake yi musu bayani idan har ba su ba da amsa ba.

(Ɗ) 7. Umurci ɗalibai da su nuna kalmomin a cikin littafinsu yayin da suke karanta labarin a bayyane. A tabbatar suna karatun tare. Zagaya don taimaka wa ɗaliban da ke da buƙata a lokacin da suke karatun.

8. Tambayi ɗalibai ma'anar kalmomin **[ƙura, sayo]**.

(M) 9. Auna fahimtar ɗalibai dangane da labarin, ta hanyar tambayoyi.

Umurci ɗalibai da su yi tunanin labarin da aka karanto kafin su ɗaga hannu.


Mako Na 7 Darasi Na 3 da Na 4

Nana ta je garin Ringimi a mota.
Baba ya wanke motarsa da ruwa.
Saboda motar ta yi ƙura sosai.
Mama da Nana za su je kasuwa.
Za su je kasuwa a motar Baba.
Za su sayo kaji da doya.

49

**Tambayoyi**

1. **Me motar Baba ta yi?**
2. **Me Nana da Mama za su sayo?**

## Karatun Labari a Bayyane

minti 5

(M) 1. Karanta kan labari [**Labarin Gizo Da Dogo (1)]**
2. Nuna hoto idan akwai shi.
3. Tambayi ɗalibai su yi hasashen abin da suke ganin zai faru a labarin.
4. Koyar da ma'anar sabbin kalmomi **[rimi, shela, baɗi]** ta hanyar amfani da sassan jiki, ko hotuna, ko wata hanya da za su fahimta.
5. Umurci ɗalibai su gano kalmomin nan a lokacin da kake/kike karanta labarin, ta hanyar ɗaga babban yatsa sama a duk lokacin da suka ji an faɗi kalmomin.
6. Karanta labarin ta yadda zai jawo hankalin ɗalibai.

   *An yi wani mutum mai tsawon gaske, wanda ya fi kowa tsawo a lokacinsa. Ya ma fi bishiyar **<u>rimi</u>** tsawo. Ya shiga gari yana yawo da wata ƙatuwar saniya. Ya yi **<u>shela</u>**, 'wa zai karɓi saniyar nan, **<u>baɗi</u>** in na dawo ya taba tsakiyar kaina, in ya kasa in cinye shi'. Kowa ya ƙi, sai gizo ya karɓi saniya ya cinye abinsa. Bai ba kowa a garin ba. Da shekara ta zagayo sai mutumin nan ya dawo. Ya nufi gidan gizo. Ganin haka sai mutanen gari suka biyo shi, su ga yadda za ta kasance. Gizo kuma ya shiga tsoro.*
7. Tambayi ɗalibai su koma kan hasashensu.
8. Yi wa ɗalibai tambayoyin da ke ƙasan labarin.

**Tambayoyi**

1. **Wa ya shiga gari da ƙatuwar saniya?**
2. **Wa ya karɓi saniyar mutumin nan?**

## Rubutu

minti 19


Jimlar da za a rubuta: **[Baba na wanke mota.]**

M 1. Umurci ɗalibai ɗaban-ɗaban da su gano abinda ke cikin hoton da ke sashen rubutu a cikin littattafansu.

2. Ka/ki karanta jimlar **[Baba na wanke mota.]**

Ɗ 3. Umurci ɗalibai da su tusa **[Baba na wanke mota.]** da ke da ɗigo-ɗigo, sannan su rubuta **[Baba na wanke mota.]** a filin da aka tanada a littafinsu don rubutu.

4. A duba yanayin zamansu, da yanayin riƙon fensiri da inda suke fara rubutun da kuma yadda suke rubutun.




## Aikin Gida

1. Tuna wa ɗalibai su karanta darasin yau tare da iyayensu ko 'yan'uwa ko abokai.
2. Tuna wa ɗalibai su gwada rubutun da aka yi a aji a sashen da aka tanadar don yin hakan a littafansu.

## Matashiya A Kan Darasi Na Huɗu (4)

1. Tuna wa ɗalibai cewa za a maimaita darasin da ya gabata.
2. A darasi na 2, a maimaita dukkan darasin amma a yi amfani da wannan labarin da tambayoyinsa a sashen Karatun Labari a Bayyane:

### Labarin Gizo Da Dogo (2)

*Bayan gizo ya tsorata, sai wata dabara ta zo masa. Ya yi maza ya kwaɓa laka ya shiga ɗaki. Da mutumin ya iso gidansa, sai ya ce, 'gizo ina kake, yau alƙawalinmu ya cika?'. Gizo ya amsa, 'ina zuwa, **dakata** man kaɗan ina ɗinkin bango ne. Mutumin nan ya yi mamakin yadda ake ɗinkin bango, ya ce, 'ɗinkin bango kuma! Gizo ya ce, 'leko ka gani'. Ya **durƙusa** ya leƙa ɗakin. Gizo ya yi sauri ya taɓa tsakiyar kansa ya ce, 'Na taɓa! Na taɓa!'. Shi ke nan mutumin nan ya tafi cike da baƙin ciki.*

***Tambayoyi***

*1. Wace dabara gizo ya yi?*

*2. Wa ya taɓa tsakiyar kan dogon mutumin nan?*

*3. Me ya sa dogo ya duƙa, domin ya ga abin da gizo ke yi?*

Labarin da za a a yi amfani da shi:

**Nana ta je garin Ringimi a mota.**

**Baba ya wanke motarsa da ruwa.**

**Saboda motar ta yi ƙura sosai.**

**Mama da Nana za su je kasuwa.**

**Za su je kasuwa a motar Baba.**

**Za su sayo kaji da doya.**

Tambayoyin da za a yi wa ɗalibai:

1. **Me motar Baba ta yi?**
2. **Me Nana da Mama za su sayo?**

Jimlar da za a rubuta: ***[Baba na wanke mota.]***

1. Rubuta a kan allo.

   **Nana ta je garin Ringimi a mota.**

   **Baba ya wanke motarsa da ruwa.**

   **Saboda motar ta yi ƙura sosai.**

   **Mama da Nana za su je kasuwa.**

   **Za su je kasuwa a motar Baba.**

   **Za su sayo kaji da doya.**

2. Zaɓi ɗalibai maza da mata, a ƙalla biyar, don su karanta labarin da aka rubuta a kan allon.
3. A yi wa kowane daga cikin ɗaliban da aka zaɓa tambayoyin auna fahimtar labarin da suka karanta kafin umurtar ɗalibi/ɗaliba na/ta gaba da ya/ta karanta labarin.
   1. **Me motar Baba ta yi?**
   2. **Me Nana da Mama za su sayo?**
4. Rubuta ***[Baba na wanke mota.]*** a kan allo.
5. Zaɓi ɗalibai maza da mata, a ƙalla biyar, don su gwada rubuta jimlar a kan allo.
6. A auna sashen da ɗaliban suka fi rauni daga gwajin da aka gabatar.
7. Yayin da aka gano wuraren da yara suke da matsala, sai a yi ɗayan waɗannan:
   - Idan ma fi yawan ɗaliban ba su zo makaranta a kwanakin dasussan ba, ko kuma ba su fahimci darussan ba, to a koyar da cikakken darasi ɗaya na wannan makon.
   - Idan kuma ma fi yawan yara suna da rauni ne a wani sashi na darasi, sai a zaɓi sashen ƙarin ƙwarewa da yake da alaƙa da wannan sashen a koyar.

# Mako Na 8 Darasi Na 1 da Na 2

## Waƙa ⏰ minti 5

Waƙar da za a gabatar.

**<u>Waƙar Kirge 2</u>**

**Shida, ranakun aiki,**
**Bakwai, ranakun mako,**
**Takwas, goma ba biyu kenan,**
**Tara, daga ke sai goma,**
**Goma, biyar biyu kenan.**

(M) 1. Rera waƙar sau biyu, tare da kwaikwayon abin da ake faɗa a cikin waƙar.

(M'D) 2. Maimaita mataki na ɗaya (1) tare da ɗalibai.

(D) 3. Umurci ɗalibai da su rera waƙar tare da kwaikwayon abin da ake faɗa a cikin waƙar.

## Karatun Labari ⏰ minti 15

(M) 1. Jagoranci ɗalibai su gano sunayen abubuwan da ke cikin hoton littafinsu. A tambaye su abin da suke tsammani zai faru dangane da hotunan.

2. Rubuta labarin a kan allo.

**Ana buki a Bausa.**
**Mama da Baba da Abba za su je Bausa.**
**Baba yana tuƙa motarsa a hankali.**
**Sun haɗu da raƙumi a hanya.**
**Baba ya ce wa Abba ya kalli raƙumin.**
**Abba ya ji daɗin ganin raƙumi.**

3. Karanta labarin, kana/kina bi da yatsa a ƙasan kowace kalma.

4. Koya wa ɗalibai ma'anar kalmomi **[hankali, haɗu, kalli]** kamar yadda suka zo a cikin labarin, ta hanyar amfani da sassan jiki, ko hotuna, ko wata hanya da za su fahimta.

(M'D) 5. Maimaita mataki na uku (3) tare da umurtar ɗalibai da su nuna kalmomin a cikin littafinsu yayin da suke karantawa.

6. Tambayi ɗalibai ma'anar kalmomin **[hankali, haɗu, kalli]**, sannan a sake yi musu bayani idan har ba su ba da amsa ba.


(D) 7. Umurci ɗalibai da su nuna kalmomin a cikin littafinsu yayin da suke karanta labarin a bayyane. A tabbatar suna karatun tare. Zagaya don taimaka wa ɗaliban da ke da buƙata a lokacin da suke karatun.

8. Tambayi ɗalibai ma'anar kalmomin **[hankali, haɗu, kalli]**.

(M) 9. Auna fahimtar ɗalibai dangane da labarin, ta hanyar tambayoyi.

Umurci ɗalibai da su yi tunanin labarin da aka karanto kafin su ɗaga hannu.

Mako Na 8 Darasi Na 1 da Na 2



Ana buki a Bausa.
Mama da Baba da Abba za su je Bausa.
Baba yana tuƙa motarsa a hankali.
Sun haɗu da raƙumi a hanya.
Baba ya ce wa Abba ya kalli raƙumin.
Abba ya ji daɗin ganin raƙumi.

54

**Tambayoyi**

1. **Ina Mama da Baba za su je?**
2. **Me Abba ya ji daɗin gani?**

## Karatun Labari a Bayyane ⏰ minti 5

(M) 1. Karanta kan labari **[Darussan Da Dila Ya Koya (1)]**

2. Nuna hoto idan akwai shi.

3. Tambayi ɗalibai su yi hasashen abin da suke ganin zai faru a labarin.

4. Koyar da ma'anar sabbin kalmomi **[barance, taƙama, gulmar]** ta hanyar amfani da sassan jiki, ko hotuna, ko wata hanya da za su fahimta.

5. Umurci ɗalibai su gano kalmomin nan a lokacin da kake/kike karanta labarin, ta hanyar ɗaga babban yatsa sama a duk lokacin da suka ji an faɗi kalmomin.

6. Karanta labarin ta yadda zai jawo hankalin ɗalibai.

*Dila na **<u>barance</u>** a gidan sarki. Wata rana bayan ya gama aiki zai koma daji, sai ya ji sarki na yi wa yarima faɗa. Ya saurara, ya ji sarki na cewa, 'ka bi duniya sannu, mulkin da kake **<u>taƙama</u>** da shi, ɗayan biyu ne. Ko dai ka mutu ka bar shi, ko da ranka ya kubuce maka, ya tafi zuwa ga waninka. Kar kaa wulaƙanta ɗan`adam. Ɗan`adam daraje ke gare shi'. Ya wuce. Kafin ya fita waje, ya ji fadawa na **<u>gulmar</u>** yarima. Ashe wani tsoho ya sa aka buga, domin bai gaishe shi ba, a lokacin da yake shigewa.*

7. Tambayi ɗalibai su koma kan hasashensu.

8. Yi wa ɗalibai tambayoyin da ke ƙasan labarin.

**Tambayoyi**

1. **Wa ke barance gidan sarki?**
2. **Wa ya ce a daina wulaƙanta ɗan`adam?**

# Mako Na 8 Darasi Na 1 da Na 2

## Rubutu

minti 19

Jimlar da za a rubuta: **[Raƙumi na ɗauke da kaya.]**

(M) 1. Umurci ɗalibai daban-daban da su gano abinda ke cikin hoton da ke sashen rubutu a cikin littattafansu.

2. Ka/ki karanta jimlar **[Raƙumi na ɗauke da kaya.]**

(D) 3. Umurci ɗalibai da su tusa **[Raƙumi na ɗauke da kaya.]** da ke da ɗigo-ɗigo, sannan su rubuta **[Raƙumi na ɗauke da kaya.]** a filin da aka tanada a littafinsu don rubutu.

4. A duba yanayin zamansu, da yanayin riƙon fensiri da inda suke fara rubutun da kuma yadda suke rubutun.


Mako Na 8 Darasi Na 1 da Na 2

Raƙumi na ɗauke da kaya.

55

## Aikin Gida

1. Tuna wa ɗalibai su karanta darasin yau tare da iyayensu ko 'yan'uwa ko abokai.
2. Tuna wa ɗalibai su gwada rubutun da aka yi a aji a sashen da aka tanadar don yin hakan a littafansu.

## Matashiya A Kan Darasi Na Biyu (2)

1. Tuna wa ɗalibai cewa za a maimaita darasin da ya gabata.
2. A darasi na 2, a maimaita dukkan darasin amma a yi amfani da wannan labarin da tambayoyinsa a sashen Karatun Labari a Bayyane:

### Darussan da dila ya koya (2)

*Da dila ya isa ƙofar gida, ya ji wani tsohon doki yana cewa, 'komai lokaci ke gare shi. A da **bayi** biyar ke kula da ni. Mai ba ni abinci daban. Mai share wajen kwanciyata daban. Mai gyaran gashina daban. Mai **datse** mani **kofatona** daban. Mai fita da ni **kilisa** daban. Yau na wayi gari babu ko ɗaya. Cikin kashi nake kwana ciki nake tashi. Abinci sai an ga dama a bani'. Da isar dila daji, ya tara dabbobi ya ba su labarin abin da ya ji a gidan sarki. Dabbobin nan suka buɗe baki suka ce, 'duniya makaranta ce!'.*

***Tambayoyi***

1. *Wa dila ya ji yana magana da ya fito ƙofar gida?*
2. *Su wa dila ya tara da isarsa daji?*
3. *Me ya sa dabbobi suka ce duniya makaranta ce?*

## Waƙa
⏰ minti 5

Waƙar da za a gabatar.

**<u>Waƙar Kirge 2</u>**

**Shida, ranakun aiki,**
**Bakwai, ranakun mako,**
**Takwas, goma ba biyu kenan,**
**Tara, daga ke sai goma,**
**Goma, biyar biyu kenan.**

(M) 1. Rera waƙar sau biyu, tare da kwaikwayon abin da ake faɗa a cikin waƙar.

(M/D) 2. Maimaita mataki na ɗaya (1) tare da ɗalibai.

(D) 3. Umurci ɗalibai da su rera waƙar tare da kwaikwayon abin da ake faɗa a cikin waƙar.

## Karatun Labari
⏰ minti 15

(M) 1. Jagoranci ɗalibai su gano sunayen abubuwan da ke cikin hoton littafinsu. A tambaye su abin da suke tsammani zai faru dangane da hotunan.

2. Rubuta labarin a kan allo.

**Kaka da Nana za su je ƙauye.**
**Akwai rafi a hanyar ƙauyen.**
**Nana da Kaka sun shiga kwale-kwale.**
**Za a tsallakar da su rafi.**
**Nana na tsoron ruwa sosai.**
**Kaka ta ce ta rufe idonta.**
**Nana kuwa ta rufe idanunta.**

3. Karanta labarin, kana/kina bi da yatsa a ƙasan kowace kalma.

4. Koya wa ɗalibai ma'anar kalmomi **[rafi, kwale-kwale, tsallake]** kamar yadda suka zo a cikin labarin, ta hanyar amfani da sassan jiki, ko hotuna, ko wata hanya da za su fahimta.

(M/D) 5. Maimaita mataki na uku (3) tare da umurtar ɗalibai da su nuna kalmomin a cikin littafinsu yayin da suke karantawa.

6. Tambayi ɗalibai ma'anar kalmomin **[rafi, kwale-kwale, tsallake]**, sannan a sake yi musu bayani idan har ba su ba da amsa ba.

(D) 7. Umurci ɗalibai da su nuna kalmomin a cikin littafinsu yayin da suke karanta labarin a bayyane. A tabbatar suna karatun tare. Zagaya don taimaka wa ɗaliban da ke da buƙata a lokacin da suke karatun.

8. Tambayi ɗalibai ma'anar kalmomin **[rafi, kwale-kwale, tsallake]**.

(M) 9. Auna fahimtar ɗalibai dangane da labarin, ta hanyar tambayoyi.

Umurci ɗalibai da su yi tunanin labarin da aka karanto kafin su ɗaga hannu.

Mako Na 8 Darasi Na 3 da Na 4



Kaka da Nana za su je ƙauye.
Akwai rafi a hanyar ƙauyen.
Nana da Kaka sun shiga kwale-kwale.
Za a tsallakar da su rafi.
Nana na tsoron ruwa sosai.
Kaka ta ce ta rufe idonta.
Nana kuwa ta rufe idanunta.

59

**Tambayoyi**

1. **Ina su Nana za su je?**
2. **Me suka shiga?**

## Karatun Labari a Bayyane
⏰ minti 5

(M) 1. Karanta kan labari **[Labarin Wani Babban Malami (1)]**

2. Nuna hoto idan akwai shi.

3. Tambayi ɗalibai su yi hasashen abin da suke ganin zai faru a labarin.

4. Koyar da ma'anar sabbin kalmomi **[dukiya, yunwa, kwanciya]** ta hanyar amfani da sassan jiki, ko hotuna, ko wata hanya da za su fahimta.

5. Umurci ɗalibai su gano kalmomin nan a lokacin da kake/kike karanta labarin, ta hanyar ɗaga babban yatsa sama a duk lokacin da suka ji an faɗi kalmomin.

6. Karanta labarin ta yadda zai jawo hankalin ɗalibai.

*Wata rana wani babban sarki ya shirya kyauta, domin ya kai wa wani babban malami. Cikin kyautar akwai bayi biyu, da likitoci biyu waɗanda ya fi ji da su, da **<u>dukiya</u>** mai yawa. Da isarsu suka yi gaisuwa, suka faɗa wa malamin daga wurin da suke. Suka kawo kyauta suka ba malam. Ya dubi bayi, da likitoci, da dukiyar. Ya ce, 'ku gaya wa ubangidanku, na gode, amma ba mu da buƙatar likitocinsa. Dalili kuwa shi ne, ba mu cin abinci sai mun ji **<u>yunwa</u>**. Ba mu cika cikinmu, idan mun ci. Ba mu **<u>kwanciya</u>**, bayan mun ci.*

7. Tambayi ɗalibai su koma kan hasashensu.

8. Yi wa ɗalibai tambayoyin da ke ƙasan labarin.

**Tambayoyi**

1. **Wa ya shirya kyauta ga babban malami?**
2. **Likitoci nawa ne cikin kyautar da aka yi wa malam?**

## Rubutu

minti 19


Jimlar da za a rubuta: **[Nana na zaune a cikin kwale-kwale.]**

M 1. Umurci ɗalibai daban-daban da su gano abinda ke cikin hoton da ke sashen rubutu a cikin littattafansu.

2. Ka/ki karanta jimlar **[Nana na zaune a cikin kwale-kwale.]**

D 3. Umurci ɗalibai da su tusa **[Nana na zaune a cikin kwale-kwale.]** da ke da ɗigo-ɗigo, sannan su rubuta **[Nana na zaune a cikin kwale-kwale.]** a filin da aka tanada a littafinsu don rubutu.

4. A duba yanayin zamansu, da yanayin riƙon fensiri da inda suke fara rubutun da kuma yadda suke rubutun.




## Aikin Gida

1. Tuna wa ɗalibai su karanta darasin yau tare da iyayensu ko 'yan'uwa ko abokai.
2. Tuna wa ɗalibai su gwada rubutun da aka yi a aji a sashen da aka tanadar don yin hakan a littafansu.

## Matashiya A Kan Darasi Na Huɗu (4)

1. Tuna wa ɗalibai cewa za a maimaita darasin da ya gabata.
2. A darasi na 2, a maimaita dukkan darasin amma a yi amfani da wannan labarin da tambayoyinsa a sashen Karatun Labari a Bayyane:

### Labarin Wani Babban Malami (2)

*Malami ya ci gaba da cewa, 'dukiya kuma, idan ta yi yawa halaka ce, saboda haka ba mu da **buƙata**'. `Yan aike suka yi godiya suka koma. Ɗaya daga cikin likitocin nan, ya yi mamaki matuƙa dangane da maganar babban malami. Ya shiga bincike domin ya gano **alakar** rashin lafiya da cika ciki wurin cin abinci da kwanciya bayan cin abinci. Bayan shekara biyu ya gano cewa, mutum kan **daɗe** bai yi rashin lafiya ba **matuƙar** ba zai ci abinci ba sai ya ji yunwa, ba cika cikinsa idan ya ci abinci, ba ya kwanciya bayan cin abinci.*

***Tambayoyi***

*1. Me yawan dukiya yake kawo wa?*
*2. Wa ya yi mamakin maganar babban malamin?*
*3. Me ya sa likitan nan ya yi bincike a kan maganar malami?*

# Mako Na 8 Darasi Na 5

Labarin da za a a yi amfani da shi:

**Kaka da Nana za su je ƙauye.**

**Akwai rafi a hanyar ƙauyen.**

**Nana da Kaka sun shiga kwale-kwale.**

**Za a tsallakar da su rafi.**

**Nana na tsoron ruwa sosai.**

**Kaka ta ce ta rufe idonta.**

**Nana kuwa ta rufe idanunta.**

Tambayoyin da za a yi wa ɗalibai:

1. **Ina su Nana za su je?**
2. **Me suka shiga?**

Jimlar da za a rubuta: ***[Nana na zaune a cikin kwale-kwale.]***

1. Rubuta a kan allo.

   **Kaka da Nana za su je ƙauye.**

   **Akwai rafi a hanyar ƙauyen.**

   **Nana da Kaka sun shiga kwale-kwale.**

   **Za a tsallakar da su rafi.**

   **Nana na tsoron ruwa sosai.**

   **Kaka ta ce ta rufe idonta.**

   **Nana kuwa ta rufe idanunta.**

2. Zaɓi ɗalibai maza da mata, a ƙalla biyar, don su karanta labarin da aka rubuta a kan allon.
3. A yi wa kowane daga cikin ɗaliban da aka zaɓa tambayoyin auna fahimtar labarin da suka karanta kafin umurtar ɗalibi/ɗaliba na/ta gaba da ya/ta karanta labarin.
   1. **Ina su Nana za su je?**
   2. **Me suka shiga?**
4. Rubuta ***[Nana na zaune a cikin kwale-kwale]*** a kan allo.
5. Zaɓi ɗalibai maza da mata, a ƙalla biyar, don su gwada rubuta jimlar a kan allo.
6. A auna sashen da ɗaliban suka fi rauni daga gwajin da aka gabatar.
7. Yayin da aka gano wuraren da yara suke da matsala, sai a yi ɗayan waɗannan:
   - Idan ma fi yawan ɗaliban ba su zo makaranta a kwanakin dasussan ba, ko kuma ba su fahimci darussan ba, to a koyar da cikakken darasi ɗaya na wannan makon.
   - Idan kuma ma fi yawan yara suna da rauni ne a wani sashi na darasi, sai a zaɓi sashen ƙarin ƙwarewa da yake da alaƙa da wannan sashen a koyar.

## Waƙa

minti 5

Waƙar da za a gabatar.

**<u>Waƙar Ranakun Mako</u>**

**Lahadi, Litanin, Talata, Laraba,**
**Alhamis, Jumu'a, assabar ce ƙarshe,**
**Mu je makaranta,**
**Litanin, Talata, Laraba, Alhamis, Jumu'a**
**Assabar da Lahadi, kwanakin hutawa x 2**

M 1. Rera waƙar sau biyu, tare da kwaikwayon abin da ake faɗa a cikin waƙar.

M'D 2. Maimaita mataki na ɗaya (1) tare da ɗalibai.

D 3. Umurci ɗalibai da su rera waƙar tare da kwaikwayon abin da ake faɗa a cikin waƙar.

## Karatun Labari

minti 15

M 1. Jagoranci ɗalibai su gano sunayen abubuwan da ke cikin hoton littafinsu. A tambaye su abin da suke tsammani zai faru dangane da hotunan.

2. Rubuta labarin a kan allo.

**Ali da Abba da Nana na wasa a waje.**
**Sai ga jirgin sama zai wuce.**
**Abba ya ce su duba sama.**
**Sun kalli sama sai ga jirgi babba.**
**Sun ji daɗin ganin jirgin.**
**Sun bi jirgi da kallo har ya wuce.**

3. Karanta labarin, kana/kina bi da yatsa a ƙasan kowace kalma.

4. Koya wa ɗalibai ma'anar kalmomi **[duba, daɗi, wuce]** kamar yadda suka zo a cikin labarin, ta hanyar amfani da sassan jiki, ko hotuna, ko wata hanya da za su fahimta.

M'D 5. Maimaita mataki na uku (3) tare da umurtar ɗalibai da su nuna kalmomin a cikin littafinsu yayin da suke karantawa.

6. Tambayi ɗalibai ma'anar kalmomin **[duba, daɗi, wuce]**, sannan a sake yi musu bayani idan har ba su ba da amsa ba.

D 7. Umurci ɗalibai da su nuna kalmomin a cikin littafinsu yayin da suke karanta labarin a bayyane. A tabbatar suna karatun tare. Zagaya don taimaka wa ɗaliban da ke da buƙata a lokacin da suke karatun.

8. Tambayi ɗalibai ma'anar kalmomin **[duba, daɗi, wuce]**.

M 9. Auna fahimtar ɗalibai dangane da labarin, ta hanyar tambayoyi.

Umurci ɗalibai da su yi tunanin labarin da aka karanto kafin su ɗaga hannu.

Mako Na 9 Darasi Na 1 da Na 2



Ali da Abba da Nana na wasa a waje.
Sai ga jirgin sama zai wuce.
Abba ya ce su duba sama.
Sun kalli sama sai ga jirgi babba.
Sun ji daɗin ganin jirgin.
Sun bi jirgi da kallo har ya wuce.

64

**Tambayoyi**

1. **Me Abba ya gani a sama?**
2. **Wa ya kalli sama?**

## Karatun Labari a Bayyane

minti 5

M 1. Karanta kan labari **[Yan`mata Masu Kifi (1)]**

2. Nuna hoto idan akwai shi.

3. Tambayi ɗalibai su yi hasashen abin da suke ganin zai faru a labarin.

4. Koyar da ma'anar sabbin kalmomi **[kullum, Washegari, godiya]** ta hanyar amfani da sassan jiki, ko hotuna, ko wata hanya da za su fahimta.

5. Umurci ɗalibai su gano kalmomin nan a lokacin da kake/kike karanta labarin, ta hanyar ɗaga babban yatsa sama a duk lokacin da suka ji an faɗi kalmomin.

6. Karanta labarin ta yadda zai jawo hankalin ɗalibai.

*Wasu `yanmata a wani ƙauye kusa da bakin ruwa, **<u>kullum</u>** sukan tafi kamun kifi. Wata rana suka tafi kamun kifi. A hanyarsu ta dawowa, sai suka haɗu da wata tsohuwa ta roƙe su, su ba ta kifi. Duk suka ki ba ta, sai wata yarinya ɗaya a cikinsu mai suna Kumatu ta ba ta. **<u>Washegari</u>** da suka koma duk `yanmatan suka samo kifi mai yawa, sai dai Kumatu biyu kaɗai ta samo. Suka sake haɗuwa da tsohuwa. Kamar jiya, ta sake roƙonsu. Duk suka sake hana ta, sai Kumatu ce kawai ta ba ta. Tsohuwa ta yi **<u>godiya</u>**.*

7. Tambayi ɗalibai su koma kan hasashensu.

8. Yi wa ɗalibai tambayoyin da ke ƙasan labarin.

**Tambayoyi**

1. **Su wa suka haɗu da `yanmata a kan hanya?**
2. **Wace ce ta ba tsohuwa kifi?**

## Rubutu

minti 19

Jimlar da za a rubuta: **[Nana na nuna jirgin sama.]**

M 1. Umurci ɗalibai daban-daban da su gano abinda ke cikin hoton da ke sashen rubutu a cikin littattafansu.

2. Ka/ki karanta jimlar **[Nana na nuna jirgin sama.]**

D 3. Umurci ɗalibai da su tusa **[Nana na nuna jirgin sama.]** da ke da ɗigo-ɗigo, sannan su rubuta **[Nana na nuna jirgin sama.]** a filin da aka tanada a littafinsu don rubutu.

4. A duba yanayin zamansu, da yanayin riƙon fensiri da inda suke fara rubutun da kuma yadda suke rubutun.




## Aikin Gida

1. Tuna wa ɗalibai su karanta darasin yau tare da iyayensu ko 'yan'uwa ko abokai.
2. Tuna wa ɗalibai su gwada rubutun da aka yi a aji a sashen da aka tanadar don yin hakan a littafansu.

## Matashiya A Kan Darasi Na Biyu (2)

1. Tuna wa ɗalibai cewa za a maimaita darasin da ya gabata.
2. A darasi na 2, a maimaita dukkan darasin amma a yi amfani da wannan labarin da tambayoyinsa a sashen Karatun Labari a Bayyane:

### `Yan`mata Masu Kifi (2)

*Bayan `yan kwanaki, sarki ya sa aka yi shela duk **budurwar** da ta kamo kifi **ragon ruwa**, ta dafa mashi zai aure ta. `Yanmata suka **fantsama** neman kifi, amma ina! Ba su samu ba. Kumatu ta **makara**, ta kamo hanya, tana tafe sai ga tsohuwar da ta ba kifi. Ta gaya mata halin da ake ciki. Tsohuwa ta kwatanta mata wani gulbi. Tana isa ta kamo kifin. Ta koma gida, ta dafa ta kai wa sarki. Sarki ya yi farin-ciki ƙwarai, ya cika alƙawalinsa. Kwana bakwai aka yi ana shagalin bukinsa. Sauran `yanmatan kuwa tuni suka ciji yatsa!*

***Tambayoyi***

1. *Ya sunan kifin da sarki ke son a kamo masa?*
2. *Wace ce ta kamo kifi ragon ruwa?*
3. *Me ya sa tsohuwar nan ta nuna wa yarinya inda za ta samo ragon ruwa?*

## Waƙa

minti 5

Waƙar da za a gabatar.

**<u>Waƙar Ranakun Mako</u>**

**Lahadi, Litanin, Talata, Laraba,**
**Alhamis, Jumu'a, assabar ce ƙarshe,**
**Mu je makaranta,**
**Litanin, Talata, Laraba, Alhamis, Jumu'a**
**Assabar da Lahadi, kwanakin hutawa x 2**

M 1. Rera waƙar sau biyu, tare da kwaikwayon abin da ake faɗa a cikin waƙar.

MƊ 2. Maimaita mataki na ɗaya (1) tare da ɗalibai.

Ɗ 3. Umurci ɗalibai da su rera waƙar tare da kwaikwayon abin da ake faɗa a cikin waƙar.

## Karatun Labari

minti 15

M 1. Jagoranci ɗalibai su gano sunayen abubuwan da ke cikin hoton littafinsu. A tambaye su abin da suke tsammani zai faru dangane da hotunan.

2. Rubuta labarin a kan allo.

**Ana sayar da daƙuwa a kasuwa.**
**Nana da Amina za su sayo daƙuwa.**
**Sun haɗu da fadawa a hanya.**
**Nana da Amina sun sayo daƙuwa.**
**Za su je gida su raba ɗaƙuwar.**
**Sun tafi kasuwa a kan keken Amina ne.**

3. Karanta labarin, kana/kina bi da yatsa a ƙasan kowace kalma.
4. Koya wa ɗalibai ma'anar kalmomi **[daƙuwa, fadawa, raba]** kamar yadda suka zo a cikin labarin, ta hanyar amfani da sassan jiki, ko hotuna, ko wata hanya da za su fahimta.

MƊ 5. Maimaita mataki na uku (3) tare da umurtar ɗalibai da su nuna kalmomin a cikin littafinsu yayin da suke karantawa.

6. Tambayi ɗalibai ma'anar kalmomin **[daƙuwa, fadawa, raba]**, sannan a sake yi musu bayani idan har ba su ba da amsa ba.

Ɗ 7. Umurci ɗalibai da su nuna kalmomin a cikin littafinsu yayin da suke karanta labarin a bayyane. A tabbatar suna karatun tare. Zagaya don taimaka wa ɗaliban da ke da buƙata a lokacin da suke karatun.

8. Tambayi ɗalibai ma'anar kalmomin **[daƙuwa, fadawa, raba]**.

M 9. Auna fahimtar ɗalibai dangane da labarin, ta hanyar tambayoyi.

Umurci ɗalibai da su yi tunanin labarin da aka karanto kafin su ɗaga hannu.

Mako Na 9 Darasi Na 3 da Na 4



Ana sayar da daƙuwa a kasuwa.
Nana da Amina za su sayo daƙuwa.
Sun haɗu da fadawa a hanya.
Nana da Amina sun sayo daƙuwa.
Za su je gida su raba ɗaƙuwar.
Sun tafi kasuwa a kan keken Amina ne.

69

**Tambayoyi**

1. **Me Nana da Amina za su saya?**
2. **A kan me suka tafi kasuwa?**

## Karatun Labari a Bayyane

minti 5

M 1. Karanta kan labari **[Kifayen Gado (1)]**

2. Nuna hoto idan akwai shi.
3. Tambayi ɗalibai su yi hasashen abin da suke ganin zai faru a labarin.
4. Koyar da ma'anar sabbin kalmomi **[kawayensu, kamo, laɓe]** ta hanyar amfani da sassan jiki, ko hotuna, ko wata hanya da za su fahimta.
5. Umurci ɗalibai su gano kalmomin nan a lokacin da kake/kike karanta labarin, ta hanyar ɗaga babban yatsa sama a duk lokacin da suka ji an faɗi kalmomin.
6. Karanta labarin ta yadda zai jawo hankalin ɗalibai.

*Wata mata da `ya`yanta biyu. Yaran kan tafi wasa da dare da **<u>ƙawayensu</u>**. Rannan mahaifiyarsu ta ce wa babbar, 'ina son ki fara zuwa kamun kifi, amma ba na son kowa ya sani'. Idan ƙawayenki suka zo wajenki, ki ce ba ki da lafiya. Ta koya mata waƙar da za ta yi, idan ta je rafi. Ta ce kar ta kwashe kifin duka, ta **<u>kamo</u>** daidai bukata. Sai cikin ƙawayenta, wata ta **<u>laɓe</u>**, ta bi ta, ta ga yadda take samo kifi masu yawa. Da ƙawarta ta ga yadda take samo kifaye, sai ita ma ta yi yadda ta yi.*

7. Tambayi ɗalibai su koma kan hasashensu.
8. Yi wa ɗalibai tambayoyin da ke ƙasan labarin.

**Tambayoyi**

1. **Su wa ke fita wasa da ƙawayensu da dare?**
2. **Me mahaifiyar yarinyar ke so a kamo mata?**

## Rubutu

minti 19


Jimlar da za a rubuta: **[Nana da Amina a kan keke.]**

M 1. Umurci ɗalibai daban-daban da su gano abinda ke cikin hoton da ke sashen rubutu a cikin littattafansu.

2. Ka/ki karanta jimlar **[Nana da Amina a kan keke.]**

D 3. Umurci ɗalibai da su tusa **[Nana da Amina a kan keke.]** da ke da ɗigo-ɗigo, sannan su rubuta **[Nana da Amina a kan keke.]** a filin da aka tanada a littafinsu don rubutu.

4. A duba yanayin zamansu, da yanayin riƙon fensiri da inda suke fara rubutun da kuma yadda suke rubutun.




## Aikin Gida

1. Tuna wa ɗalibai su karanta darasin yau tare da iyayensu ko 'yan'uwa ko abokai.
2. Tuna wa ɗalibai su gwada rubutun da aka yi a aji a sashen da aka tanadar don yin hakan a littafansu.

## Matashiya A Kan Darasi Na Huɗu (4)

1. Tuna wa ɗalibai cewa za a maimaita darasin da ya gabata.
2. A darasi na 2, a maimaita dukkan darasin amma a yi amfani da wannan labarin da tambayoyinsa a sashen Karatun Labari a Bayyane:

### Kifayen Gado (2)

*Bayan ƙawar ta yi yadda ta ga ta yi, sai kifaye suka fito ta kwashe gaba ɗaya don* ***hadama***. *Washegari yarinya ta dawo ta yi waka, babu kifi ko ɗaya. Ta koma gida ta sanar da mahaifiyarsu. Ta ce, 'ba komai. Duk wanda ya kwashe kifayen* ***asirinsa*** *zai* ***tonu****, saboda* ***gadon*** *iyayena ne'. Shi ke nan, ta nufi bakin rafi ta gaida rafi. Ta kuma faɗa masa damuwarta. Rafi ya ce ba komai, kifayen za su dawo. Ita kuwa ƙawarta da ta sace musu kifi. Kafin ta kai gida kifayen duk sun ruɓe yadda ba za a iya ci ba.*

***Tambayoyi***

*1. Wace ce ta kwashe kifaye gaba ɗaya?*
*2. Wane ne ya ce kifayen za su dawo?*
*3. Me ya sa kifayen da yarinyar nan ta kwaso suka ruɓe?*

# Mako Na 9 Darasi Na 5

Labarin da za a a yi amfani da shi:

**Ana sayar da daƙuwa a kasuwa.**

**Nana da Amina za su sayo daƙuwa.**

**Sun haɗu da fadawa a hanya.**

**Nana da Amina sun sayo daƙuwa.**

**Za su je gida su raba ɗaƙuwar.**

**Sun tafi kasuwa a kan keken Amina ne.**

Tambayoyin da za a yi wa ɗalibai:

1. **Me Nana da Amina za su saya?**
2. **A kan me suka tafi kasuwa?**

Jimlar da za a rubuta: ***[Nana da Amina a kan keke.]***

1. Rubuta a kan allo.

   **Ana sayar da daƙuwa a kasuwa.**

   **Nana da Amina za su sayo daƙuwa.**

   **Sun haɗu da fadawa a hanya.**

   **Nana da Amina sun sayo daƙuwa.**

   **Za su je gida raba ɗaƙuwar.**

   **Sun tafi kasuwa a kan keken Amina ne.**

2. Zaɓi ɗalibai maza da mata, a ƙalla biyar, don su karanta labarin da aka rubuta a kan allon.
3. A yi wa kowane daga cikin ɗaliban da aka zaɓa tambayoyin auna fahimtar labarin da suka karanta kafin umurtar ɗalibi/ɗaliba na/ta gaba da ya/ta karanta labarin.
   1. **Me Nana da Amina za su saya?**

   **2. A kan me suka tafi kasuwa?**
4. Rubuta ***[Nana da Amina a kan keke.]*** a kan allo.
5. Zaɓi ɗalibai maza da mata, a ƙalla biyar, don su gwada rubuta jimlar a kan allo.
6. A auna sashen da ɗaliban suka fi rauni daga gwajin da aka gabatar.
7. Yayin da aka gano wuraren da yara suke da matsala, sai a yi ɗayan waɗannan:
   - Idan ma fi yawan ɗaliban ba su zo makaranta a kwanakin dasussan ba, ko kuma ba su fahimci darussan ba, to a koyar da cikakken darasi ɗaya na wannan makon.
   - Idan kuma ma fi yawan yara suna da rauni ne a wani sashi na darasi, sai a zaɓi sashen ƙarin ƙwarewa da yake da alaƙa da wannan sashen a koyar.

# Mako Na 10

1. Za a yi wa dukkanin ɗaliban ajin gwaji.
2. Za ka/ki zauna da ɗaliban ɗaya bayan ɗaya don yin gwajin.
3. Ka/ki fara gwajin ta hanyar ba ɗalibi/ɗaliba "Takardar Gwada Ɗalibai".
4. Umurci ɗalibin/ɗalibar da ya/ta fara karantu daga "Takardar Gwada Ɗalibai" yayin da kake/kike maka abinda yake/take karantawar a "Takardar Auna Fahimtar Ɗalibai" (Za a ga kwafin wannan takardar a shafi na 55 na wannan Jagoran Malamai).
   - Idan ɗalibi/ɗaliba ya/ta faɗa daidai, sai a maka (√) harafin ko gaɓar ko kalmar.
   - Idan kuma bai faɗa daidai ba sai a jawa harafin ko gaɓar ko kalmar layi (—).
   - A zagaye harafin ko gaɓar ko kalmar da aka ja wa layi idan har ɗalibin/ɗalibar ya/ta yi wa kansa/kanta gyara ya/ta faɗa daidai.
5. Idan ɗalibi/ɗaliba bai karanta inda ya ke ba bayan daƙiƙa 3, to sai a umurce shi/ta da ya/ta wuce zuwa ga abu na gaba a "Takardar Gwada Ɗalibai".
6. A ba ɗalibai bayan "Takardar Auna Fahimtar Ɗalibai" don rubuta haruffan da za a karanto musu.
7. Maimaita mataki na biyu zuwa na huɗu (2-4) da dukkanin ɗaliban ajin.
8. A duba sashen da ɗaliban suka fi rauni daga "Takardar Auna Fahimtar Ɗalibai" na gwajin da aka gabatar.

13. Yayin da aka gano wuraren da ɗalibai suke da matsala, sai a yi ɗayan waɗannan:
   - Idan ma fi yawan ɗaliban ba su zo makaranta a makwannin da suka gabata ba, ko kuma ba su fahimci darussan ba, to a maimaita koyar da wasu daga cikin darussan makwannin da suka gabata.
   - Idan kuma ma fi yawan ɗaliban suna da rauni ne a wani sashi na darasi, sai a zaɓi sashen ƙarin ƙwarewa da yake da alaƙa da wannan sashen a koyar.

## Takardar Auna Fahimtar Ɗalibai

Adadin amsoshin da aka amsa daidai

**SunanƊalibi/Ɗaliba:**________________________________________

Sashe na 1. Haruffa

**ʻy Ky fy Gy ky ʻY ƙ ƙw**

---

Sashe na 2. Gaɓar Kalma

**kyau kyan ʻya ʻyar fyay**

---

Sashe na 3. Karatun Kalmomi

**ʻyaya kyanwa kyauta kyau ʻyarsa**

---

Sashe na 4. Karatun Labari

**Sashe na 4. Karatun Labari**
**Kaka da Nana za su je ƙauye.**
**Akwai rafi a hanyar ƙauyen.**
**Nana da Kaka sun shiga kwale-kwale.**
**Za a tsallakar da su rafi.**
**Nana na tsoron ruwa sosai.**
**Kaka ta ce ta rufe idonta.**
**Nana kuwa ta rufe idanunta.**

---

Sashe na 5. Auna Fahimta

1. **Ina su Nana za su je?**
2. **Me su ka shiga?**

---

Sashe na 6. Shifta

**ʻyarta kyauta ʻyanci ƙyale fyace**

---

**Sharhin Malami/Malama:**

# Mako Na 11 Darasi Na 1 da Na 2

## Waƙa

minti 5

Waƙar da za a gabatar.

**Waƙar Wasullan Hausa**

**A, na Aminu,**
**I, na Imamu,**
**O, sai omo,**
**U, na Ummaru,**
**Haka ne!**
**Ehhhhhh, haka ne!**

M 1. Rera waƙar sau biyu, tare da kwaikwayon abin da ake faɗa a cikin waƙar.

M'D 2. Maimaita mataki na ɗaya (1) tare da ɗalibai.

D 3. Umurci ɗalibai da su rera waƙar tare da kwaikwayon abin da ake faɗa a cikin waƙar.

## Karatun Labari

minti 15

M 1. Jagoranci ɗalibai su gano sunayen abubuwan da ke cikin hoton littafinsu. A tambaye su abin da suke tsammani zai faru dangane da hotunan.

2. Rubuta labarin a kan allo.

**Lokacin ɗari ya yi dawa ta nuna.**
**Kaka da Abba sun tafi gona da babur.**
**Kaka da Abba za su girbe dawa.**
**Za su kai dawa kasuwa.**
**Sun ɗora dawa a kan babur.**
**Sun kai dawar kasuwa sun sayar.**

3. Karanta labarin, kana/kina bi da yatsa a ƙasan kowace kalma.

4. Koya wa ɗalibai ma'anar kalmomi [ɗari, girbe, ɗora] kamar yadda suka zo a cikin labarin, ta hanyar amfani da sassan jiki, ko hotuna, ko wata hanya da za su fahimta.

M'D 5. Maimaita mataki na uku (3) tare da umurtar ɗalibai da su nuna kalmomin a cikin littafinsu yayin da suke karantawa.


6. Tambayi ɗalibai ma'anar kalmomin **[ɗari, girbe, ɗora]**, sannan a sake yi musu bayani idan har ba su ba da amsa ba.

D 7. Umurci ɗalibai da su nuna kalmomin a cikin littafinsu yayin da suke karanta labarin a bayyane. A tabbatar suna karatun tare. Zagaya don taimaka wa ɗaliban da ke da buƙata a lokacin da suke karatun.

8. Tambayi ɗalibai ma'anar kalmomin **[ɗari, girbe, ɗora]**.

M 9. Auna fahimtar ɗalibai dangane da labarin, ta hanyar tambayoyi.

Umurci ɗalibai da su yi tunanin labarin da aka karanto kafin su ɗaga hannu.


Mako Na 11 Darasi Na 1 da Na 2

Lokacin ɗari ya yi dawa ta nuna.
Kaka da Abba sun tafi gona da babur.
Kaka da Abba za su girbe dawa.
Za su kai dawa kasuwa.
Sun ɗora dawa a kan babur.
Sun kai dawar kasuwa sun sayar.

76

**Tambayoyi**

1. **Da me Kaka da Abba suka tafi gona?**
2. **Me Abba da Kaka suka girbe?**

## Karatun Labari a Bayyane

minti 5

M 1. Karanta kan labari **[Auren Kaza Da Mazuru (1)]**

2. Nuna hoto idan akwai shi.

3. Tambayi ɗalibai su yi hasashen abin da suke ganin zai faru a labarin.

4. Koyar da ma'anar sabbin kalmomi **[sirdi, yauƙi]** ta hanyar amfani da sassan jiki, ko hotuna, ko wata hanya da za su fahimta.

5. Umurci ɗalibai su gano kalmomin nan a lokacin da kake/kike karanta labarin, ta hanyar ɗaga babban yatsa sama a duk lokacin da suka ji an faɗi kalmomin.

6. Karanta labarin ta yadda zai jawo hankalin ɗalibai.

*Wata kaza ce za ta yi aure. Amma duk zakaran da ya zo, sai ta ce ba shi da gashi ko bai iya cara ba. Wasu ma don wulaƙanci sai ta ce ba su da* ***sirdi****. Ko ta ce ya yi mata tsawo, ko ba shi da kyau. Muzuru ya sami labarin kaza, da buƙatar iyayenta na su aurar da ita. Muzuru ya yo shigar manyan mutane, babbar riga da hula da rawani. Ya nufi gidan su kaza. Kaza ta fito tana* ***yauƙi****. Da ta gan shi da irin wannan shigar da ya yi ta ce lallai ta samu mijin.*

7. Tambayi ɗalibai su koma kan hasashensu.

8. Yi wa ɗalibai tambayoyin da ke ƙasan labarin.

**Tambayoyi**

1. **Wa ya sami labarin kaza?**
2. **Wane ne ya yi shigar manya?**

# Mako Na 11 Darasi Na 1 da Na 2

## Rubutu

minti 19


Jimlar da za a rubuta: **[Kaka da Abba a kan babur.]**

M 1. Umurci ɗalibai daban-daban da su gano abinda ke cikin hoton da ke sashen rubutu a cikin littattafansu.

2. Ka/ki karanta jimlar **[Kaka da Abba a kan babur.]**

D 3. Umurci ɗalibai da su tusa **[Kaka da Abba a kan babur.]** da ke da ɗigo-ɗigo, sannan su rubuta **[Kaka da Abba a kan babur.]** a filin da aka tanada a littafinsu don rubutu.

5. A duba yanayin zamansu, da yanayin riƙon fensiri da inda suke fara rubutun da kuma yadda suke rubutun.




## Aikin Gida

1. Tuna wa ɗalibai su karanta darasin yau tare da iyayensu ko 'yan'uwa ko abokai.
2. Tuna wa ɗalibai su gwada rubutun da aka yi a aji a sashen da aka tanadar don yin hakan a littafansu.

## Matashiya A Kan Darasi Na Biyu (2)

1. Tuna wa ɗalibai cewa za a maimaita darasin da ya gabata.
2. A darasi na 2, a maimaita dukkan darasin amma a yi amfani da wannan labarin da tambayoyinsa a sashen Karatun Labari a Bayyane:

### Auren Kaza Da Mazuru (2)

*Bayan kaza ta yarda za ta auri muzuru. Iyayenta sun yi **kokari** su hana ta aurenshi amma ta ki jin maganarsu. Aka ɗaura auren kaza da muzuru. Ranar da za a kai amarya, abokan muzuru na ta murna za a kawo masu nama. Da dare ya yi, `yan kawo amarya duk sun watse, sai muzuru ya shigo ɗakin amarya, ya **cabke** ta. Tun tana kuka kwayat! Kwayat! Har aka ji shiru, ya cinye ta. Ya **sulale** ya bar garin ba a kara ganinsa ba. Da a ce kaza ta ji maganar iyayenta da ba a cinye ta ba.*

***Tambayoyi***

*1. Su wa ke murna za a kawo masu nama?*
*2. Wane ne ya cafke kaza?*
*3. Da a ce kaza ta ji maganar iyayenta da me zai faru?*

# Mako Na 11 Darasi Na 3 da Na 4

## Waƙa
minti 5

Waƙar da za a gabatar.


**<u>Waƙar Wasullan Hausa</u>**

**A, na Aminu,**
**I, na Imamu,**
**O, sai omo,**
**U, na Ummaru,**
**Haka ne!**
**Ehhhhhh, haka ne!**

(M) 1. Rera waƙar sau biyu, tare da kwaikwayon abin da ake faɗa a cikin waƙar.
(MD) 2. Maimaita mataki na ɗaya (1) tare da ɗalibai.
(D) 3. Umurci ɗalibai da su rera waƙar tare da kwaikwayon abin da ake faɗa a cikin waƙar.

## Karatun Labari
minti 15

(M) 1. Jagoranci ɗalibai su gano sunayen abubuwan da ke cikin hoton littafinsu. A tambaye su abin da suke tsammani zai faru dangane da hotunan.
2. Rubuta labarin a kan allo.
**Abba da Ali sun je kasuwa.**
**Sun ga wata babbar mota.**
**Ana ta lodi a babbar mota.**
**Ana ta loda buhun gwaza.**
**Za a kai buhuhuwan gwaza wani gari.**
**Abba ya tsaya kallon babbar mota.**
**Ali ya sayo kwandon gwaiba.**
3. Karanta labarin, kana/kina bi da yatsa a ƙasan kowace kalma.
4. Koya wa ɗalibai ma'anar kalmomi **[lodi, buhuhuwa, kwando]** kamar yadda suka zo a cikin labarin, ta hanyar amfani da sassan jiki, ko hotuna, ko wata hanya da za su fahimta.
(MD) 5. Maimaita mataki na uku (3) tare da umurtar ɗalibai da su nuna kalmomin a cikin littafinsu yayin da suke karantawa.
6. Tambayi ɗalibai ma'anar kalmomin [lodi, buhuhuwa, kwando], sannan a sake yi musu bayani idan har ba su ba da amsa ba.
(D) 7. Umurci ɗalibai da su nuna kalmomin a cikin littafinsu yayin da suke karanta labarin a bayyane. A tabbatar suna karatun tare. Zagaya don taimaka wa ɗaliban da ke da buƙata a lokacin da suke karatun.
8. Tambayi ɗalibai ma'anar kalmomin **[lodi, buhuhuwa, kwando]**.
(M) 9. Auna fahimtar ɗalibai dangane da labarin, ta hanyar tambayoyi.
Umurci ɗalibai da su yi tunanin labarin da aka karanto kafin su ɗaga hannu.


Mako Na 11 Darasi Na 3 da Na 4

Abba da Ali sun je kasuwa.
Sun ga wata babbar mota.
Ana ta lodi a babbar mota.
Ana ta loda buhun gwaza.
Za a kai buhuhuwan gwaza wani gari.
Abba ya tsaya kallon babbar mota.
Ali ya sayo kwandon gwaiba.

81

**Tambayoyi**
1. **Me Abba da Ali suka gani?**
2. **Me ake lodawa a babbar mota?**

## Karatun Labari a Bayyane
minti 5

(M) 1. Karanta kan labari **[Maikuɗi da Yaronsa (1)]**
2. Nuna hoto idan akwai shi.
3. Tambayi ɗalibai su yi hasashen abin da suke ganin zai faru a labarin.
4. Koyar da ma'anar sabbin kalmomi **[kwarai, karɓi, inganci]** ta hanyar amfani da sassan jiki, ko hotuna, ko wata hanya da za su fahimta.
5. Umurci ɗalibai su gano kalmomin nan a lokacin da kake/kike karanta labarin, ta hanyar ɗaga babban yatsa sama a duk lokacin da suka ji an faɗi kalmomin.
6. Karanta labarin ta yadda zai jawo hankalin ɗalibai.
*Akwai wani maikuɗi da ke da wani yaronsa da ya amince masa **<u>kwarai</u>**. Sun dade tare komai ya sa shi yana yi masa. Sai rannan ya ba yaron kuɗi don ya gina masa gida a wani ƙauye. Yaron ya **<u>karɓi</u>** kuɗi ya tafi. Amma sai ya yi tunanin yin wani ha`inci, domin yana son wani abu daga cikin kuɗin. Saboda haka sai ya yi gini marar **<u>inganci</u>**, ya yi amfani da kaya marasa kyau. Yaron nan yana da tabbacin maikuɗin nan ba zai gane ba, kuma ba zai tambaye shi ba. Saboda ya riga ya amince masa sosai.*
7. Tambayi ɗalibai su koma kan hasashensu.
8. Yi wa ɗalibai tambayoyin da ke ƙasan labarin.

**Tambayoyi**
1. **Me Maikuɗi ya sa yaro ya yi masa?**
2. **Wane tunani yaron nan ya yi?**

# Mako Na 11 Darasi Na 3 da Na 4

## Rubutu

minti 19


Jimlar da za a rubuta: **[An loda buhuhuwan gwaza a babbar mota.]**

M 1. Umurci ɗalibai daban-daban da su gano abinda ke cikin hoton da ke sashen rubutu a cikin littattafansu.

2. Ka/ki karanta jimlar **[An loda buhuhuwan gwaza a babbar mota.]**

D 3. Umurci ɗalibai da su tusa **[An loda buhuhuwan gwaza a babbar mota.]** da ke da ɗigo-ɗigo, sannan su rubuta **[An loda buhuhuwan gwaza a babbar mota.]** a filin da aka tanada a littafinsu don rubutu.

4. A duba yanayin zamansu, da yanayin riƙon fensiri da inda suke fara rubutun da kuma yadda suke rubutun.




## Aikin Gida

1. Tuna wa ɗalibai su karanta darasin yau tare da iyayensu ko 'yan'uwa ko abokai.
2. Tuna wa ɗalibai su gwada rubutun da aka yi a aji a sashen da aka tanadar don yin hakan a littafansu.

## Matashiya A Kan Darasi Na Huɗu (4)

1. Tuna wa ɗalibai cewa za a maimaita darasin da ya gabata.
2. A darasi na 2, a maimaita dukkan darasin amma a yi amfani da wannan labarin da tambayoyinsa a sashen Karatun Labari a Bayyane:

### Maikuɗi da Yaronsa (2)

*Bayan yaron nan ya kare ginin gidan, maikuɗin nan bai tambaye shi ya aka yi ginin ba, balle ma ya je ya gani. Yaron ya yi ta **murna** don ya sami kuɗi masu yawa. Bayan an ƙare gina gida kaf, sai ya ɗauki makullai domin ya ba wa maikuɗin. Maikuɗin ya ce, 'ai dama naka ne, ina so ne in saka maka da duk **alherin** da ka yi mani. Yaro ya yi murna gaban mai kuɗi amma fa a cikin ransa ya yi ta zargin kansa da kuma **da-na-sanin** domin gidan da ya gina bai da **karko**.*

***Tambayoyi***

*1. Bayan an gama ginin wa a ka yi wa kyautar gidan?*
*2. Me ya sa Maikuɗi ya yi kyautar gidan?*
*3. Me ya sa yaron nan ya yi da-na-sani?*

# Mako Na 11 Darasi Na 5

Labarin da za a a yi amfani da shi:

**Abba da Ali sun je kasuwa.**

**Sun ga wata babbar mota.**

**Ana ta lodi a babbar mota.**

**Ana ta loda buhun gwaza.**

**Za a kai buhuhuwan gwaza wani gari.**

**Abba ya tsaya kallon babbar mota.**

**Ali ya sayo kwandon gwaiba.**

Tambayoyin da za a yi wa ɗalibai:

1. **Me Abba da Ali suka gani?**
2. **Me ake lodawa a babbar mota?**

Jimlar da za a rubuta: ***[An loda buhuhuwan gwaza a babbar mota.]***

1. Rubuta a kan allo.

   **Abba da Ali sun je kasuwa.**

   **Sun ga wata babbar mota.**

   **Ana ta lodi a babbar mota.**

   **Ana ta loda buhun gwaza.**

   **Za a kai buhuhuwan gwaza wani gari.**

   **Abba ya tsaya kallon babbar mota.**

   **Ali ya sayo kwandon gwaiba.**

2. Zaɓi ɗalibai maza da mata, a ƙalla biyar, don su karanta labarin da aka rubuta a kan allon.
3. A yi wa kowane daga cikin ɗaliban da aka zaɓa tambayoyin auna fahimtar labarin da suka karanta kafin umurtar ɗalibi/ɗaliba na/ta gaba da ya/ta karanta labarin.
   1. **Me Abba da Ali suka gani?**
   2. **Me ake lodawa a babbar mota?**
4. Rubuta ***[An loda buhuhuwan gwaza a babbar mota.]*** a kan allo.
5. Zaɓi ɗalibai maza da mata, a ƙalla biyar, don su gwada rubuta jimlar a kan allo.
6. A auna sashen da ɗaliban suka fi rauni daga gwajin da aka gabatar.
7. Yayin da aka gano wuraren da yara suke da matsala, sai a yi ɗayan waɗannan:
   - Idan ma fi yawan ɗaliban ba su zo makaranta a kwanakin dasussan ba, ko kuma ba su fahimci darussan ba, to a koyar da cikakken darasi ɗaya na wannan makon.
   - Idan kuma ma fi yawan yara suna da rauni ne a wani sashi na darasi, sai a zaɓi sashen ƙarin ƙwarewa da yake da alaƙa da wannan sashen a koyar.

## Waƙa
minti 5

Waƙar da za a gabatar.

**<u>Waƙar Gaɓar Kalma</u>**

**A, i, o, u, e!**
**A, i, o, u, e!**
**Ba bi, bo, bu, be!**
**Ba, bi, bo, bu, be!**
**Ca, ci, co, cu, ce!**
**Ca, ci, co, cu, ce!**
**Da, di, do, du, deeeee!!!**

M 1. Rera waƙar sau biyu, tare da kwaikwayon abin da ake faɗa a cikin waƙar.

MD 2. Maimaita mataki na ɗaya (1) tare da ɗalibai.

D 3. Umurci ɗalibai da su rera waƙar tare da kwaikwayon abin da ake faɗa a cikin waƙar.

## Karatun Labari
minti 15

M 1. Jagoranci ɗalibai su gano sunayen abubuwan da ke cikin hoton littafinsu. A tambaye su abin da suke tsammani zai faru dangane da hotunan.

2. Rubuta labarin a kan allo.

**Baba da Mama za su je Bausa.**
**Motar Baba ta lalace a kan hanya.**
**Baba ya kira mai gyara ya gyara.**
**Sun ci gaba da tafiyarsu.**
**Za su kai wa su Kaka ziyara.**
**Sun yi wa Kaka sayayya mai yawa.**

3. Karanta labarin, kana/kina bi da yatsa a ƙasan kowace kalma.

4. Koya wa ɗalibai ma'anar kalmomi **[lalace, gyara, ziyara]** kamar yadda suka zo a cikin labarin, ta hanyar amfani da sassan jiki, ko hotuna, ko wata hanya da za su fahimta.

MD 5. Maimaita mataki na uku (3) tare da umurtar ɗalibai da su nuna kalmomin a cikin littafinsu yayin da suke karantawa.

6. Tambayi ɗalibai ma'anar kalmomin [**lalace, gyara, ziyara**], sannan a sake yi musu bayani idan har ba su ba da amsa ba.

D 7. Umurci ɗalibai da su nuna kalmomin a cikin littafinsu yayin da suke karanta labarin a bayyane. A tabbatar suna karatun tare. Zagaya don taimaka wa ɗaliban da ke da buƙata a lokacin da suke karatun.

8. Tambayi ɗalibai ma'anar kalmomin **[lalace, gyara, ziyara]**.

M 9. Auna fahimtar ɗalibai dangane da labarin, ta hanyar tambayoyi.

Umurci ɗalibai da su yi tunanin labarin da aka karanto kafin su ɗaga hannu.

Mako Na 12 Darasi Na 1 da Na 2



Baba da Mama za su je Bausa.
Motar Baba ta lalace a kan hanya.
Baba ya kira mai gyara ya gyara.
Sun ci gaba da tafiyarsu.
Za su kai wa su Kaka ziyara.
Sun yi wa Kaka sayayya mai yawa.

86

**Tambayoyi**

1. **A cikin me su Baba da Mama suke tafiya?**
2. **Ina su Baba da Mama za su je?**

## Karatun Labari a Bayyane
minti 5

M 1. Karanta kan labari **[Tatsuniyar Wata Mayya (1)]**

2. Nuna hoto idan akwai shi.

3. Tambayi ɗalibai su yi hasashen abin da suke ganin zai faru a labarin.

4. Koyar da ma'anar sabbin kalmomi **[kitso, kirɓin, gumba]** ta hanyar amfani da sassan jiki, ko hotuna, ko wata hanya da za su fahimta.

5. Umurci ɗalibai su gano kalmomin nan a lokacin da kake/kike karanta labarin, ta hanyar ɗaga babban yatsa sama a duk lokacin da suka ji an faɗi kalmomin.

6. Karanta labarin ta yadda zai jawo hankalin ɗalibai.

*Wata rana wata yarinya ta zo* ***<u>kitso</u>****, sai ta tarar da makitsiyar tana* ***<u>kirɓin</u> <u>gumba</u>****. Sai ta jira har ta ƙare sannan suka fara kitso. Kafin su fara sai makitsiyar ta ba yarinyar gumba, sannan suka ci gaba da kitso. Can sai makitsiyar ta ce wa yarinya, 'ina gumbarki?' sai yarinya ta ce, ' ga ta nan a hannuna'. Sai makitsiyar ta ce, 'ki cinye mana'. Sai ta ce, 'to'. Amma ba ta cinye ba. Ashe ita wannan makitsiyar mayya ce, in ka je gidanta ta ba ka abu ka cinye sai ta kama ka ta cinye.*

7. Tambayi ɗalibai su koma kan hasashensu.

8. Yi wa ɗalibai tambayoyin da ke ƙasan labarin.

**Tambayoyi**

1. **Wace ce ta je kitso?**
2. **Me makitsiyar ta ba yarinya?**

## Rubutu

minti 19


Jimlar da za a rubuta: **[Motar Baba ta lalace a kan hanya.]**

M 1. Umurci ɗalibai daban-daban da su gano abinda ke cikin hoton da ke sashen rubutu a cikin littattafansu.

2. Ka/ki karanta jimlar **[Motar Baba ta lalace a kan hanya.]**

D 3. Umurci ɗalibai da su tusa **[Motar Baba ta lalace a kan hanya.]** da ke da ɗigo-ɗigo, sannan su rubuta **[Motar Baba ta lalace a kan hanya.]** a filin da aka tanada a littafinsu don rubutu.

5. A duba yanayin zamansu, da yanayin riƙon fensiri da inda suke fara rubutun da kuma yadda suke rubutun.




## Aikin Gida

1. Tuna wa ɗalibai su karanta darasin yau tare da iyayensu ko 'yan'uwa ko abokai.
2. Tuna wa ɗalibai su gwada rubutun da aka yi a aji a sashen da aka tanadar don yin hakan a littafansu.

## Matashiya A Kan Darasi Na Biyu (2)

1. Tuna wa ɗalibai cewa za a maimaita darasin da ya gabata.
2. A darasi na 2, a maimaita dukkan darasin amma a yi amfani da wannan labarin da tambayoyinsa a sashen Karatun Labari a Bayyane:

### Tatsuniyar Wata Mayya (2)

*Ita kuma wannan yarinyar da ma gidansu iyayenta sun yi mata* ***tarbiya*** *da* ***gargaɗi*** *cewa, duk ta je wani waje aka ba ta wani abu kan hanya ne ko abokin babanta ne ta amsa amma ka da ta kuskura ta ci sai ta zo gida. Ana gama mata kitso mayyar ta ce mata cikin* ***tsawa****, 'in ga hannunki' sai ta nuna mata. Tana ganin gumba sai ta amshe ta ce wa yarinya, 'Allah ya cece ki, ja`ira da kin kuskura kin ci mani gumba da na lashe ki'. Yarinya ta yi wa matar nasiha, ta tuba, ta daina cinye mutane.*

***Tambayoyi***

1. *Wace ce iyayenta suka yi mata gargaɗi?*
2. *Wace ce ta ce in ga hannunki?*
3. *Me ya sa yarinyar ta yi wa mayya nasiha?*

# Mako Na 12 Darasi Na 3 da Na 4

## Waƙa
minti 5

Waƙar da za a gabatar.

**Waƙar Gaɓar Kalma**

**A, i, o, u, e!**
**A, i, o, u, e!**
**Ba bi, bo, bu, be!**
**Ba, bi, bo, bu, be!**
**Ca, ci, co, cu, ce!**
**Ca, ci, co, cu, ce!**
**Da, di, do, du, deeeee!!!**

(M) 1. Rera waƙar sau biyu, tare da kwaikwayon abin da ake faɗa a cikin waƙar.
(MD) 2. Maimaita mataki na ɗaya (1) tare da ɗalibai.
(D) 3. Umurci ɗalibai da su rera waƙar tare da kwaikwayon abin da ake faɗa a cikin waƙar.

## Karatun Labari
minti 15

(M) 1. Jagoranci ɗalibai su gano sunayen abubuwan da ke cikin hoton littafinsu. A tambaye su abin da suke tsammani zai faru dangane da hotunan.
2. Rubuta labarin a kan allo.

**Abba da Ali sun shiga gasar ƙwallo.**
**Za a yi gasar a wani ƙauye kusa da su.**
**Abba da Ali sun yi shiri domin gasar.**
**Sun shiga mota da 'yan wasa.**
**Su Abba sun lashe gasar.**
**Gasa ta yi kyau.**

3. Karanta labarin, kana/kina bi da yatsa a ƙasan kowace kalma.
4. Koya wa ɗalibai ma'anar kalmomi **[gasa, shiri, lashe]** kamar yadda suka zo a cikin labarin, ta hanyar amfani da sassan jiki, ko hotuna, ko wata hanya da za su fahimta.
(MD) 5. Maimaita mataki na uku (3) tare da umurtar ɗalibai da su nuna kalmomin a cikin littafinsu yayin da suke karantawa.
6. Tambayi ɗalibai ma'anar kalmomin **[gasa, shiri, lashe]**, sannan a sake yi musu bayani idan har ba su ba da amsa ba.
(D) 7. Umurci ɗalibai da su nuna kalmomin a cikin littafinsu yayin da suke karanta labarin a bayyane. A tabbatar suna karatun tare. Zagaya don taimaka wa ɗaliban da ke da buƙata a lokacin da suke karatun.
8. Tambayi ɗalibai ma'anar kalmomin **[gasa, shiri, lashe]**.
(M) 9. Auna fahimtar ɗalibai dangane da labarin, ta hanyar tambayoyi.

Umurci ɗalibai da su yi tunanin labarin da aka karanto kafin su ɗaga hannu.

Mako Na 12 Darasi Na 3 da Na 4



Abba da Ali sun shiga gasar ƙwallo.
Za a yi gasar a wani ƙauye kusa da su.
Abba da Ali sun yi shiri domin gasar.
Sun shiga mota da 'yan wasa.
Su Abba sun lashe gasar.
Gasa ta yi kyau.

91

**Tambayoyi**

1. **Gasar me su Abba suka shiga?**
2. **Su wa suka lashe gasar?**

## Karatun Labari a Bayyane
minti 5

(M) 1. Karanta kan labari **[Labarin Zomo Da Dila Mai Kwaɗayi (1)]**
2. Nuna hoto idan akwai shi.
3. Tambayi ɗalibai su yi hasashen abin da suke ganin zai faru a labarin.
4. Koyar da ma'anar sabbin kalmomi **[dama, hutawa, Inuwa]** ta hanyar amfani da sassan jiki, ko hotuna, ko wata hanya da za su fahimta.
5. Umurci ɗalibai su gano kalmomin nan a lokacin da kake/kike karanta labarin, ta hanyar ɗaga babban yatsa sama a duk lokacin da suka ji an faɗi kalmomin.
6. Karanta labarin ta yadda zai jawo hankalin ɗalibai.

*Zomo da dila suka tafi farauta. Da hanya ta rabu biyu, zomo ya ce wa dila ya bi **dama**. Ni kuma in bi hagu. Dila ya ce bai yarda ba. Zomo ya yarda suka tafi. Zomo na cikin tafiya sai ya zauna gindin wata bishiya yana **hutawa**, ya ce, '**Inuwar** nan na da daɗi. Kawai ya ji an ce, 'ina ma ka ci ganyena'. Ya duba, ashe bishiyar ce ke magana. Ya tsinki ganyen ya ci, ya ji daɗi. Bishiyar ta ce, 'ina ma ka shiga cikina'. Ya ce, 'buɗe'. In ka gama, ka ce, 'kif" zan buɗe ka fita.*

7. Tambayi ɗalibai su koma kan hasashensu.
8. Yi wa ɗalibai tambayoyin da ke ƙasan labarin.

**Tambayoyi**

1. **Su wa suka tafi farauta?**
2. **Wace ce ta nemi a ci ganyenta?**

## Rubutu

⏰ minti 19


Jimlar da za a rubuta: **[‘Yan ƙwallo sun shiga mota.]**

(M) 1. Umurci ɗalibai daban-daban da su gano abinda ke cikin hoton da ke sashen rubutu a cikin littattafansu.

2. Ka/ki karanta jimlar **[‘Yan ƙwallo sun shiga mota.]**

(Ɗ) 3. Umurci ɗalibai da su tusa **[‘Yan ƙwallo sun shiga mota.]** da ke da ɗigo-ɗigo, sannan su rubuta **[‘Yan ƙwallo sun shiga mota.]** a filin da aka tanada a littafinsu don rubutu.

5. A duba yanayin zamansu, da yanayin riƙon fensiri da inda suke fara rubutun da kuma yadda suke rubutun.




## Aikin Gida

1. Tuna wa ɗalibai su karanta darasin yau tare da iyayensu ko ‘yan’uwa ko abokai.
2. Tuna wa ɗalibai su gwada rubutun da aka yi a aji a sashen da aka tanadar don yin hakan a littafansu.

## Matashiya A Kan Darasi Na Huɗu (4)

1. Tuna wa ɗalibai cewa za a maimaita darasin da ya gabata.
2. A darasi na 2, a maimaita dukkan darasin amma a yi amfani da wannan labarin da tambayoyinsa a sashen Karatun Labari a Bayyane:

### Labarin Zomo Da Dila Mai Kwaɗayi (2)

